Sarki ya hana saukar baƙo

Le roi a interdit d'héberger tout étranger

Daga/de Yazi Dogo

Mai Fasarawa/Traducteur: Hamza Abdoul Aziz

.

Taƙaitawa :
Sarki ya hana saukar baƙo, wasan kwaikwayo ne wanda a ciki Yazi Dogo yake bada labarin wani sarki da ya ɗauki matakin hana sauke baƙi, bayan ya ga sun cika haddasa matsaloli cikin masarautarsa. Wani bafade mai suna Nagudu ya saɓa, ya sauke baƙo, ya ba shi abinci da wuri kwana, amma da alƙawalin ya yi sabko ya wuce. Sai kuwa baƙon ya mutu kafin safiya ta waye. Ya ɗauki gawar ya saka cikin akwati, kamar wata dukiyar, ya kai masallaci, don wani ya gani ya ɗauka. Haka kuwa aka yi, da Ladan da Liman duk suka faɗa tarkon. Matsalar ta kai gaban Sarki. Da har ya ɗauki tsattsauran hukunci kan waɗanda ake zargi. Allah ya sa ɗan kanwarsa da yi karatun boko ya zo gaishe su. Da matashin ya ga cewa dakwai ƙura-ƙura cikin shara'ar, sai ya nemi a ba shi damar sake yin shara'ar, don gano haƙiƙanin mai laifi. Matashin ya yi bincike ta amfani da ilimin da ya koyo har ya gano cewa zumuwar da aka saka cikin furar da ya sha, ita ce ke da dafin da ya yi dalilin mutuwar wannan baƙon. Shara'ar ta birge ƴan fadar har da sarki. Ganin wannan sarki ya bada umurnin saka yaran gari su yi karatun zamani da addinin musulunci.

Résumé :
Sarki ya hana saukar baƙo est une pièce théâtrale dans laquelle Yazi Dogo raconte l'histoire d'un roi qui, excédé par la recrudescence des troubles à l'ordre publique causés par des inconnus, interdit d'héberger les étrangers sur l'ensemble de son royaume. Un notable, du nom de Nagoudou, enfreint cette interdiction et héberge un étranger, mais avec la condition de continuer son chemin très tôt le matin. Il lui donne à manger et lui donne une couchette. Mais l'étranger meurt avant le matin. Pour s'en débarrasser, il met le corps dans une cantine, faisant comme si c'était des objets de valeur et l'amène à la mosquée. Le Muezzin et l'Imam tombent dans le piège. L'affaire arrive à la cour. Le roi condamne tous les accusés à la peine capitale, sans investigation approfondie. Heureusement, le neveu du roi qui venait de terminer ses études en droit moderne est là. Voyant cela il demande l'indulgence du roi pour reprendre le jugement et trouver le vrai coupable. Il fait des investigations et découvre que c'est le miel consommé chez Nagoudou qui était infecté et a causé la mort du pauvre étranger. Ce jugement impressionne toute la cour. Réalisant l'importance et l'efficacité de ce savoir moderne, le roi ordonne qu'on inscrive tous les enfants de la cité aussi bien à l'école moderne qu'à l'école coranique.

Fadar Sarki/*A la cour du roi*

Wata safiya, fadar Sarki ta yi tsap, shirin halartar ƴan fada. Wani dogari ya tsare kujerar sarki, yayin da fadawa suke halarta ɗaya bayan ɗaya. Mutun biyu da suka riga zuwa na tattaunawa tsabkaninsu.

Un matin, la cour du roi est prête à accueillir les courtisans. Le trône est bien gardé par un garde, les notables arrivent l'un après l'autre. Les deux premiers arrivants échangent entre eux.

Nagudu : Yau Bala ka yo sabko fa fada.

Nagoudou : Aujourd'hui, Bala tu es matinal à la cour.

Bala : To, gidan ne yake mini daɗi.

Bala : C'est parce que, je suis de bonne humeur.

Nagudu : Uhum, barka, muna lafiya dai ?

Nagoudou : Uhum, bonjour, comment allez-vous ?

Bala : Muna lahiya ko ? Ba dai an tashi lafiya ba ?

Bala : Ça va ? Bien réveillé ?

Nagudu : A, lafiya lau !

Nagoudou : Ah, très bien !

Bala : To madalla. Wai ni, Turaki, lafiya ma nike ganin yana tafiya yana wani doro, yana banƙare ƙahwahuwa ?

Bala : Donc c'est bien. Mais, dis-moi pourquoi Touraki marche-t-il le dos courbé et les jambes arquées ?

Nagudu : Yanzu kai ba ka sani ba !

Nagoudou : Mais tu ne le sais pas, toi !

Bala: Wani abu ya samu?

Bala : Que s'est-il passé ?

Nagudu : Turaki nan da kaka gani, ba ma so a sani ne a fada. Ai gwaiwa gare shi ce...

Nagoudou : En fait Touraki a une hernie. Mais on ne veut pas qu'on le sache à la cour.

Bala : Uhum, a'uzu billahi ! Ashe don wannan ne yake tafiya…, sarautar nan, shi so yake yi ya samu ya ci gadonta.

Bala : Ah bon ! Que Dieu nous en préserve ! Alors, c'est la raison pour laquelle il marche… Pourtant il aspire au trône !

Nagudu : E, ai ba a son a sani ne ; gwaiwa gare shi.

Nagoudou : Effectivement, c'est que nous ne voulons pas qu'on le sache. Il a une hernie.

Turaki ya shigo biye da wani bafade. Turaki ya gyara muriya.

Turaki entre suivi d'un notable. Turaki se racle la gorge.

Bala *(ƙasa-ƙasa) :* Rage radiyo !

Bala (tout bas) : parle bas !

Nagudu : E, gaskiya na.

Nagoudou : Oui, c'est vrai.

Turaki : Yau kun yo sabko, ko ?

Touraki : Aujourd'hui vous avez été matinal, n'est-ce pas ?

Nagudu : Yo Turaki !

Nagoudou : Mais dis-donc Turaki !

Turaki: Ka san mu sha'ani da sanyi…

Touraki : Tu sais, nous, quand il fait froid…

Nagudu : E, gaskiya ne.

Nagoudou : Effectivement.

Turaki: Ba kaɓ… kai, ina kwananku!

Touraki : J'ai commis une gaf… hé, bonjour !

Nagudu da Balla : Lafiya lau !

Nagoudou et Balla : Bonjour

Turaki : Ni ba kaɓɓa ba ni yi jiya…

Touraki : Si vous savez la gaffe que j'ai commise hier…

Nagudu : Asha !

Nagoudou : Dommage !

Turaki : … Sai na kwana a waje.

Touraki : … J'ai passé la nuit dehors.

Nagudu : Lokacin bai yi ba, Turaki.

Nagoudou : Ce n'est pas encore le moment.

Turaki : Sanyi ya kama ni.

Touraki : J'ai pris froid.

Nagudu : Ɗarin nan da ya fara shiga…

Nagoudou : Ce froid qui a à peine commencé …

Bala : Um !

Bala : Oui !

Nagudu : Ai ɗarin ya fara shiga, amma bai shiga ba sosai.

Nagoudou : Le froid a certes commencé, mais il n'est pas excessif.

Turaki *(ya yi kamar bai ji ba) :* Ƙirjin nan nawa duk ya bi ya ɗaure min, wallahi, sai da anka dafa mini da tafarnuwa da man shanu, duka. Da ƙyar ni samu na futo.

Touraki (faisant semblant de n'avoir pas entendu) : J'avais la poitrine toute ankylosée, je vous assure. Il a fallu qu'on me chauffe de l'ail et du beurre. C'est difficilement que j'ai pu sortir.

Bala da Nagudu : E, e.

Bala da Nagoudou : Oui, oui.

Turaki : E, ka ji, abin ya sa, wallahi.

Touraki : Oui, c'est cela la raison, au nom d'Allah.

Wasu fadawa biyu suka yi sallama.
Deux autres notables s'annoncent par des salutations.

Fadawa biyu : Ina kwana ?

Deux notables : Comment allez-vous ?

Turaki, Nagudu da Balla : Lafiya lau.

Touraki, Nagoudou et Balla : Très bien.

Nagudu : Ai ɗarin ya fara cika, amma bai cika ba, wallahi (Nagudu ya ƙara nanatawa don ya tona wa Turaki assiri)

Nagoudou : Certes, le froid a commencé à devenir intense, mais il n'a pas atteint le sommet (Nagoudou insiste pour faire allusion à la hernie deTuraki).

Turaki : Uhum, yaya, ban gan ka ba wurin ɗaurin auren ɗan Dodo jiya ?

Touraki : Hier je ne t'ai pas vu aux cérémonies du mariage du fils de Dodo ?

Nagudu : E, na yi niyya in je, amma akwai ɗan maƙwabcina bai ji daɗi jikinshi ba jiya.

Nagoudou : Oui, j'avais l'intention d'y aller, mais il y avait le fils d'un voisin qui était souffrant.

Alamar da Dogari ɣa ɣi don gabatar da isowar Sarki fada ita ta katse wannan hirar. Kowa ɣa miƙe don girmama Sarki. Ya hau kujerarsa ɣaɣin da dogarin da ɣa rakko shi ɣake martaba shi. Sannan sauran ɣ̃an fada suka zauna tare da durƙusawa don gaida shi.

Les alertes du garde du roi annonçant l'arrivée de ce dernier au palais interrompent cette conversation. Tout le monde se lève en signe de respect au roi. Ce dernier prend place pendant que le garde du corps qui est venu avec lui fit exécuter le protocole qui accompagne sa prise de la place[1]*. Les notables se prosternent pour le saluer avant de s'assoir.*

Turaki: Allah ya baka nasara! Allah ya ja zamaninka !

Touraki : Votre Majesté ! Longue vie !

Sauran fadawa suka rinka cewa « amin » sannan suka gaida shi imma da « Ranka ya daɗe » *imma da* « Allah ya ja zamaninka » *ko kuma* « Allah ya taimake ka ». *Ana cikin haka, sai Liman da mataimakinshi, Ladan, suka shigo. Liman ɣa durƙusa gaban Sarki sannan ɣa shiga addu'ar buɗe zaman fada na wannan ranar. Dukan su suka rinka cewa «Amin » don fatan Allah ɣa karɓi addu'ar. Bayan addu'a ta ƙare sai sarki ɣa urmurci Liman da ɣa zauna a wurinshi; sannan ɣa fuskanci fada.*

Le reste des notables disent « amin » *et le saluent à leur tour tantôt par* « Longue vie » *tantôt par*, « Puisse Allah prolonger ton règne ! » ; *ou même en disant* « Puisse Allah t'aider » ! *Pendant ce temps, l'Imam et son adjoint, Ladan, font leur entrée. L'Imam s'accroupit devant le roi et commence les invocations coraniques marquant le début de la journée à la cour. Tous disent « amine » afin que l'invocation soit exhaussée. La fatia finie, le roi autorise l'Imam à s'assoir à sa place pour faire face à la cour.*

Sarki : Turaki.

Le roi : Touraki.

Turaki: Allah ya ba ka nasara!

Touraki : Votre Majesté !

Sarki : Yaya, gari ya kwan lafiya ?

Le roi : Alors, Comment va la cité ce matin ?

Turaki : Ranka ya daɗe, gari ya kwan lafiya, a unguwata.

Touraki : Votre Majesté, Tout va bien dans mon quartier.

A matsayinsa na Sarkin Fada, Turaki ɣa tattambayi sauran fadawa in garin ɣa kwan lafiya a unguwoɣinsu, kamar haka.

[1] Le notable tend son bras, la manche de son boubou avec, pour cacher l'action de s'assoir du chef. Ce protocole se fait aussi quand le chef se lève. Il faut noter que le plus souvent ce sont deux dogarai qui se chargent de ce protocole.

En sa qualité du chef des notables, Touraki s'adresse aux autres notables pour savoir si leurs quartiers se sont bien réveillés, en ces termes.

Turaki : Yaya kai, ungurwarka ta kwan lafiya ?

Touraki : Toi, est-ce que ton quartier s'est bien réveillé ?

Bala : Lafiya lau.

Bala : Très bien.

Turaki : Kai, wajenku ya kwan lafiya ?

Touraki : Et toi, ton quartier s'est-il bien reveillé ?

Bala : Lafiya limis.

Bala : Très bien.

Turaki : Kai fa ?

Touraki : Et de ton côté ?

Nagudu : Alhamdulilahi.

Nagoudou : On remercie Allah

Turaki : Kai fa Liman[2] ?

Touraki : Et de Côté l'Imam ?

Liman : Lafiya lau.

Imam : Très bien.

Turaki : Ladan, ungurwarka ta kwan lafiya ?

Touraki : Ladan, est-ce que ton quartier va bien ce matin ?

Ladan: Gari ya kwan lafiya.

Le Muezzin : La cité s'est bien réveillée.

Turaki : Ranka ya daɗe, cikin albarkarka kowa ya kwan lafiya.

Touraki : Votre Majesté, avec votre miséricorde, tout le monde s'est bien réveillé.

Sarki : Haka ne mai kyau. Abin da ya sa, na ga shegantaka ta fara yawa.

Le roi : Ça, c'est bien. C'est parce que, j'ai constaté que le banditisme est de plus en plus grandissant dans la cité.

[2] Le marabout désigné pour conduire les prières.

Duk lokacin da Sarki ya yi magana, sai Turaki ya nanatata, kamar haka :
Chaque fois que le roi parle, Touraki reprend ses propos et les commente, comme suit :

Turaki : Sarki ya ce abinda ya sa shi yin wannan tambaya, don ya ga manaƙisa da munafici da lalata sun soma yawa a garin nan.
Touraki : Le roi a dit qu'il avait posé ces questions parce qu'il avait constaté que le banditisme, l'hypocrisie et la médisance sont devenus de plus en plus courants.

Sarki : Wallahi duk wanda ya kuskura ya rabu da hanya, yana bi ta bayan gidan shi …

Le roi : Je jure sur le nom d'Allah, tout ce lui qui s'écarte du droit chemin en empruntant les voies tortueuses…

Turaki : Ya ce, wallahi, ya tashi da shi ; ya yanka shi.

Touraki : Il a juré au nom d'Allah, il va finir avec lui en lui tranchant la tête.

Sarki : Na fidda hankali… ; na fidda hankalin mutun !

Le roi : Je vais le priver de sa raison … ; je vais le détruire !

Turaki : Sarki ya ce ya fidda muku ƙwaluwa ! Wallahi ku kiyayi kanku !

Touraki : Le roi dit qu'il va vous enlever la cervelle ! Au nom d'Allah, méfiez-vous !

Zuwan Mai'unguwa ne ya katse musu hamzari. Ya durƙusa ya gaida Sarki kamar haka :
L'arrivée d'un chef du quartier les interrompe. Il s'incline et salue le roi en ces termes :

Mai'unguwa: Allah ba ka nasara.

Le chef de quartier : Gloire à sa majesté

Sauran fadawa : Amin, Mai'unguwa.

Les autres notables : Amin, chef du quartier.

Sarki : Tashi koma can zamna.

Le roi : Lève-toi et vas là-bas t'assoir.

Turaki ya yi masa faɗa, sannan ya tambayi dalilinsa na zuwa fada a makare.
Touraki le sermonne et lui demande des explications par rapport à son retard.

Turaki : Kai mai unguwa yanzu ka koyi lalata, duk safe fada sai ta cika, kai kana can kana kewaye-kewaye, kana kewaye-kewaye, ka leƙa gidan wannan ka leƙa gidan wannan ; to yanzu me ya tsaida ka ?

Touraki : Toi, chef du quartier, tu as développé de mauvaises habitudes, chaque matin la cour se rempli pendant que toi tu es quelque part, en train de trainer par-ci, par-là ; tu te rends chez celui-ci, tu vas chez celui- là. Mais dis-nous donc ce qui t'a retenu ce matin.

Mai'unguwa : Turaki da mahwari, tun a tsakar dare anka yi kururuwa unguwar tau : ɓarawo ! Munka tashi. Bin shi muke yi. Shi tsallake wannan gini ; shi faɗa nan. Cikin tsallake-tsallaken nan ya faɗa ya karye wata tsofuwa.

Le chef de quartier : Turaki, il y'a une raison. En pleine nuit, un cri d'alerte a été poussé dans mon quartier et nous a réveillé : Au voleur ! On s'y était mêlé. On s'était mis à sa poursuite. Tantôt il escaladait ce mur, tantôt il tombait par-ci, il sautait par-là. Dans cette escalade, il tomba sur une vieille et la fractura.

Turaki da sauran fadawa (hankali a tashi) : Subahanallahi, ta wannan garin ? An kuwa yi ta'asa !

Touraki et les autres notables (bouleversés) : Ce n'est pas possible, une vieille de cette cité ? C'est une catastrophe !

Turaki : Kai Sarki ya ji wannan labarin, ashe kai ba ka iya kama ɓarawo ! Kai da nika tsammani mayaƙi ne !

Turaki : Ecoute, le roi est déjà au courant de cette histoire ! Tu as été incapable d'attraper un voleur ! Toi que je prenais pour un guerrier !

Mai'unguwa : Turaki ka sani…

Le chef de quartier : Turaki, tu sais…

Turaki: Ina amfaninka! Ina amfanin zamanka a gidan nan!

Touraki : Tu ne vaux rien ! Ta présence dans cette cour est inutile !

Mai'unguwa : … halin ne…

Le chef de quartier : C'est la situation…

Turaki: Ina mazakuntar ka? Wane irin hali?

Touraki : Où est ton courage ? Quelle situation ?

Mai'unguwa : Ɓarawo nan, mu cewa muka, ba ɓarawo ba ne.

Le chef de quartier : Ce voleur-là, nous pensons qu'il n'est pas ordinaire.

Turaki : An ka ji sata a garin nan baƙo ne.

Touraki i : Dès qu'il ya vol dans ce village, c'est par un étranger

Bala: Ba a kama shi ba dai…?

Bala : On ne l'a pas encore pris… n'est-ce pas ?

Turaki : Baƙo ne.

Touraki : C'est un étranger.

Mai'unguwa: In na kama shi kuma ina zuwa war haka!

Le chef de quartier : Si je l'avais pris, je ne serais pas venu à pareil moment !

Sarki : Na ba ka doki… !

Le roi : Je t'ai donné un cheval … !

Turaki: …da takobi! Ina amfanin ka!

Touraki : … et une épée ! Tu ne vaux rien !

Sarki : Na ba ka takobi !

Le roi : Je t'ai donné une épée !

Turaki : Sarki ya ce ya ba ka doki.

Touraki : Sarki a dit qu'il t'avait donné un cheval.

Mai'unguwa: Dokin ma, Ranka ya daɗe, ana can ana….

Le chef de quartier : Même ce cheval, votre Majesté, on est entrain …

Sarki (Ya katse shi) : In ba ka doki da takobi kuma ka bari ɓarawo ya shigo gari ya dira, har wata tsofuwa ta ƙasa ta ta karye ! In sha ma Allahu, Sarkin dogarai, munafikin banza, tuɓe min shi. Daga yau ka zama talaka. Tashi daga cikin mu.

Le roi : (Il l'interrompt en ces termes) : Je t'ai donné un cheval et une épée et tu laisses un voleur opérer dans ma cité, jusqu'à fracturer une vieille de ma cité ! Par la grâce d'Allah, chef des gardes, destitue se vaut-rien hypocrite. A partir d'aujourd'hui tu n'es plus notable à la cour. Sors d'ici.

Turaki (*Ya ƙarfafa wannan hukunci na Sarki kamar haka*) : « Tuɓe[3] shi ! Fita daga cikin mu ! Ba kowa ba ne ! » Kawo shi nan (*cewa de rawanin sarauta da aka karɓe daga hannu Mai'unguwa*).

Turaki (Il appuie la décision du roi en ces termes) : « Détrône-le ! Mets-toi de côté ! Il n'est plus rien ! Amène le ici. », (faisant référence au turban, symbole de la noblesse, repris du chef de quartier).

Sarki: In ba ka doki kuma ɓarawo… (*Sarki ya ci gaba da cewa*): "Koma can baya, tare da yin alama.

Le roi : Je mets à ta disposition un cheval mais un voleur … (Le roi continue de le menacer) : Mets-toi derrière (en le lui signifiant par des gestes).
Ana nan, sai wani talaka ya shigo da wata akwati aka. Ya aje ta gaban sarki bayan da Turaki ya yi masa umurni. Ya durƙusa ya gaɣar da sarki.
En ce moment, un sujet fait son entrée avec une caisse sur la tête. Il la dépose après avoir reçu l'autorisation de la part de Turaki. Il se prosterne devant le roi pour le saluer.

[3] Destitution qui consiste à dérouler le turban de noblesse.

Turaki : Aje nan ; aje gaban sarki !

Touraki : Dépose ça ici ; dépose devant le roi !

Sarki : Sarkin dogarai, a sa wannan cikin.

Le roi : Chef des gardes, fais entrer cette caisse à l'intérieur.

Ɗan saurayi : A'a, Allah ya taimake ka, wannan sanduƙi ba na sawa gida ba ne.

Le jeune homme : Non, Votre Majesté, cette caisse n'est pas à faire entrer à l'intérieur.

Sarki : A'a, ba na sawa cikin gida ba ne, na gidanka ne !

Le roi : Mais dis-donc, ce n'est pas à faire entrer à l'intérieur, ou est-ce que tu te crois ?

Turaki : Sarki ya ce na gidanka ne !

Touraki : Sarki demande pour qui tu te prends ?

Ɗan saurayi : Ai, a ji abin da ya sa na ce hakane…

Le jeune homme : S'il vous plait, permettez- moi de m'expliquer…

Sarki ya yarda ya saurare shi.
Le chef accepte de l'écouter.

Ɗan saurayi: Jiya da dare, asuba, na ɗan fito, in gani ko an yi kiran salla. Sai na ga wannan duhu duhun, na ɗauka ko Usman bagobiri ne yake jira na.

Le jeune homme : C'était hier nuit, à l'aube, j'étais sorti voir si le muézin à fait l'appel à la prière. Là, j'ai aperçu une silhouette. J'ai pensé que c'était Ousmane Bagobiri qui m'attendait.

Turaki : Usman bagobiri fa ?

Touraki : Ousmane bagobiri ?

Ɗan saurayi : Usman bagobiri ? Usman bagobiri, shiru ?

Le jeune homme : Ousmane bagobiri ? Ousmane bagobiri ?

Fadawa : Na'am.

Les notables : Oui.

Da ya buɗa ya ga cewa kaya maras wata daraja sai ya ce : to, Allah ya baka nasara, ai ba kayan kirki ba ne a ciki, tsumma ne kawai a ciki. Amma da ya ƙara tonawa ya ga kuɗi da ba ya so ya gwadowa Sarki sai ya shiga zargin wannan talakan mai akwati.

Quand il ouvre la cantine et voit des habits de moindre valeur, il dit : bon, votre Majesté il n'y a rien d'intéressant, il n'y a que des chiffons. Mais quand il trouve une liasse de billets de

banque dont il ne veut pas montrer au roi, il se met à accuser sans fondement ce sujet qui a amené la caisse.

Turaki: Akwatin wannan an buɗa shi!

Touraki : Cette cantine a été ouverte auparavant !

Ɗan saurayi: Aradu, ba a buɗa ba.

Le jeune homme : Je jure par le tonnerre, je ne l'ai pas ouverte !

Turaki: Yanzu a gidanka, babu wanda ya ga akwatin wannan?

Touraki : Tu veux dire que chez toi personne n'a vu cette caisse ?

Ɗan saurayi : A'a, Hajiya kaɗai ta kama min na ɗora !

Le jeune homme : Non, Seule Hajiya m'a aidé à la porter sur la tête.

Turaki : Wa ya ce ka gayawa Hajiya ?

Touraki : Qui t'a dit de l'informer ?

Ɗan saurayi: A'a, wai don yana da nauyi.

Le jeune homme : Non, c'est parce que la caisse est lourde.

Turaki: Kai da ka san ba komi a ciki. (*Yana wa sarki magana*) ranka ya daɗe ba komi a cikin wanan akwatin.

Touraki : Tu sais bien qu'il n'y a rien dans la cantine. (Il s'adresse au roi) Sa Majesté il n'y a rien d'important dedans.

Ya saka kudin cikin aljihuna rigarsa ba tare da wani ya gani ba. Da yake babbar rigar ta yi masa karya. Ya ci gaba yana magana da wani dogari.
Il enfouit la somme dans la poche de son boubou comme s'il n'avait rien trouvé- son grand boubou lui servant de camouflage. Il continue en s'adressant à une garde.

Turaki : Kai, ɗauki, sa cikin gida !

Touraki : Hé, apporte ça à l'intérieur !

Dogarin ya yi abin da aka ce ya yi, ba tare de ɓata lokaci ba.
Le garde s'exécuta sans délai.

Sarki: To ji nan. (Ya amsama fadawa)

Le roi : Ecoutez bien (S'adressant au notables)

Ɗan saurayi: Allah ya ba ka nasara!

Le jeune homme : Gloire à sa majesté !

Sarki : Daga yau !

Le roi : A partir d'aujourd'hui !

Ɗan saurayi: Na ji, ranka ya daɗe.

Le jeune homme : C'est entendu, Votre Majesté.

Turaki : Sarki ya ce daga yau.

Touraki : Le roi dit que cela ne se reproduise plus.

Sarki : Ba kai ba ; makwabtan gidanku ; makwabtan kusa da kai ma, su zo su gaya mini !

Le roi : Que ce soit toi ou quelqu'un de ton voisinage, qui aurait retrouvé quelque chose, qu'il vienne m'informer !

Turaki : Sarki ya ce ; ko kazar mutane ka gani, ka zo ka gaya mai.

Touraki : Le roi dit que même si tu vois la poule de ton voisin, tu dois venir lui rendre compte !

Saurayi ya durƙusa, ya nemi gafara. Sarki ya ci gaba.
Le jeune homme se prosterne pour demander pardon. Le roi continue.

Sarki : In sha Allahu, duk wanda bai shaida min ba ya sha yuƙa !

Le roi : Plaise à Dieu, tout celui qui ne me rend pas compte, sera décapité !

Turaki : Sarki ya ce duk wanda bai nuna mishi ba abin da aka tsinta, ya sha yuƙa !

Touraki : Le roi dit que tout celui qui ne lui rend pas compte de ce qu'il aura ramassé, sera décapité !

Ɗan saurayi : (… ya faɗa, cikin tsoro) Kaina bisa wuyana ! Ban gani ba !

Le jeune homme (Il dit avec peur) C'est entendu ! Je n'ai rien ramassé !

A fusace, Sarki ya hau musu da faɗa. Ba mai kan ƙarar ba, ba fadawan ba.
Furieux, le roi se déferle sur le plaignant et ses notables.

Sarki : Kaƙa, za a yi ɓarawo ya karye min tsofuwa, kuma yanzu a kawo min akwati …

Le roi : Comment se fait-il qu'un voleur fracture une vielle de ma cité, et maintenant on m'amène une caisse…

Turaki: Hucewa, ranka ya daɗe!

Touraki Votre colère est juste, Votre Majesté !

Ran sarki ya yi matuƙar ɓaci. Fadawa suka ci gaba da ba shi haƙuri.
Le roi est très fâché. Ses notables continuent à apaiser sa colère.

Wani matsahin magidanci ya shigo tare de ƙanwarsa. Ya sunkuya gaban sarki tare da cewa : « ranka ya daɗe ». *Fadawa suka amsa kamar haka* : « yaro sannu » *tare da ba shi dama ya zauna. Ya sake durƙusawa gaban sarki sannan ya kama wuri ya zauna.*

Un jeune homme entre accompagné de sa sœur. Il s'incline devant le roi en guise de respect en prononçant « votre majesté ». Les notables lui répondent en disant : « salut jeune homme » et l'invitent à s'assoir. Il se prosterne encore devant le roi avant de prendre place.

Turaki : Samari, sarki ya ce ka maida zancenka.

Touraki : Jeune homme, le roi te demande de répéter ce que tu as dit.

Samari : Allah ba ka nasara, ƙarar wani magori ni kawo.

Le jeune homme : Votre Majesté, je suis venu me plaindre d'un guérisseur.

Sarki : (Cikin kiɗima) Kuma !

Le roi : (Désemparé) Encore !

Samari : Allah ba ka nasara, wannan dai ƙaunata ce. Ba ta lafiya. Bakinta ka ciwo. Ina neman magani ; wannan kasuwar ta shekaranjiya da ta wuce ; sai ni gamu da wannan magorin. Ya ce min yana da magani. Ya ba ni wani gari ni zo ni ba ta ; ta ƙumsa a baki. Wallahi Summa tallahi garin sai ƙara cabke mata baki.

Le jeune homme : Votre Majesté, celle- là est ma sœur. Elle a mal aux dents. Je lui cherchais du remède quand, le jour du marché dernier, j'ai rencontré un guérisseur ambulant. Il m'a dit qu'il savait soigner le mal des dents. Il m'a donné un produit que j'ai donné à ma sœur. Quand elle l'a utilisé, il a aggravé sa maladie.

Fadawa : Subahanallahi !

Les notables : Qu'Allah nous en préserve !

Samari : Haƙori uku suka zube.

Le jeune homme : Elle a perdu trois dents.

Sarki : Turaki, ka ga abinda ya sa na tambaye ka ko gari ya kwan lafiya, kuka ce, eee… Yanzu an kawo akwatin sata, an karya tsohuwa, an hudda haƙori ukku ! Ku je, ku kamo mini shi !

Le roi : Vois – tu Touraki, voilà pourquoi je t'avais demandé si le village s'était bien réveillé. Vous m'avez dit que oui. Or, voilà qu'on m'apporte une caisse volée. On me dit ensuite qu'une vielle a été fracturée. Et maintenant on a fait perdre trois dents à une fille. Allez me chercher le guérisseur !

Cikin mamaki fadawa suka tattambaya « Haƙori nawa ? », *tare da tausaya wa yarinyar. Etonnés les notables demandent* « combien de dents ? », *en témoignant leur compassion pour la jeune fille.*

Turaki : *[Ya huskanci sarki]* : Ba ƙiyawa ba aka yi. Sarki ya ce yanzu duk galgaɗin da aka yi muku, na kada ku sha ruwan tabki ba a dafa ba, ka da ku ɗauki ruwan tabki, ka ba ta baki ya taɓu. Kuna ji ana yi maku galgaɗin lahiyar jikinku ; in wa zai sha ruwan ya dafa shi. Ya bar shi ya wuni ya kwan, an ya yi sanyi ya sha, saboda tsutsocin da suke ciki. Kai ba ka ji ba ; ko ?

Touraki : [S'adressant au roi] : On n'a pas désobéi à vos instructions. Le roi dit que malgré tous les conseils pour que vous ne buviez pas l'eau des mares sans l'avoir bouillie au préalable, tu lui en a donné au point qu'elle a perdu des dents ! On vous l'a toujours dit, avant de boire l'eau des mares il faut d'abord la bouillir puis la laisser se refroidir toute une nuit avant de la consommer. Tu ne le sais donc pas ?

Turaki : *(ya wa sarki ƙusƙus a kunne) :* Allah ba ka nasara ; an ka ji magori, baƙo ne, ba ɗan garin ba ne. A nan garin babu boka, babu magori,

Touraki : (murmurant à l'oreille du roi) : Votre Majesté, un guérisseur doit être un étranger. Il n'est pas de la cité. Il n'y ni guérisseur ni charlatan dans cette cité.

Sarki: Wai ina magorin ya hito?

Le roi : Alors, d'où vient ce guérisseur ?

Turaki : Sarki ya ce daga ina magorin yake.

Touraki : Le roi demande d'où vient ce guérisseur.

Ɗan Samari : A'a, ni ban sani ba. Kasuwa na gan shi.

Le jeune homme : Je ne sais vraiment pas. C'est au marché que je l'ai rencontré.

Nagudu : Ya ce baƙo ne, Ranka ya daɗe.

Nagoudou : Il a dit que c'est un étranger, Votre Majesté

Turaki : Yana garin ?

Touraki : Est-il toujours dans la cité ?

Ɗan Samari : Iya garin.

Le jeune homme : Oui, il est là !

Turaki: Ka san inda yake?

Touraki : Tu sais où il se trouve ?

Ɗan Samari: A'a, ban san inda yake ba.

Le jeune homme : Non, je ne sais pas là où il se trouve.

Ana haka sai, aka ji wata muriya na tasowa. Nan da nan, ɗan saurayin ya gane muryar ta magorin.
Pendant ce temps, une voix se fait entendre. Tout de suite le jeune homme reconnait la voix du guérisseur.

Magori : Maganin ƙwarai sai gado ! Maganin ƙwarai sai gado ! Magani ga jikan Ladi. Ladi ta dakanta ta ba mu. Ina mai ciwon haƙori ko mai ciwon wuya ? Ina mai ciwon mura ko mai ciwon haƙarƙari ? Maganin ƙwarai sai gado. Ga magori jikan Ladi. Maganin ƙwarai sai gado ! Ladi ta dakanta ta ba mu.

Le guérisseur : Les bons médicaments viennent d'une lignée de guérisseurs ! Les bons médicaments, on les trouve chez les héritiers ! Les bons médicaments on les trouve auprès du petit fils de Ladi. C'est elle en personne qui les a pilés et nous les a donnés ! Qui souffre de mal de dents ou de mal du ventre ? Les bons médicaments, on les trouve chez les héritiers ! Voici le guérisseur, le petit fils de Ladi. Les bons médicaments, Ladi les a préparés pour nous.

Ɗan Samari : Allah ya ba ka nasara, wagga muryashi ta !

Le jeune homme : Votre Majesté, c'est sa voix du guérisseur !

Sarki : Shi na wancen ?

Le roi : C'est lui là-bas ?

Samari : E, shi ne.

Le jeune homme : Oui, c'est lui.

Sarki: Ɗan farka, kai tashi ka kawo min shi!

Le roi : Fils de pute, va me l'amener !

Turaki : Sarki ya ce tashi ka kirawo shi. Ce ana kiran shi !

Touraki : Le roi te demande de le lui amener. Va lui dire que le roi l'appelle !

Ɗan samarin ya tashi, ya je.

Le jeune se lève et se dirige vers lui.

Sarki ya fusata, ya farma fadawa.
Furieux, le roi s'en prend à ses notables.

Sarki : Anka ce min gari ya kwan lafiya !

Le roi : Vous m'avez dit que la cité s'était bien réveillée !

Turaki : Ranka ya daɗe, ba laifina ba ne. (*Ya juya ga sauran fadawa*) Kai, ban tambaye ku ba ƙasa ta kwan lafiya ?

Touraki : Votre Majesté, ce n'est pas de ma faute. (Il se tourne vers les autres notables) Hé, vous ! Ne vous ai-je pas demandé si la cité s'était bien réveillée ?

Ɗan saurayin ya dawo tare da Magorin. Ya ci gaba da wasa kanshi da kasha.
Le jeune homme revient accompagné du guérisseur qui continue à se flatter.

Magori : Ina mai tambaya ? Ina ma tambayi ga jikan Ladi ? Ga mai gadon maganin ya zo. Magani ga jikan Ladi. Ladi ta daka ta ba mu. Maganin ƙwarai sai gado. Wa ne yaro !

Le guérisseur : Qui demande ? Qui demande auprès du petit fils de Ladi ? Voici le guérisseur héritier ! Les bons médicaments se trouvent chez le petit fils de Ladi. Ladi l'a préparé pour nous. Le bon médicament se trouve chez le petit fils de Ladi. Qui peut rivaliser avec moi ?

Turaki : Kai ! Ba Ladi ba ta baka magani, ko litinin da talata da laraba da suka ba ka magani ; yau ka zo gidan magani ! Mu za ka yi ma shegantaka nan ? Ba ka san ba nan ne gidan magani ? Ya ka iso nan wuri na. Sarki yake da magani ba wani ba ! Kai kana da magani ?

Touraki : Tais-toi ! Que ton fournisseur soit Lundi, Mardi et Mercredi ; aujourd'hui, tu es venu à la source de la médecine ! Tu oses nous manquez de respect ? Ne sais-tu pas que c'est ici la source des médicaments ? Tu crois vraiment que tu as de bons médicaments ?

Magori ya matsa kusan Turaki sannan ya durƙusa.
Le guérisseur se rapproche de Turaki et s'accroupit.

Sarki : Kai, shegantaka ce ka zo ka yi min ko yaya ?

Le roi : Dis-donc, tu es venu te moquer de moi ?

Turaki : Sarki ya ce shegantaka da makirci da munafirci da lalata ka zo ka yi mai ?

Touraki : Le roi demande si tu es venu te moquer de lui ?

Sarki : Munafuki !

Le roi : Hypocrite !

Magori : Wa ni nan ! Wane ni ranka ya daɗe !

Le guérisseur : Comment oserais-je ! Comment oserais-je ! Votre Majesté !

Sarki : Wai, ka san ni ?

Le roi : D'ailleurs, est-ce que tu me connais ?

Turaki : Sarki ya ce ka sans shi ?

Touraki : Le roi te demande si tu le connais ?

Magori : Allah ya ba ka nasara, wa ne ni ?

Le guérisseur : Votre Majesté, qui suis-je pour vous manquer de respect ?

Sarki : Ka taɓa gani na ?

Le roi : M'as-tu une fois vu ?

Turaki : Ka taɓa ganin ça ?

Touraki : L'as-tu une fois vu ?

Magori : Wa ne ni ? Wa ne ni ?

Le guérisseur : Comment oserais-je ? Comment oserais-je !

Sarki : Ba ka taɓa jin labari na ba ?

Le roi : N'as-tu pas entendu parler de moi ?

Magori : Wa ne ni, ranka ya daɗe ?

Le guérisseur : Comment oserais-je, votre Majesté ?

Sarki: To in sha Allahu yau zan mu gamu mu da kai! Ɗan farka, wai kake tashi talakata ce, kake ba ta magani har haƙora ukku su zube ! Yaro maida min magani ka ji

Le roi : Plaise à Allah, aujourd'hui tu sauras qui je suis. Imbécile, tu oses donner à mon sujet un médicament qui lui fait perdre trois dents ! Petit écoutes-moi bien !

Ɗan saurayi : Allah ya ba ka nasara, shi na wanda ya ba ni magani na ba ta har haƙora ukku sunka zube.

Le jeune homme : Votre Majesté, c'est lui qui m'a vendu le médicament, qui a fait tomber trois dents de ma sœur.

Sarki : Kai boka yaya kuka yi ?

Le roi : Guérisseur, que s'est-il passé entre vous ?

Magori : Allah ba ka nasara, ni wadda muka yi. Ya ce ƙanwar shi tana da ciwon haƙori…

Le guérisseur : Votre Majesté ! Voici ce qui s'est passé : il m'a dit que sa sœur avait mal aux dents…

Matashin ya katse masa hamzari kamar haka:
Le jeune homme le contredit en disant :

Matashi : Ranka ya daɗe, ƙarya yake yi.

Le jeune homme : Votre Majesté, il ment.

Turaki ya dakatar da matashin da cewa :
Turaki arrête le jeune homme en lui disant :

Turaki : Dakata bak ka da magana.

Touraki : Attend, tu n'as pas la parole.

Magori : Ya ce ƙanwar shi tana da ciwon haƙori. Ni kau ina da magani haƙori ƙaƙa ! Magani na gadon gadon. Kakan kakana ya ba ni, na kawo, na ba shi, na ce ya nemi jal kanwa, ya nemi kaɗa ya gama da jal kanwa ; ya daka ya sa a kogon haƙorin.

Le guérisseur : Il m'a dit que sa sœur avait mal aux dents. Et moi, j'ai un médicament très efficace contre ça ! Un médicament que j'ai hérité de mes aïeux et que mon grand-père m'a transmis. Je le lui ai donné en lui précisant qu'il devait chercher du natron rouge et l'y ajouter. Puis moudre le tout ensemble et appliquer la poudre obtenue dans le creux de la dent.

Ɗan saurayi: Wallahi, summa tallahi, ba haka muka yi da shi ba!

Le jeune homme : Je vous jure, ce n'est pas comme cela que ça s'est passé !

Turaki : Dakata, an ji zancenka, an ji zancensa. Amma duk wani magani. Don kal ku ce ba a gaya muku ba. Magani a wurin sarki yake !

Touraki : Arrête, on t'a entendu, on l'a entendu, aussi. Mais vous êtes désormais prévenus que c'est le roi qui a le monopole des médicaments !

Touraki ya miƙe ya raɗa wa sarki wani abu cikin kunne.
Touraki se lève et chuchote quelques mots à l'oreille du roi.

Sarki : Sarkin dogarai, kama shi munafikin banza ka je ka bige mai haure ukku ukku so ukku. In ya so gobe ya ƙara !

Le roi : Chef des gardes, attrape cet hypocrite et va lui arracher trois dents fois trois. Qu'il récidive demain s'il veut !

Sarkin Dogarai ya yi waje da shi da ƙarfin tsiya. Magorin ya rarumi jikarsa yayin da ake cukwikuyar shi.
Le chef des gardes le tire par la force en dehors de la cour. Le guérisseur essaye de ramasser son sac posé à meme le sol.

Turaki : ɗauki ! Je ka da shi !

Touraki : Prends ! Emmène-le !

Ya juya wajen saurayin da ƙanwarsa.

Il se tourne vers le jeune homme et sa sœur.

Turaki: Kai yaro da ke yarinya, ku tashi ku je an sallame ku. Amma ƙanwarka ka kai ta likita a yi mata magani.

Touraki : Toi jeune homme et toi jeune femme, vous pouvez partir. Mais amène ta sœur au dispensaire pour la faire soigner.

Na'am, in ji saurayin yayin da yake miƙewa.
D'accord, dit le jeune homme en se levant.

Turaki: Kuma gaban nan ruwan tabki ka da ka ƙara sha in ba ka dafa ba.

Touraki : Dorénavant, il ne faut plus boire l'eau des mares sans l'avoir bouillie.

Ɗan saurayi : Na'am !

Le jeune homme : D'accord !

Turaki : Tashi ku tafi !

Touraki : Allez-y !

Sarki : Fadawa gare ku nike kap !

Le roi : Je m'adresse à vous tous, les notables !

Turaki : Ku daga yau, gaba ɗaya a gaya muku !

Touraki : Dorénavant, écoutez tous !

Sarki : Kowa ya buɗe kunneshi ya ji !

Le roi : Que chacun écoute attentivement !

Touraki : Sarki ya ce, kowa ya buɗe kunnen shi guda biyu ya shi.

Le roi : Le roi demande que chacun écoute attentivement.

Sarki : Daga yau, ba cikin garin nan ba, har cikin ƙasata ; na hana sauke baƙo !

Le roi : Dorénavant, pas seulement dans cette ville, mais dans tout le royaume ; j'interdis d'héberger un étranger !

Touraki : Daga yau, ba cikin garinshi ba, har cikin ƙasarsa ya hana sauke baƙo !

Touraki : Dorénavant, pas seulement dans cette ville, dans tout le royaume ; il a interdit d'héberger un étranger.

Sarkin dogarai ya dawo yana cewa ya cika aikin da sarki ya sa shi.
Le chef de la garde royale revient et dit avoir accompli la tâche que le roi lui a confiée.

Sarkin dogarai: An gama da shi, ranka ya daɗe!

Le chef des gardes : On a fini avec lui, Votre Majesté !

Wani bafade : Hattara … !

Un notable : Que votre volonté soit faite… !

Sarki: Duk wanda ya sauke baƙo a kan ransa! Ya sha yuƙa ko shi ko wane ne!

Le roi : Tout celui qui héberge un étranger court la peine de mort ! Il sera exécuté sans exception !

Turaki : Sarki ya ce ya hana saukar baƙo saboda tsaron ƙasa, saboda tsaron lafiyar kanmu. An da duk baƙon ya zo, an mutun ya kuskure ya sauke shi a gidansa, ya ce wallahi a kan ranshi.

Touraki : Le roi dit qu'il a interdit d'héberger un étranger pour la sécurité du royaume, pour notre sécurité. Quiconque héberge un étranger, le fera au péril de sa vie !

Fadawa : Gaskiya ne ! Gaskiya ne !

Les notables : C'est juste ! C'est juste !

Ladan : Turaki, mu ko da almajiri in ya zo unguwarmu ma zo mu gayi !

Le Muezzin : Touraki, même si c'est un talibé qui arrive dans notre quartier, nous viendrons le déclarer !

Turaki ya katse shi kamar haka : Ba almajiri ba ko baƙon malamai suka zo wajenku, to, ku zo ku shaida mana !

Touraki l'interrompt en ces termes : Même si ce sont des marabouts qui arrivent il faut t venir les déclarer !

Ladan : Ma zo ma gaya muku ! Ma zo ma gaya muku !

Le Muezzin : Nous viendrons vous les déclarer ! Nous viendrons vous les déclarer !

Sarki : Wallahi tallahi, duk wanda bai zo ya gaya mini ba, in sha ma Allahu ya sha yuƙa !

Le roi : Je vous le jure, tout celui qui ne viendra pas me prévenir sera exécuté !

Turaki : Ranka ya daɗe !

Touraki : Votre Majesté !

Fadawa : Hattara Zaki !

Les Notables : Vos désirs sont des ordres !

Turaki : Kun ji abinda sarki ya ce.

Touraki : Vous avez entendu ce que le roi a décidé.

Sarki : Turaki !

Le roi : Touraki !

Turaki: Na'am ranka ya daɗe.

Touraki: Oui, votre Majesté.

Sarki: Ka sa ɗan ƙira ya hau bisa doki, ya kewaya duk cikin garin kuma ya tai duk ƙasata kowane gari inda ni ke iko, duk wanda ya sauke baƙo a kan ransa.

Le roi : Instruit le crieur public pour qu'il monte à cheval et qu'il passe dans toute la cité et ensuite dans tous les villages du royaume pour transmettre ce message.

Turaki : Sarki ya ce a shaida muku kowa ya koma cikin ƙasa ya faɗi daga yau an hana saukar baƙo !

Touraki : Le roi ordonne à chacun de retourner dans son village pour informer les populations que personne ne doit héberge un étranger !

Sarki : Kuma na gaya muku !

Le roi : Vous êtes aussi informés !

Turaki: Duk wanda ya kuskure ya sauke baƙo…

Touraki : Tout celui qui se hasarde à héberger un étranger…

Sarki: A kan ransa! Ya sha yuƙa ko wane ne!

Le roi : Tout contrevenant sera décapité, sans exception !

Turaki: Sarki ya ce, a kan ransa. In kunne ya ji, jiki ya tsira!

Touraki : Le roi a dit que tout contrevenant sera exécuté. Un homme averti en vaut deux !

Sarki ya tashi. A nan ma sarkin dogarai ya miƙe don kara wa sarki labule yayin da yake tashi. Abin da ya kawo ƙarshen wannan dogon zaman na Fadar. Fadawa suka bi sarki da "tashi lafiya, Ranka ya daɗe!".
Le roi se lève. Le chef de la garde royale se leve en même temps que lui, en cachant avec une manche de son boubou les mouvements du roi. Debout, les notables disent à l'unisson : « Au revoir, Votre Majesté ! »

Turaki: In kunne ya ji jiki ya tsira. (*Turaki ya ƙarƙare da cewa, yayin da yake ɗaukar rawanin Mai'unguwa da aka tuɓe. Suka fita).*

Touraki : Un homme averti en vaut deux (*rappelle Touraki en ramassant le turban du chef de quartier destitué, avant de quitter la cour.)*

Gidan Nagudu

Chez Nagoudou

A can gidan Nagudu, matarsa Rabi ta yi tagumi ta ƙosa mijinta har wannan lokaci bai zo gida ba. Ta fara magana ita kaƈai.
Chez le notable Nagoudou, son épouse Rabi, la main contre la joue, est inquiète du retard inhabituel de son époux. Elle monologue.

Rabi : Ni yau, ko lafiya ma mai gida ya daƈe bau zo ba ?

Rabi : Qu'est-ce qui se passe aujourd'hui ? Mon époux n'est toujours pas rentré !

Bayan haka kaƈan Nagudu ya shigo a gajiye.
Peu après Nagoudou entre fatigué.

Nagudu: Kai… Yo, ana nan zaune?

Nagoudou : Ah… tu es assise à m'attendre ?

Rabi : Ga ni zamne, yanzu ni ƙare cewa ko lafiya ?

Rabi : Je suis là assise, je me demandais pourquoi tu n'étais pas encore à la maison.

Nagudu : Lafiya.

Nagoudou : Rien de grave.

Rabi : Sannu da zuwa !

Rabi : Bonne arrivée !

Nagudu : Yawwa sannu !

Nagoudou : Merci !

Ya zauna kan tabarma kusa ga matarsa tare da cewa « bismillahi ».
Il s'assoit sur une natte à côté de sa femme en disant « Bismillahi » (Au nom d'Allah).

Rabi : Yau kun daƈe fada !

Rabi : Aujourd'hui tu es resté tard à la cour !

Nagudu : Tillas mu daƈe fada mana !

Nagoudou : On y était obligé !

Rabi : Lafia ?

Rabi : Pourquoi ?

Nagudu : Yau ban taɓa ba … Yau fa fada lalacewa ta yi.

Nagoudou : Aujourd'hui c'était … Un jour macabre à la cour.

Rabi : Assha ! Assha !

Rabi : Que Dieu nous en garde ! Que Dieu nous en garde !

Nagudu : Unm, ran Sarki ya ɓace.

Nagoudou : Ah oui, le roi était fâché.

Rabi : Assha ! Assha !

Rabi : Que Dieu nous en garde ! Que Dieu nous en garde !

Nagudu : Yau fada ba daƈi !

Nagoudou : Aujourd'hui, la cour était dans tous ses états.

Rabi : To !

Rabi : Mais pourquoi ?

Nagudu: Yo, ke kin ga Turaki!

Nagoudou : Il fallait voir Touraki !

Rabi : Um… ?

Rabi : Quoi… ?

Nagudu : Turaki idon sun yi ja, faƈa ya kai kamar ya ci mu ƈanye !

Nagoudou : Les yeux de Touraki étaient devenus rouges, comme s'il voulait nous manger vifs !

Rabi : Assha ! Mi anka yi mai gida ?

Rabi : Que Dieu nous en garde ! Qu'est-ce qui a pu se passer ?

Nagudu : Garin ne yanzu ake nan ana abubuwa iri-iri.

Nagoudou : Il se produit de choses dans la cité !

Rabi : Subahanallahi !

Rabi : Que Dieu nous en garde !

Nagudu : Abubuwa da ba su da kyau.

Nagoudou : Des pratiques déplorables.

Rabi : Assha ! Assha !

Rabi : Que Dieu nous en garde ! Que Dieu nous en garde !

Nagudu : Abin nan ya ɓata ma sarki rai. To sarki ya tara mu mu duka. Ai inda kin saurara kin ji an yi gangami. Ana cewa Sarki ya ce kar kowa ya yada ya sauke baƙo.

Nagoudou : Cela a mis le roi en colère. Alors ce dernier nous a réuni tous. Si tu avais prêté attention, tu aurais pu entendre le crieur public annoncer un message du roi qui interdit d'héberger un étranger.

Rabi : I, na ji gangamin amma ban san ko mine ne ba.

Rabi : Oui, j'ai entendu un crieur public, mais je n'ai pas pu comprendre le message.

Nagudu: E to, zancen kenan. Garin ne da yanzu ana abubuwan da ba su da kyau. Abin da za ɓata ma sarki rai ; shi kuma ya tara mu, ya ɗauki matakai, ya ɗauki doka.

Nagoudou : Oui, c'était cela. Il se passe dans la cité des choses qui ne sont pas bien. Cela n'a pas plu au roi. Il nous a alors réuni et a pris une des mesures, sous formes d'interdiction royale.

Rabi : Subahanallahi !

Rabi : Que Dieu nous en garde !

Nagudu : Sarki cewa ya yi daga yau, kak kowa ya yadda ya sauke mishi baƙo ; ko wane iri na.

Nagoudou : Le roi a dit qu'à partir d'aujourd'hui, personne ne doit héberger un étranger, sans exception !

Rabi : Assha, Maigida !

Rabi : Que Dieu nous en garde, mon mari !

Nagudu : Wallai !

Nagoudou : Je te le jure !

Rabi : Yanzu baƙo duk da naka na, ba ka da ikon ka sabkad da shi ?

Rabi : Désormais on ne pourra plus héberger un étranger, même un parent ?

Nagudu : Baƙo naka ? Sarki na magana kuma baƙo zai zama naka ?

Nagoudou : Ton propre étranger ? Comment un notable peut-il héberger un étranger alors que le roi l'a déjà interdit ?

Rabi : Wallahi ko, Lalle sarki…

Rabi : C'est impossible ? C'est vrai le roi …

Nagudu : To, kin ji abinda sarki ya ce.

Nagoudou : En tout cas, c'est ce que le roi a décrété.

Rabi : Babbar magana !

Rabi : C'est plus fort que nous !

Nagudu : E, babbar magana ce.

Nagoudou : Effectivement, c'est plus fort que nous.

Rabi : In kunne ya ji, ai jiki ya tsira, ko !

Rabi : Un homme averti en vaut deux ! N'est-ce pas ?

Nagudu : A'a, jiki tsira yakai. Amma kamar ku, da yake ba ma nan wani bi, da an zo, an sallama, « ah, to zamna har maigida ya zo », ku sauke muna mutane tun ba mu zo munka gani ba.

Nagoudou : Les gens s'en accommoderont. Mais c'est vous qu'on redoute, vous qui pouvez, en notre absence, héberger des étrangers avant qu'on arrive pour donner notre avis.

Rabi: Yanzu in an yi baƙo, ya sallamo mu…

Rabi : Si maintenant nous avons un étranger qui se présente …

Nagudu : To daga yau. Daga yau, ni na gaya miki.

Nagoudou : Dorénavant, plus jamais cela. Je t'ai averti.

Rabi : Ka san baƙo alheri na, wani baƙo fa.

Rabi : Tu sais que certains étrangers portent bonheur

Nagudu: To, an san da hakanan, amma dai tun da sarki ya ya riga ya ɗauki wannan dokan ba mu warware ta.

Nagoudou : Oui, j'en suis conscient, mais comme le roi a déjà décidé autrement, je n'y peux rien.

Rabi: To…

Rabi: D'accord…

Nagudu: Ba mu warwareta.

Nagoudou : Nous n'irons pas à l'encontre de cette décision.

Rabi: to…

Rabi: D'accord…

Nagudu: Da ma ke ta ad da wani karanbaninki. In ban na nan kada ki yadda ki sauke min baƙo. Ko wane iri ne !

Nagoudou : C'est toi qui es souvent capricieuse. Pendant mon absence, il ne faut pas héberger des étrangers, quelque soient nos rapports avec eux.

Rabi : Ai shi kenan magana ta ƙare.

Rabi : Ne t'en fait pas, j'ai bien compris

Nagudu: Haba Gaskiyar sarki. Gari ake nan abubuwa. Ka ji an ce an yi kaza wannan anguwar; can waccan wajen ka ji an ce an yi kaza; an yi kaza, abin ya ɓata mini rai!

Nagoudou : Le roi a vraiment raison. Dans cette cité, il y a des pratiques abominables. On entend que telle chose s'est produite dans tel ou tel quartier. C'est vraiment malheureux.

Kwatsam, suka ji sallama bakin ƙofa.
Soudain, un étranger s'annonce à la porte.

Baƙo: Salama alaikum! Salama alaikum!

L'étranger : Que la paix soit avec vous ! Que la paix soit avec vous !

Suka yi tsit na wani ɗan lokaci. Nagudu ya umurci matarsa da ce wa baƙon ya wuce.
Ils se taisent pendant un instant. Nagoudou ordonne à son épouse de faire partir l'étranger.

Nagudu : Kai wanga abu na mutane ! Dan Allah tashi tai ko wane ne, ce masa ba kowa gidan !

Nagoudou : Vraiment les gens sont compliqués ! S'il te plait, vas lui dire que ton mari a voyagé, quelle que soit sa provenance.

Ya ci gaba da magana shi kaɗai.
Il continue son monologue.

Nagudu : Kamar da gamgam an ce kar yadda a sauke … ka zo dare ya raba, ka zo kana yi ma mutane salama alaikum ! Kai, sha'anin mutanen yau dai, ga shi ga kamarshi !

Nagoudou : Comme pour nous tester contre l'interdiction royale, voilà un étranger qui arrive en milieu de nuit et demande à être héberger ! Ah, l'homme d'aujourd'hui est insupportable !

Rabi : Baƙo ne.

Rabi : C'est un étranger.

Nagudu : Aaa ?

Nagoudou : Quoi ?

Rabi : Baƙo.

Rabi : Un étranger.

Nagudu : Je ki ce mishi ba kowa a gidan.

Nagoudou : Vas lui dire que ton mari a voyagé.

Rabi : Haba maigida yaya in ce mishi, ba kowa ?

Rabi : S'il te plait mon mari, comment pourrais-je lui dire que tu es absent ?

Nagudu : Mi ni gaya miki yanzu ?

Nagoudou : Qu'est-ce que je t'ai dit tout à l'heure ?

Rabi : Sai ka bari…

Rabi : Mais tu attends…

Nagudu : Ba zancen da muke yi ba kenan, yanzu ?

Nagoudou : Ce n'est pas de tes caprices que je parlais tout à l'heure ?

Rabi: … Ka ji abin da ya kawo shi. Ka sani ko mai wucewa ne ?

Rabi : … Ecoute ses doléances. Il se peut qu'il soit juste de passage.

Matar ta ci gaba da yi masa magiya.
La femme continue à le supplier.

Nagudu : Ba dai baƙo ba ne ; to, ya yi ta tahiya mana !

Nagoudou : C'est un étranger, n'est-ce pas ? Alors qu'il continue !

Rabi : Yi hanƙuri, maigida. Ka ji abinda ya kawo shi.

Rabi : Soit sensible, mon mari. Ecoutez- le pour savoir ce qui l'a amené

Nagudu : Ke… Ke diba… !

Nagoudou : Toi… Laisses-moi tranquille !

Rabi : Yi hanƙuri maigida.

Rabi : S'il te plait, mon mari.

Nagudu : Yanzu ni ƙare yi miki zancen.

Nagoudou : Je viens tout juste de t'en parler, non ?

Rabi : Yi hanƙuri maigida. Baƙo, wani baƙo gida, alheri na

Rabi : S'il te plait, mon mari. Certains étrangers portent bonheur.

Nagudu : Asshe ? To, ce ya shigo mu ga ko ƙaƙa take.

Nagoudou : Vraiment ? Bon comme tu insistes, qu'il entre, on va voir.

Matar ta koma waje don ta shigo da baƙon. Kafin matar ta dawo ya ci gaba da magana shi kaƈai kamar haka :
La femme retourne à la porte pour faire entrer l'étranger. Avant qu'elle ne revienne Nagoudou continue à monologuer en ces termes :

Nagudu : Kai, sha'anin dai da mata ; ke yanzu, in ƙare miki zancen kada a sauke baƙo ; ba ki ce mishi shi yi ta tafiya.

Nagoudou : Ah, les femmes ; je viens juste de lui faire part de la décision du roi ; elle refuse de lui dire de continuer son chemin

Matar da baƙon sun shigo. Ya yi sallama kamar haka:
La femme revient avec l'étranger qui s'annonce par :

Baƙo : Salama alaikum !

L'étranger : Que la paix soit avec vous !

Nagudu : amin !

Nagoudou : Amen !

Boƙon ya aje sakonshi tare da ci gaba da gaisawa da maigida.
L'étranger dépose son sac en continuant à saluer son hôte.

Baƙo : Maigida, muna lafiya ?

L'étranger : Comment ça va monsieur !

Nagudu : Lafiya lau.

Nagoudou : Je vais bien.

Baƙo : Barka dai !

L'étranger : Salut !

Nagudu : lafiya lau.

Nagoudou : Bien.

Ci gaba da gaisawa.
Les salutations continuent.

Nagudu : Yo, baƙo !

Nagoudou : Alors Etranger !

Baƙo : Na'am.

L'étranger : Oui.

Nagudu : Daga ina ka fito ?

Nagoudou : D'où viens-tu ?

Baƙo : Daga Dingas.

L'étranger : Je viens de Dingas.

Nagudu : Za ka ina ?

Nagoudou : Tu vas où ?

Baƙo : Kuma za ni Washa.

L'étranger : En suite je vais à Wacha.

Nagudu : Washa ?

Nagoudou : Wacha ?

Baƙo : Uhum.

L'étranger : Oui.

Nagudu : To, yanzu abinda za a yi.

Nagoudou : Bon, maintenant ce qu'on va faire …

Baƙo : Uhum.

L'étranger : Uhum.

Nagudu : Tashi za ka yi, ka yi niyya, ka je ka.

Nagoudou : Tu vas te remettre en route.

Baƙo: Haba maigida, yi hankuri mana.

L'étranger : S'il te plait, laisse-moi passer la nuit.

Nagudu : In yi hanƙuri ?

Nagoudou : Que je te laisse passer la nuit ?

Baƙo: Ya yi dare fa…! (Ana *gane ba bahaushe ba ne.)*

L'étranger : Il fait nuit… ! (Son accent n'est pas local)

Nagudu : Kai diba !

Nagoudou : Hei, écoute-moi !

Baƙo : Maigida yi hankuri.

L'étranger : S'il te plait monsieur.

Nagudu: Yo ai ka san daren ya yi!

Nagoudou : Tu savais bien qu'il faisait nuit !

Baƙo: Yo, haniyar babu kyau. Hanya akwai wani buldu; akwai wani…!

L'étranger : Vraiment la route est dangereuse. Il ya des dangers comme bouldou, comme… !

Nagudu : Ba buldu ba ; ko buludda. Ba buldu ba ; ko buludda…

Nagoudou : Que diable avec ton bouldou, ton je ne sais quoi…

Baƙo : Maigida… ?

L'étranger : S'il te plait … ?

Nagudu : … Tafiya za ka yi !

Nagoudou : Tu vas partir !

Baƙo : Maigida na roke ka.

L'étranger : Je t'en supplie, monsieur.

Nagudu : Ka roƙan mi ?

Nagoudou : Pourquoi me supplier ?

Baƙo : Maigida, yi hankuri.

L'étranger : Je t'en supplie, monsieur.

Nagudu : Kai, a'a !

Nagoudou : Non, Jamais !

Baƙo : Maigida, dare guda !

L'étranger : Monsieur, une seule nuit !

Nagudu : Kai a'a. Kar ka yi min wannan zancen !

Nagoudou : Non, jamais ! Ne me force pas !

Matar Nagudu ta kama ma baƙo don gamsar da maigidanta don ya sauke shi.

L'épouse de Nagoudou appuie l'étranger pour persuader son mari à l'héberger.

Rabi : Haba maigida !

Rabi : Calme-toi chéri !

Nagudu : Ke, ba ta da, haba maigida !

Nagoudou : Toi, ne m'en supplie pas !

Rabi : Yi hanƙuri, tunda dai…

Rabi : Ne te fâche pas, puisse que …

Baƙo : Yi hankuri.

L'étranger : Ecoute ta femme.

Nagudu : Kai !

Nagoudou : Toi, fais attention !

Rabi : Yi hanƙuri, Sai ya yi sabko ya tafiya tai maigida.

Rabi : Donne-lui une chance. Il va se lever très tôt le matin pour continuer son chemin.

Suka samu suka gamsar da shi. Ya yarda ya sauke Boƙon amma da sharaɗin zai wuce tun da asuba.
L'épouse et l'étranger ont réussi à dissuader Nagoudou. Il accepte d'héberger l'étranger mais à condition qu'il quitte dès l'aube.

Baƙo : Yawwa haka ne maigida, tun safe bai yi bai na tashi.

L'étranger : Très bien, monsieur, très tôt le matin, je continue.

Nagudu : Kai ban yarda ba !

Nagoudou : Non, je reviens sur ma décision !

Rabi : Don sarki ya hana saukar baƙo !

Rabi : Parce que le roi a interdit d'héberger un étranger … !

Nagudu : Ni ban yarda da wannan sabkon ba. Ni ban yarda in saɓa ma umurnin sarki ba.

Nagoudou : Je ne suis pas d'accord qu'il quitte très tôt. Je ne veux pas aller contre la décision du roi.

Rabi : Kai maigida, tare da shi muke nan ?

Rabi : Mon chéri, est-ce que le roi est avec nous ici ?

Baƙo : Haka ne.

L'étranger : Elle a raison.

Nagudu ya yi shiru, yana tunani. Matar ta ci gaba da ƙoƙarin ganin ya sabke baƙon. Nagoudou reste silencieux, il réfléchit. Son épouse continue à plaider en faveur de l'étranger.

Rabi: Ai, ba tare da shi muke nan ga ba. Kuma dare na. Babu mai motsi. Ko kaza ba ta motsi.

Rabi : Nous ne sommes pas avec le roi ici. Et puis il fait nuit. Rien ne bouge. Même les poules ne bougent pas.

Nagudu : Ya yi sabko… ?

Nagoudou : Il va se lever très tôt… ?

Rabi : Ka bari sai ya yi sabko ya tafi, ko ?

Rabi : Tu acceptes de l'héberger mais il va quitter très tôt, n'est-ce pas ?

Baƙo: Yi hankuri maigida. Yi hankuri.

L'étranger : Accorde-moi cette faveur, monsieur, s'il te plait.

Nagudu : To, Diba baƙo…

Nagoudou : Bon, écoute-moi étranger…

Baƙo : Uhum !

L'étranger : Uhum !

Nagudu : E… Uwargida ta ƙare zance.

Nagoudou : Ma femme a tranché.

Baƙo : Yawwa ! Yawwa !

L'étranger : Bien ! Bien !

Nagudu : Tunda ta riga ta sa bakinta.

Nagoudou : Comme elle a intercédé.

Baƙo : Uhum…

L'étranger : Uhum…

Rabi : Ni dai haka nan na ni gani.

Rabi : En tout cas, c'est ce que moi je vois.

Nagudu : Tunda dai sabko za ka yi, ka tafi…

Nagoudou : Puisque tu vas te lever très tôt le matin pour partir …

Baƙo: E, da asuba luk zan tafi.

L'étranger : Sans problème, je quitterai dès l'aube.

Nagudu : Yanzu wannan alfarmar yi ma ita za mu yi.

Nagoudou : Bon, nous allons t'accorder cette faveur.

Baƙo: Yawwa! Yawwa, na gode Wallai! Na gode !

L'étranger : C'est bien, c'est bien. Merci vraiment ! Merci !

Nagudu : …Ka yi sabko ka tafiyarka.

Nagoudou : … Tu dois quitter très tôt le matin.

Baƙo : Na gode.

L'étranger : Merci.

Nagudu : Don abin da ya sa baƙo…

Nagoudou : La raison est que …

Baƙo : Uhum ?

L'étranger : Uhum ?

Nagudu : … Doka ce ka iske sarki ya sa.

Nagoudou : … Tu es arrivé après une décision du roi qui interdit d'héberger un étranger.

Baƙo : Yo !

L'étranger : Ah bon !

Nagudu : Gari ya rikice.

Nagoudou : La cité fait face à des problèmes.

Baƙo. Haka fa. Haka fa.

L'étranger: D'accord; d'accord.

Nagudu: Amma yanzu da yake tsakaninmu ne …

Nagoudou : Mais maintenant c'est entre nous….

Baƙo : E, haka ne.

L'étranger : Oui, c'est d'accord.

Nagudu: … Zan bari ka kwanta…

Nagoudou : … Je te laisse te coucher…

Baƙo : Haka ne.

L'étranger : C'est cela.

Nagudu : … Kuma tun sassafiyar fari.

Nagoudou : … Et très tôt le matin.

Baƙo : Uhum.

L'étranger : Uhum.

Nagudu : Ka yi sabko ka tafi.

Nagoudou : Tu te réveilles très tôt pour partir.

Baƙo: Ina tafiya; ina tafiya.

L'étranger : … Sans problème, je quitterai comme prévu.

Rabi : Bari in ɗauko mai tabarma.

Rabi : Je lui apporte une natte.

Nagudu : E, ɗauko mishi tabarma.

Nagoudou : Oui, apporte-lui une natte.

Baƙo : Wuuu ! …

L'étranger : Wuuu !…

Nagudu : …Garin ne baƙo, ai ba ƙiyawa aka yi ba.

Nagoudou : … C'est à cause de la situation de la cité. Ce n'est pas parce qu'on ne veut pas t'héberger.

Daga ƙarshe Nagudu amince. Sai matar ta kawo ma baƙo tabarma. Ta kawo cikin sauri yayin da Nagudu ya ci gaba da bayar da dalilan ƙin yardar shi.
Finalement Nagoudou accepte d'héberger l'étranger. Son épouse amène une natte à ce dernier pendant que son mari continue à justifier son refus initial.

Baƙo : Gari da doka, ai babu lafiya !

L'étranger : Une interdiction signifie qu'il y des problèmes !

Nagudu : Sarki ya ɗauki doka.

Nagoudou : Le roi a pris cette décision.

Baƙo : Wallai na gode.

L'étranger : Merci, beaucoup.

Nagudu: Mu kuwa ba mu so mu tada dokar sarki.

Nagoudou : Nous n'avons pas voulu aller à l'encontre de la décision royale.

Baƙo: Uhum, haka nan na. Haka nan na.

L'étranger : Uhum, c'est normal. C'est normal.

Nagudu : Amma sabko.

Nagoudou : Mais il faudra partir très tôt.

Baƙo : Uhum….

L'étranger : Uhum….

Nagudu : Da zakara ya yi kuka, ka yi niyya ka tafi.

Nagoudou : Dès le premier chant du coq, tu dois partir.

Baƙo: Uhum... tun ba yi kuka ba na tafi.

L'étranger : Uhum… je quitterai avant le chant du coq.

Nagudu : E.

Nagoudou : D'accord.

Baƙo : Wallai na gode.

L'étranger : Merci beaucoup.

Nagudu yana nunama matarshi inda za ta shimfiɗa ma baƙon tabarma.
Nagoudou indique à sa femme l'endroit où elle va placer la natte pour l'étranger.

Nagudu : E, Shimfiɗa mishi ita nan.

Nagoudou : Il faut la lui étaler ici.

Ta shimfiɗa tabarma, amma ba yadda shi Nagudu yake ganin ya kamata ba. Ya ci gaba da nuna mata yadda za ta yi, kamar haha :

Elle étale la natte, mais pas comme son mari le lui a indiqué. Ce dernier continue à lui donner des directives, comme suit :

Nagudu : Gyara mishi haka. A'a, yi na haka da ita.

Nagoudou : Arrange-la comme ça. Non, tire de l'autre côté.

Bayan hakan sai baƙon ya samu wuri ya zauna kan shimfiɗa.
La natte étant étalée, l'étranger y prend place

Nagudu : Ah, to baƙo.

Nagoudou : La natte est prête, étranger.

Baƙo : Na'am.

L'étranger : Je vois.

Nagudu : Bisimilla !

Nagoudou : Prends place !

Baƙo: E, yawwa, yawwa! Na gode wallahi!

L'étranger : D'accord, d'accord ! Merci beaucoup !

Nagudu : Umm, ke diba ɗauko tuwo kawo mishi.

Nagoudou : Uhum, apporte-lui à du Touwo.

Rabi : Ai, babu tuwo ; sai dai fura.

Rabi : Il n'y a pas de Touwo, mais il y a du foura.

Nagudu : A ?

Nagoudou : Comment ?

Rabi : Sai dai hura ; kuma hurar ba nono.

Rabi : Il n'y a que du foura sans lait.

Nagudu ya yi shiru na wani ɗan lokaci. Can sai ya tuno da wata ɣar zuma da ya sayo kwanan nan.
Nagoudou reste silencieux un instant. Puis il se souvient du miel qu'il a acheté il n'y a pas longtemps.

Nagudu : Ba akwai zumuwar nan da na sayo kwanankin baya ba ?

Nagoudou : Ne reste-il pas du miel que j'ai acheté il n'y a pas longtemps ?

Rabi : I, tana nan.

Rabi : Oui, il en reste

Nagudu : Yawwa. To ɗibi ɣad daidai ki sa ciki, ki gurmaza ki bashi.

Nagoudou : C'est bien alors. Prends-en un peu, dilue-le dans le foura et donne-le-lui.

Rabi : To

Rabi : D'accord.

Sai ta shiga aiki.
Elle entre dans une chambre.

Nagudu: E, dama, kawo mishi.

Nagoudou : Bien. Tu le prépares et tu le lui donnes.

Ta kawo mai hurar. Yayin da ya ke sha Nagudu ya matso kusa da shi.
Elle lui amène le foura. Pendant qu'il la boit Nagoudou s'approche de lui.

Nagudu : Baƙo !

Nagoudou : Etranger !

Baƙo : Na'am !

L'étranger : Oui !

Nagudu : Bari dai in ƙara zawwa kusa gare ka…

Nagoudou : C'est mieux que je m'approche plus près de toi …

Ya tsugunna kusa da baƙonsa don ya ji daɗi magana da shi cikin sirri.
Il s'accroupit à côté de son étranger, afin qu'il puisse lui parler en toute discrétion.

Baƙo : Yawwa ; Yawwa !

L'étranger : Bien, bien !

Nagudu : Sabada… Ko ba gaskiya ba ?

Nagoudou : Parce que… tu me comprends vraiment ?

Baƙo : E !

L'étranger : Oui !

Nagudu : Don kada ka ce wai na yi ƙuraragi.

Nagoudou : Pour que tu ne penses pas que je ne veux pas que tu passes la nuit ici.

Baƙo : Uhum !

L'étranger : D'accord !

Nagudu : Ka ji dai na gaya ma, sarki na ya yi doka.

Nagoudou : Je t'ai informé qu'il s'agissait d'une interdiction du roi.

Baƙo : Uhum, ba laifi.

L'étranger : Uhum, ce n'est pas grave.

Nagudu: Kuma ina roƙon ka; don Allah don Annabi ka yi sabko.

Nagoudou : Alors je t'implore de quitter très tôt le matin.

Baƙo : Uhum.

L'étranger : Uhum.

Nagudu : Ka yi sabko.

Nagoudou : Quitte très tôt.

Baƙo : Da safiya lib ina tafiya.

L'étranger : Très tôt le matin, je quitte.

Nagudu : Da zakara ya koka ka tahi.

Nagoudou : Il faut te lever dès le premier chant du coq.

Baƙo : E, tun ba yi kuka ba ina tahi.

L'étranger : D'accord, je partirai, avant meme qu'il ne chante.

Nagudu : Yanzu Baƙo ba ka tuwari ; ko ?

Nagoudou : Etranger, tu ne tousses pas, n'est-ce pas ?

Baƙo : Ina tari kadan.

L'étranger : Je tousse un peu.

Da maganarsa irin ta wanda ba bahaushe ba.
Dans un accent d'un locuteur non natif hausa.

Nagudu: Inda ɗan tuwara; in ji!

Nagoudou : Tousse un peu, pour que j'en apprécie… !

Ya yi tari da ƙari.

Il tousse avec force.

Nagudu : A'a ! Wannan ya yi yawa mana! Ɗan rage ; in ji.

Nagoudou : Non ! C'est trop ! Tousse doucement.

Ya ɗan tara.
Il tousse avec moins de force.

Nagudu: To, yawwa! Kama tuwarin nan in ya kama ka...

Nagoudou : C'est bon comme cela ! Si la toux te tient…

Baƙo : E, e.

L'étranger : Oui, oui.

Nagudu : Ka ga, a unguwal kowa ya san ni banna tari.

Nagoudou : Tu vois dans ce quartier, tout le monde sait que je ne tous pas.

Baƙo : E ; haka ne ; haka ne.

L'étranger : Oui, d'accord ; d'accord.

Nagudu : Don kar a ji tari ; a ce gidan can da baƙo.

Nagoudou : Pour que ta toux n'indique pas ta présence chez moi.

Baƙo : E ; e.

L'étranger : Oui, Oui.

Nagudu : E ; kuma a yi sabko a tafi.

Nagoudou : Oui, et puis il faut te lever très tôt.

Baƙo : E ; haka ne.

L'étranger : D'accord.

Yayin da ake wannan matar na can tana damun fura.
Pendant ce temps l'épouse de Nagudu pétrie le foura.

Nagudu : Ke hurar ta damu ?

Nagoudou : Le foura, est-il prêt ?

Rabi : E.

Rabi : Oui.

Nagudu : To, kawo mai.

Nagoudou : Alors, apporte-le-lui.

Baƙo: E; haka ya yi kyau.

L'étranger : Oui, ça c'est bien.

Nagudu : E ; haka nan ne.

Nagoudou : Oui, c'est juste.

Baƙo : Gwara da ka gaya mini. Da na yi iri namu, mutanen Bornu.

L'étranger : C'est bien tu m'aies informé. Sinon j'allais faire comme chez nous au Bornou.

Nagudu : Miƙa mai. Aza mishi da kyau.

Nagoudou : Donne-lui. Pose-la bien.

Matar ta ajiye mai ƙwaryar hura da ruwa yayin shi baƙon ya janye sandarsa don ya gyara zaman shan furar.
La femme lui dépose la calebasse de foura et une autre contenant de l'eau. L'étranger arrange son bâton pour se mettre à l'aise avant de boire le fura.

Baƙo : Ni butana ma ba ruwa a ciki.

L'étranger : Il n'y a pas d'eau dans ma gourde

Nagudu : Wannan sauran zumuwar adana mini ita. Uhum, adana mini ita. (Ya umurci matarsa)

Nagoudou : Garde-moi ce reste du miel. Uhum, garde-le-moi. (Il instruit sa femme.)

Nagudu ya nunawa baƙonsa furar tare da bar masa wuri, don ya shata cikin natsuwa.

Nagoudou encourage son étranger à boire le foura en se retirant pour le laisser en profiter sans gêne.

Rabi: Am… Baƙo, a sha. E, a sha.

Rabi : Am… étranger, bois. Bois bien.

Baƙo : Uhum.

L'étranger : Uhum.

Baƙo ya fara shan furar.
L'étranger se met à boire le foura.

Nagudu : Ai, dokar sarki ce ba a tada ta. *(Ya nanata tare da neman yadda zai ɓullo ma lamarin.)*

Nagoudou : C'est la décision du roi, on n'y peut rien. (Il se répète la même phrase, cherchant une issue).

Ya ci gaba da yi ma baƙonsa hira.

Il continue à entretenir son étranger.

Nagudu : Sha ka ƙoshi.

Nagoudou : Bois-en à ta faim.

Baƙo: Ai wannan ba ka fadi ba, ina sha. Ga wannan yunwa! (*Ya ce yayin da yake murmusawa.)*

L'étranger : Mais ça ne vaut pas la peine de me le dire. Avec la faim que je ressens, je ne m'en priverai pas ! (Il le dit en souriant)

Nagudu : Amma kau ka ɗauko dare ; wallahi. Ga rishin sani !

Nagoudou : Tu es vraiment arrivé très tard dans la nuit. Ne connaissant pas la nouvelle décision du roi !

Baƙo: E mana; dare anka yi. Can ne, ana zauna ana wani gangan aure.

L'étranger : C'est vrai je suis arrivé très tard dans la nuit. J'étais là-bas à un tamtam de mariage.

Nagudu : To, sha hura ita ma ganga ce ai. Ita ma ganga ce, ai. (*Ya faɗa cikin ba'a.)*

Nagoudou : D'accord, bois ton foura, c'est aussi un tam-tam. Oui, c'est aussi un tam-tam. (Il ironise)

Ya ci gaba da shan furar. Yayin da Nagudu ke nuna cewa santi[4] *ne baƙonsa yake yi.*
L'étranger continue de boire son foura alors que Nagoudou essaie de lui faire croire qu'il parle sous l'effet justement du foura.

Nagudu: E, sha ka yi ganggar cikinka. Sha, ka ƙoshi.

Nagoudou : Oui, bois-en et fais de ton ventre un tam-tam aussi. Bois-en à ta faim.

Baƙo ya ci gaba da shan furar cikin zumuɗi, ba tare da ya san tsonar da masaukinsa ke yi masa ba. Ya ƙare shan fura, ya ɗauki faifai ya rufe ƙwaryar.

L'étranger continue de boire le foura sans se rendre compte des insinuations de son hôte. Il finit de boire et referme la calebasse avec un van.

[4] **Santi** en Haoussa est une expression qui veut dire qu'une personne dit quelque chose parce que la nourriture qu'elle mange est très bonne. Autrement dit, l'idée lui est venue grâce à la bonne qualité de la nourriture.

Nagudu : Ah ƙara !

Nagoudou : Ah non, bois-en encore !

Baƙo : Ah, ya isa !

L'étranger : Ah non, merci !

Nagudu : Asshe ?

Nagoudou : Vraiment ?

Baƙo : Ah ya isa, wallahi ! Na gode kwarai wallahi ! *(Cikin fara 'a.)*

L'étranger : Ah non, j'en ai bu à ma faim ! Merci beaucoup ! (Tout content)

Nagudu : Ahan.

Nagoudou : Tant mieux.

Baƙo : Na gode ; na gode kwarai wallahi !

L'étranger : Merci, merci beaucoup vraiment !

Nagudu : Ni ma tashi za ni yi, in kwanta. A sha ruwa.

Nagoudou : Moi-même je vais aller me coucher. N'oublie pas de boire de l'eau.

Ya ɗauki ƙoranshi, amma kafin ya tafi sai ya ƙara yi wa baƙonshi tuni da cewa ya yi sabko kamar yadda suka tsaida.
Il prend les récipients, mais avant de quitter, il fait un dernier rappel à son étranger, en ces termes.

Baƙo : Hey ; wai wai !

L'étranger : Ce n'est pas simple !

Nagudu : To baƙo !

Nagoudou : Etranger !

Baƙo : Uhum !

L'étranger : Uhum !

Nagudu : Kamar dai yadda na gaya ma.

Nagoudou : Comme je t'ai déjà dit.

Baƙo : E ; wannan ai…

L'étranger : Oui, ne t'en fait pas…

Nagudu : Da zakara ya yi kuka…

Nagoudou : Dès que le coq chante …

Baƙo: Tun ba yi kuka ba ina tafiya. Wallahi !

L'étranger : Je partirai avant même qu'il ne chante, je te jure !

Nagudu: … A yi niyya a tafi. In ka tashi …

Nagoudou : …Dès que tu te lèves, fais tout pour partir sans perte de temps

Baƙo : Uhum !

L'étranger : Uhum !

Nagudu : Mu ko, ba mu tashi ba, ka tafi.

Nagoudou : N'attend pas notre réveil pour partir.

Baƙo : Yawwa ; yawwa.

L'étranger : D'accord ; D'accord.

Nagudu : Kada ka tada mu. Ka yi niyya ka tafi.

Nagoudou : Ce n'est pas la peine de nous réveiller. Va tout simplement.

Baƙo : Yawwa ; na gode wallahi ; na gode fa !

L'étranger : D'accord ; merci beaucoup !

Nagudu : Ba godiya ba, a yi niyya a tafi.

Nagoudou : Ça suffit, tes remercîments ; il faut partir comme convenu.

Baƙo : Aa ; Yawwa, fa !

L'étranger : Ah, c'est d'accord !

Nagudu ya shige ɗaka domin baƙon sa ya kwantawa, ya huta.
Nagoudou entre dans sa chambre pour laisser son étranger se coucher et se reposer.
Bakon ya gyaggyar shimfiɗarshi. Yana magana shi kaɗai.
L'étranger prépare sa natte en monologuant.

Baƙo : Kai, gari da doka ! Wannan fura mai zuma, ai ya fi fura mai nono.

L'étranger : Ah, un village avec des restrictions ! Ce foura au miel est meilleur que celui préparé avec du lait caillé.

Baƙo *(Ya ci gaba da magana shi kaɗai) :* Bari mutun ya futa wannan tafiya na kwanaki.

L'étranger (Il continue son monologue) : Bon, c'est mieux que je me repose un peu de cette marche de plusieurs jours.
Ya miƙe a hankali, tare da yin matashin kai da jikarshi.
Il s'étale calmement sur la natte, son sac lui servant d'oreiller.
Jim kaƈan, matsanci ciyon ciki ya tayar da shi.
Peu après, des douleurs au ventre le réveillent.

Baƙo : Kai ; wannan abu, ciwo ciki ne ko mine ne ? Ni ban taba yin irin shi ba. Subahanalla ! Subahanalla !

L'étranger : Ah, ça ! Est-ce le mal de ventre, ou quoi ? Je n'ai jamais ressenti de telles douleurs ! Que Dieu m'en garde ! Que Dieu m'en garde !

Ya sake kwantawa, amma ciyon cikin ya sake dawowa. Ya tashi zaune, yana juyayin abin da ke iya faruwa da shi.
Il se recouche mais les douleurs reprennent de plus belle. Inquiet, il se met assis.

Baƙo : Allah ya sa a kare lafiya wannan abun ! Wannan ciwon ciki fa... !

L'étranger : Puisse Allah m'apporter la guérison ! Ces maux de ventre… !

Ciwon cikin ya ci gaba har sai da baƙon ya rasu.
Les maux de ventre continuent jusqu'à la mort de l'étranger.
Da safe, Nagudu ya fito don ya gani in baƙonsa ya tafi tun da asuba, kamar yadda suka ajiye.

Abin mamakin baƙo yana nan kwance. Cikin mamaki ya isa wurin shi tare da yi kiran shi.
Le matin, Nagoudou vient vérifier si son étranger est parti dès l'aube comme convenu. A sa grande surprise, il le retrouve encore étalé sur la natte. Il s'y approche et lui parle avec agacement.

Nagudu : Kai, to sabkon naka ke ga ?

Nagoudou : Toi, c'est ça ton départ à l'aube ?

Ko motsi baƙo bai yi ba. Ya ci gaba da kiran shi yayin da yake ƙara kusantar shi.

L'étranger ne bouge pas. Il continue à l'appeler tout en s'approchant davantage de lui.

Nagudu : Baƙo kai, safiya ta yi ! Kai, sabkon kenan? Na Washa?

Nagoudou : Etranger ! Il fait jour ! Hei, c'est ce que tu appelles quitter à l'aube ? Etranger de Washa ?

Shiru kake ji. Ba motsi balle magana. Ya daddage shi tare da yi masa magana.
Toujours pas de geste ni parole. Nagoudou touche l'étranger en l'appelant.

Nagudu : Kai baƙo ! Kai na Washa ? Na Washa? Na Washa? Kai bari wasa fa?

Nagoudou : Hé étranger ! L'homme de Washa ? L'homme de Washa ? Ecoute, ce n'est pas le moment de blaguer !

Nagudu yaƙi yarda da abin da yake gani.

Nagoudou refuse de croire à ce qu'il constate.

Nagudu : To ! Kai baƙo ! Kai ! kai ! baƙo ! To ?

Nagoudou : Dis-donc ! Hé étranger ! Etranger ! Hé ! Etranger ! Comment ça ?

Ya taɓa hannun baƙo don ya ji yanayin jikin. Ya ji sanyi lagas.
Il touche la main de son étranger pour en prendre la température. Il constate que le corps est frais.

Nagudu : A'a, jikin sanyi ƙaras !

Nagoudou : Ah ! Le corps est vraiment frais !

Nagudu : (Ya taɓa hannun guda na baƙon. Shi ma da sanyi. Ya ce) : To, mutane ! A'a !

Nagoudou : (Il passe sa main sur l'autre main de l'étranger. Cette main est aussi fraiche. Il dit) : Ce n'est pas possible ! Non !

Dan ya tabbatar da cewa baƙo ya mutu, sai ya kai kunnensa kan ƙirjinshi, ko ya ji bugawar zuciya. Amma ina, shiru ne.
Pour s'assurer que l'étranger est réellement mort, Nagoudou passe son oreille sur sa poitrine pour écouter les battements du cœur. Mais hélas aucun battement.

Nagudu : Ai… babu… ! Shegen ya mutu ! Shegen ya mutu ! *(Ya faɗi cikin kiɗima)*

Nagoudou : Ah… c'est fini… ! L'imbécile est mort ! L'imbécile est mort ! (Il parle dans la confusion)

Ya ruga cikin gida wajan matarsa da yi ruwa ta yi tsaki wajen sauke baƙon don ta samar da mafita.
Il court vers son épouse qui l'a convaincu d'héberger l'étranger pour qu'elle l'aide à trouver une solution.

Nagudu : Subahanallahi ! Rabi ?

Nagoudou : Que Dieu nous en préserve ! Rabi ?

Rabi : Na'am ! Mine ne maigida ? Mi anka yi ?

Rabi : Oui ! Qu'y a-t-il chéri ? Que s'est-il passé ?

Nagudu : Ga mutunenki nan !

Nagoudou : Voici ton type !

Rabi : Ba kwanan na yake yi ba ?

Rabi : N'est-il pas en train de dormir ?

Nagudu : Wa ya ce miki wannan kwana ne ? Tahi ki gani ; in kwana ne. Na ce miki ya mutu !

Nagoudou : Qui te dit que ça c'est du sommeil ? Va voir si c'est le sommeil ! Je te dis qu'il est mort !

Rabi : *(matar ta Nagudu ta tafi wajen baƙon tana kiran shi, kamar haka) : Baƙo ! Baƙo ! Ya yi mi ?*

Rabi : (son épouse se dirige vers le corps de l'étranger en l'appelant) : Etranger ! Etranger ! Il est quoi ?

Nagudu : Na ce miki ya mutu !

Nagoudou : Je te dis qu'il est mort !

Rabi ta ɓara kururuwa amma mijinta ya yi cip, ya riƙe mata baki.
Rabi pousse un grand cri mais son époux se jette sur elle et lui ferme la bouche.

Nagudu : Wa za ki yi wa ihu ? Wa ya ce in kawo shi nan, ba ke ba? Ki tara mini mutane a ce na aje baƙo? To diba, kwashe shi za ki yi. Ke ga ni garin barin shi za ni yi. Yan kuɗin da maƙwabta ke bi na; in sun zo, suka tambaya, ki ba su.

Nagoudou : Pour qui tu vas crier ? Qui m'a forcé à l'accepter, ce n'est pas toi ? Ne m'attire pas du monde qui va constater que j'ai hébergé un étranger. Ecoute, tu vas te débrouiller avec le cadavre. Moi je vais quitter ce village ! L'argent que je dois aux voisins, s'ils viennent les réclamer, tu le leur rembourses.

Ya juya baya, yana shirin gudu daga garin, amma matarsa ta hanashi tare da bas hi mafita.

Il tourne le dos pour s'en aller, mais son épouse le dissuade en lui proposant une solution.

Rabi : Ina za ka maigida ? Komo yi hanƙuri. Komo ka ji. Komo in koya maka dubarar mu ta mata.

Rabi : Où vas-tu mon mari ? Reviens et sois patient. Reviens. Reviens je vais te montrer notre astuce de femme.

Nagudu : Babu wata dubara. Ya riga ya mutu.

Nagoudou : Il ne peut y avoir de solution. Il est déjà mort.

Rabi : Zo mana ; in koya maka dubararmu ta mata.

Rabi : Reviens, je vais t'apprendre notre astuce de femme.

Nagudu : Shin mutun ya mutu ; wata dubara a akwai ?

Nagoudou : Je ne vois pas d'astuce possible pour celui qui est déjà mort !

Rabi : Zo kai dai ! zo ka jiya !

Rabi : Ne t'en fait pas ! Reviens et écoute-moi. !

Cikin kiɗima Nagudu ya haƙura.
Nagudu revient, resigné.

Nagudu : To.

Nagoudou: D'accord.

Rabi: Ka san wadda za a yi?

Rabi : Sais-tu ce que nous allons faire ?

Nagudu : Ban sani ba.

Nagoudou : Je ne sais pas.

Rabi: Yanzu ka san, tunda gobe masallaci…, ko?

Rabi : Tu sais que demain c'est un jour spécial à la mosquée…, n'est-ce pas ?

Nagoudou : E.

Nagoudou : Oui.

Rabi : Gobe ana sadaka masalaci. Ina da adaka babba. Sai mu ɗauke shi mu zunduma ; mu sa wasu ɣan kuɗi a ciki, rabi a waje. Wani ya zo sai ya ɗauka. Shi kenan.

Rabi : Tu sais demain les gens amène l'aumône à la mosquée. Moi, j'ai une grande cantine. On prend le cadavre et on le met dans la cantine. On ɣ met un peu d'argent, une partie de billets de banque à l'extérieur. Ainsi, si quelqu'un vient et qu'il voit l'argent, il va prendre la cantine et ce sera fini.

Nagudu : Ashe ?

Nagoudou : Vraiment ?

Rabi : I.

Rabi : Oui.

Nagudu : Maganar ga taki gaskiya ce.

Nagoudou : Ce que tu dis est vrai.

Rabi : To, mu je.

Rabi : Allons-y, alors.

Nagudu: To, mu je mu ɗauko akwatin. Amma in ba dan shi ba…

Nagoudou : Alors, allons-y prendre la cantine. Mais sans cette idée…

Suka shiga ɗaki, suka ɗauko wani babban akwati na katako. Suka ajiye shi kusan mamacin.
Ils entrent dans la case et ressortent avec une grande caisse en bois. Ils la déposent près du cadavre.

Rabi : Bari a maida shi na wajen.

Rabi : Ramène-le par là.

Nagudu: A'a bar shi haka nan.

Nagoudou : Ah, non laisse-le comme ça.

Nagudu ya nemi matarshi ta kama su saka shi cikin akwatin.
Nagoudou demande à sa femme de l'aider à le mettre dans la caisse.

Nagudu : Kama.

Nagoudou : Prends.

Ya kama wajen kai, matarsa wajen ƙafafuwa. Da ya ji nauyi sai ya ce matar ta dawo wurin shi, shi koma wurin ta ; saboda ta fi ƙarfi, ga alama.
Il prend les épaules et son épouse prend les pieds. Quand il sent qu'il ne peut pas soulever la partie, il demande à sa femme de venir à sa place et lui il prend la place de la femme apparemment plus forte que lui.

Nagudu: Ke, komo nan wajen kai!

Nagoudou : Toi, viens vers le coté de sa tête !

Rabi : Kama nan, kai ma, maigida !

Rabi : Tiens par-là, voyons cher mari !

Nagoudou : Koma can kama ni ce ! Ai ke san yana da nauyi.

Nagoudou : Retourne là-bas et tiens, je te dis ! Tu sais bien que c'est lourd.

Ta kama wurin da ya nuna mata.
Elle prend le côté indiqué.

Rabi : Uhum, ya fi wancen waje nauyi !

Rabi : Uhum, c'est plus lourd que l'autre côté !

Nagudu: Haba, Kama. Yo na haka.

Nagoudou : Prends avec force. Viens de ce coté

Rabi : Ah ah Maigida, nauyi addakwai !

Rabi : Non, cher mari, c'est très lourd !

Nagudu : Yau, ba dan na san akwai nauyi ba ne ; na ce ki koma can wajen. Ai dan na san akwai nauyi na.

Nagoudou : C'est justement parce que c'est lourd que je t'ai demandé de prendre ce côté. C'est parce que c'est lourd effectivement.

Suka tattali gawar suka saka cikin akwatin. Suka saka ɣan kayan sa tare da shi.
Ils trainent le cadavre et le place dans la caisse. Ils ɣ placent également son sac contenant ses effets.

Rabi : Asshe gawa nauyi gare ta !

Rabi : Je ne savais pas qu'un cadavre est aussi lourd !

Nagudu: Asshe; wa ya gaya miki!

Nagoudou : Alors tu l'as appris à tes dépens !

Suka rufe akwatin suka nufi masallaci. Da ɣake akwatin na da nauyi sosai, suka dai ja ta hakan nan don gudun safiɣa ta waɣe musu.
Ils referment la caisse et la trainent jusqu'à la mosquée en se dépêchant avant la levée du jour.

Nagudu : Kama ; kama maza !

Nagoudou : Prends ! Dépêche-toi !

Uhum ; in ji ta tare da ƙoƙarin tsara akwatin. Ta nufi wani waje.
Uhum ; elle essaie de soulever la caisse e te prendre une autre direction que celle de la mosquée.

Nagudu : Ke ja, yi nan ; ba masallaci za mu ba ! Je ki dai !

Nagoudou : Tire, passe par ici. On va à la mosquée ! N'est-ce pas ? Continue !

Ganin ba ya iya tsarawa sama, sai Nagudu ya juya, yana tura akwatin da bayan sa, yayin da matar ita take ja. Yana yi yana yi wa gawar faɗa.
Ne pouvant pas soulever la caisse tout seul, Nagoudou y oppose son dos et pousse pendant que son épouse fait l'effort de la tirer dans la meme direction. Tout en poussant il continue à gronder le cadavre.

Nagudu : Ka zo ka mutu gidan mutane ! Gidanka ne ? (Yana yi wa gawar magana kamar dai tana jin shi ne.)

Nagoudou : Tu es venu mourir chez autrui ! Est-ce que c'est chez toi ? (S'adressant au mort comme s'il pouvait l'entendre.)

Sannan ya juya wajen matarsa.
Et puis il se tourne vers son épouse.

Nagudu: Ke, ja! Ja ke!

Nagoudou : He, tire ! Toi, tire !

Rabi : Kai, nauyi !

Rabi : Vraiment, c'est très lourd !

Nagudu: Ai ke ki kawo muna wanga rikici! Ja dai ; tahi dai da shi !

Nagoudou : C'est toi qui nous as attiré tous ces ennuis ! Alors tire ! Tire !

Da kyar suka samu suka kai akwatin masalaci. Suka soka takardar kuɗi gika guda ga bakin akwatin suka rufe, suka tafiyar su.
Ils parviennent difficilement à amener la caisse à la mosquée oú ils la laissent avec un billet de mille francs coincés à la fermeture.
A masalaci
A la mosquée
Can, sai Ladan ya zo masalaci.
Peu après, le muézin arrive à la mosquée.

Ladan : Niyya masalata ! Niyya masalata ! Salatu hairun mina naumi ! Assalatu hairun mina …

Le Muezzin : Fidèles apprêtez-vous ! Fidèles apprêtez-vous ! La prière est plus méritoire que le sommeil ! La prière est plus méritoire que …

Ganin akwati da ya yi shi ya katse mishi magana.
La vue d'une caisse lui coupe la parole.

Ladan: Aaa…? *(Ya tambayi kan shi)*

Le Muezzin : Quoi… ? (Se demande-il)

Ya yi gyaran muriya, sannan ya ci gaba.
Il racle la gorge avant de continuer.

Ladan : Mutun ne ? Ana sallama ! Malam Amadou ? Mi nike gani, kai !

Le Muezzin : Est-ce une personne ? Que la paix soit avec toi ! Malam Amadou ? Mais qu'est-ce que je vois ?

Ya matsa kusan akwatin, ya fidda takardar kuɗin, cikin mamaki da murna.
Il s'approche de la caisse et retire le billet, souriant et surpris.

Ladan: Ahan, Ikon Allah! Wannan akwati ne cike da kuɗi, har yake amai! Aka kawo sadaka, aka aje a masalaci? Ha, ha, Allah Sarki! Allah na yi ma godiya !

Le Muezzin : Ah oui, Dieu est puissant ! Une cantine remplie d'argent jusqu'à débordement ! Quelqu'un l'a déposée à la mosquée ! Ha, ha ! Dieu est miséricordieux !

Ya ɗaga hannuwa sama, ya yi wa Allah godiya.
Il leve haut les mains en signe de remerciement à Allah

Ladan: Ubangiji Allah, Ubangiji Allah na ma godiya! Allah na gode ma !

Le Muezzin : Allah mon Dieu, Allah je t'en remercie ! Je t'en remercie Allah !

Ya saka takardar kuɗin cikin aljihu, sannan ya ci gaba da magana shi kaɗai.
Il retire le billet de mille francs et le met dans sa poche en continuant son monologue.

Ladan: Aaa, asshe komi ma da rana shi! Ka gani ana ta cewa Ladan Ladan…. Wani bi wasu su zage ni ; wasu su … ba abinda ba a yi mini. Asshe Allah da abinda ya gani ! Yanzu da liman aka yi mini, da ina za ni samun wannan tsintuwa !

Le muezzin : Aha, toute chose a une utilité ! Souvent les gens pensent que le muezzin …. Certains m'insultent, d'autres pensent à n'importe quoi ; j'en ai vu de toutes les sortes. Mais, c'était sans compter avec la volonté de Dieu. Cette opportunité n'aurait pas pu m'arriver si on ne m'avait pas nommé muezzin !

Ya kai can, ya kawo nan, yana dariya. Yana murnar cewa ya yi sa'ar yin tsintuwar waɗannan makuɗan kuɗaɗe. Ya tsaya kan akwati. Ya aje gorar sa. Ya kame gindin sa hannu bibbiyu. Sannan ya ci gaba da magana shi kaɗai.
Il va et vient, en riant. Il est content d'avoir eu la chance de trouver cette cagnotte. Il s'arrête devant la caisse, dépose sa canne, pose ses mains à la hanche et continue son monologue.

Ladan : Lailaha illalaha ! Ah, ni Ladan ni Ladan. Yau ga ni da akwati cike da kuɗi !

Le Muezzin : Dieu est unique ! Ah, moi le muezzin ! Aujourd'hui, me voici avec une caisse pleine d'argent !

Ya nufi kofar masallaci, ya gani ko da wani mutum kan haniyar na zuwa. Da yaga ba kowa sai ya dawo dan ya ga yaya zai yi ya kai akwatin gida cikin siri.
Il sort de la mosquée pour voir si personne n'arrive. N'ayant rien vu, il revient et cherche comment amener vite la caisse à la maison à l'insu de tout le monde.

Ladan: Bari ka gani, in yi maza, in kai shi gida. Su Malam Sanusi da wani dogon wuridin shi, yanzu za ka ga… da wasu ɣan ƙafafun shi awa… awa na takaraukarau ta sha ruwa.

Le Muezzin : Je dois me dépêcher pour amener ma cantine à la maison. Il ne faut pas que malam Sanoussi, avec sa longue invocation, me trouve ici. Ses jambes comme, comme un perroquet mouillé.

Ya shirya ya ɗauki akwatin. Akwati ga nauyi.
Il se met en position de prendre la cantine, très lourde.

Ladan : Kai, kai kai dankari ! Amma ko ba ƙaramin arziki ne a ciki ba. (*Ai duk dubarar ka sai ka zo gida !*)

Le Muezzin: He, he he! C'est gigantesque ! Il doit y avoir beaucoup d'argent. (Je ferai tout pour t'amener à la maison !)
Ya yi dabara da kyar. Ya samu ya tattalle akwatin. Bayan ya fita sauran masalata suka zo. Suka yi mamaki rashin tarar da Ladan. Da yake sun ga gorarsa, suka yi ta fashin baƙi. Wannan ya ce haka, wancen ya ce haka.
Il parvient enfin à prendre la caisse. Après sa sortie de la mosquée, les fidèles arrivent. Ils sont surpris de n'avoir trouvé que la canne de Ladan. Chacun commence à émettre des hypothèses, les unes plus vraisemblables que les autres.

Masallaci 1 : To, wannan sandar Ladan ce, ko ?

Fidèle 1 : Mais ça c'est la canne du Muezzin, n'est-ce pas ?

Masallaci 2 : E, Ita ce fa !

Fidèle 2 : Oui, c'est bien la sienne !

Masallaci 3 : Ni fa na ji kiran salla na ƙarshe. Kasan jiki da jini.

Fidèle 3 : Moi en tout cas j'ai entendu le dernier appel à la prière. Il se peut que quelque chose se soit arrivé.

Masallaci 4 : Ga rayuwa irin ta yau ; mai yiwuwa yalla cikin ya buga.

Fidèle 4 : Avec la vie d'aujourd'hui ; il se pourrait que son ventre lui fasse mal.

Masallaci 5 : Bari mu yi nafila.

Fidèle 5 : Faisons la prière surogatoire.

Suka yi nafila. Suna cikin yi sai Liman ya shigo tare da yi sallama. Lokacin sallar asuba ya yi kuma za a farawa Ladan bai nan.
Ils se mettent à faire des prières surogatoires. Pendant ce temps le Liman qui dirige la prière fait son entrée avec « Salama alaikum ». *C'est l'heure de la prière du petit matin. Ils commencent la prière sans le muezzin.*
Ɗaya daga cikin masallatan ya yi Iƙama a wurin Ladan. Amma Ladan ya zo kuma ya kama aikin shi kamar da shi aka fara sallar.
L'un des fidèles fait la Iƙama qui débute la prière, jouant ainsi le rôle du Muezzin. Mais, ce dernier arrive et reprend sa place comme s'il était là dès le début.

Sauran masallatan suka karɓa daga baya : Allahu Akbar.

Les autres fidèles répètent après lui : Allah est grand.

Haka suka yi salla, kana suka yi addu'a. Bayan sun kamala, Ladan ya ce a ƙara yin wata.
Ils accomplissent la prière, suivie d'invocations. Puis le muezzin demande des invocations supplémentaires.

Ladan : Liman, a ƙara Fatiya. Allah ka raba mu da tsiya duniya da lahira.

Le Muezzin : Imam, ajoutons des invocations pour qu'Allah nous préserve de la pauvreté ici-bas et à l'au-delà.

Liman ya yi addu'a, yayin da sauran jamma'a suke cewa : « Amin. Allah ya sa mu gama lafiya ».
L'Imam fait des invocations pendant que les autres fidèles l'encouragent par des séquences de : « Amen. Puisse Allah nous accorder une bonne fin. »
Aka shafa, kuma aka yi musafaha. Ana cikin wannan sai Liman ya nemi dalilin da ya sa ba su tarda Ladan ba a masalaci.
Ils achèvent les invocations et se saluent. Entre temps l'Imam demande au muezzin pourquoi il n'était pas à la mosquée à l'arrivée des fidèles

L'Imam : Ladan, bayan assalatu ba mu tardaka ba a masalaci !

Le marabout qui dirige la prière à la mosquée : Ladan, qu'est ce qui s'est passé ? On ne t'a pas trouvé à la mosquée après le dernier appel à la prière !

Ladan ya gano da dole say ya bada bayani
Le muezzin a compris la nécessité de se justifier.

Ladan : Eee ; na fito ma… ai har na zo masalaci ma, shin ba ku tararda sandata ba ne ?

Le muezzin : Evidemment, je suis venu à la mosquée. N'avez-vous pas trouvé ma canne ?

Sauran masalata : Ee, haka ne. Ga ta nan ma.

Le reste des fidèles : C'est vrai. Voici la canne.

Ladan : … Yawwa, sai cikina ya ɗan buga.

Le Muezzin : … Voila. Après mon ventre a commencé à me faire mal.

Liman da sauran Masalata : Asha ! Asha ! Allah ya sawaka !

Le marabout qui dirige la prière à la mosquée et les autres fidèles : Que dieu nous en garde ! Que dieu nous en garde ! Puisse Allah te guérir !

Ladan : Sai na koma gida.

Le Muezzin : C'est pourquoi je suis retourné à la maison.

Liman da sauran masallatan suka yi masa fatan Allah ya sawaka.

Le marabout qui dirige la prière à la mosquée et les autres fidèles lui souhaitent bonne guérison

Ladan: Uhm, cikina ya jiwaa.

Le Muezzin : Uhm, mon ventre m'a fait mal.

Sauran Masalata : Allah ya koro sauƙi.

Les autres fidèles : Puisse Allah te guérir.

Liman ya fita yana cewa: to sai an jima.

Le marabout qui dirige la prière à la mosquée prend congé de ses fidèles en disant : Bon, à tout à l'heure.

Sauran Masalata : Amin ! Amin summa amin.

Les fidèles : Amen ! Amen ! Amen !

Ladan ya jira mutane suka fita sai ya tsayar da abokinsa malam Amadu don su yi shawara.
Le muezzin a attendu que les fidèles sortent de la mosquée pour approcher son ami Amadou pour une concertation.

Ladan : Malam Amadu !

Le Muezzin : Malam Amadou !

Amadu : Na'am, magana kake ?

Amadou : Oui, tu t'adresses à moi ?

Ladan : E !

Le Muezzin : Oui !

Amadu : To.

Amadou : D'accord.

Ladan : Mu gaisa sannan. Muna lafiya ? Lafiya lau !

Le Muezzin : On se salue d'abord. Bonjour ! ça va bien !

Amadu : Yaya anka ji da jikin ?

Amadou : Comment va ta santé à présent ?

Ladan: Ah, jiki da sauƙi. Malam Amadu, ka san duk garin nan ba ni da wani amini sai kai.

Le Muezzin : Ah, je vais mieux. Malam Amadou, tu sais que dans ce village tu es mon seul ami.

Amadu : Da kyau !

Amadou : Effectivement !

Ladan : Ba ni da abokin shawara sai kai.

Le Muezzin : Tu es la personne à qui je demande conseil.

Amadu: Na'am!

Amadou: C'est cela!

Ladan: To, wata ƴa niyya ce na ɗauka.

Le Muezzin : J'ai une intention.

Amadu : Allah ya sa ta alheri ce !

Amadou : J'espère qu'elle est bonne !

Ladan : Ah, ta alheri ce !

Le Muezzin : Ah, c'est une bonne intention !

Amadu : Madalla.

Amadou : C'est bien alors.

Ladan : Ta alheri ce !

Le Muezzin : C'est une heureuse entreprise !

Amadu : Yawwa, to madalla !

Amadou : Alors, c'est bien !

Ladan : Ai mu ba ma tare da komi in ba alheri ba !

Le Muezzin : Nous, nous n'entreprenons que de bonnes choses !

Amadu: Yawwa! Alherin dai nike so in ji.

Amadou : C'est bien. Je préfère entendre les bonnes nouvelles !

Ladan: Yawwa. To abin da nike so…Kai arme dai nike so in yi. Na kawo mace.

Le Muezzin : Bien, ce que je voudrais… bref, je voudrais me marier. Prendre une femme.

Amadu : Ka yi biyu ?

Amadou : Une deuxième femme ?

Ladan: Yo, in ban yi biyun ba, na yi abin da na yi dai.

Le Muezzin : Si je ne prends pas une deuxième, je ferais autre chose.

Amadu: To, Allah shi sa!

Amadou: Puisse Allah agréer!

Ladan: Kuma armen da yake kai ka san duk mutane, kuma ka san masu hankali.

Le Muezzin : Je veux dire par rapport au mariage, tu connais les femmes du village ayant de bon caractère.

Amadu: Na'am.

Amadou: Oui.

Ladan: Arme nike so na budurwa. Budurwa nike so…

Le Muezzin : Je voudrais épouser une jeune fille. Je veux une jeune fille…

Amadu : Budurwa ?

Amadou : Une jeune fille ?

Ladan : I, mai nonna.

Le Muezzin : Oui, qui a les seins murs.

Amadu: Cap! Akwai wata ɗiyar abokina kuwa. Ya ɗauke ni da daraja. In ka gan ta gaban wannan kamar ita ton yi ma kanta !

Amadou : Ça tombe bien ! Il y a la fille à mon ami. Il a de la considération pour moi. C'est une très belle fille avec des seins comme tu viens de les décrire !

Ladan : Uhm ?

Le Muezzin : Uhum ?

Amadu : Haba, damɓareriya !

Amadou : Oui, une très belle fille !

Ladan: Irin ta nike so.

Le Muezzin : Elle me va parfaitement.

Amadu: To an gama wannan.

Amadou : Alors, considère que c'est déjà fait.

Ladan: To yanzu yadda za a yi; ka je ka tambaya. Ni ba wani a je a kai a kawo ba ne.

Le Muezzin : Maintenant vas me demander sa main. Je voudrais que le mariage soit célébré rapidement.

Amadu: Ah, in dan tambayawa, wannan daga na tambaya yana ba mu.

Amadou : Ne t'en fait pas, dès que je demande sa main, il va me la donner.

Ladan: To, ka san wannan abu da ake cema zuba ɗauki?

Le Muezzin : Bon, tu connais ce qu'on appelle verse l'argent et prend la marchandise ?

Amadu : Zuba ɗauki ?

Amadou : Verse et prend ?

Ladan : E.

Le Muezzin : Oui.

Amade.

Amadou : Je vois.

Ladan : Wato a lisafe maka duka ko nawa ne, duka abinda ya kamata a ba da, da ma wanda bai kamata ba, a gaya min.

Le Muezzin : Je voudrais dire, tu demandes à la famille de la fille de te dire tout ce qu'il faut et même plus. Tu n'as qu'à me le rapporter.

Amadu : Duka gaba ɗaya ?

Amadou : Le tout d'emblée ?

Ladan : E, a gaya mini.

Le Muezzin : Oui, qu'ils te le disent.

Amadu : An gama ! Ai wannan mutunen dattijai ne. Daga na ce ina son ɗiyar ta shi, zan ba wani, bai hanawa.

Amadou : Considère que c'est fait ! Cet homme-là est un sage. Dès que je lui demande la main de sa fille, au nom d'un ami, il ne va pas hésiter.

Ladan : Na sani yanzu kana nan sai ka tafi, ka riƙa cewa lafiya ma Ladan, ni ina ya samu abin yi, har zaya zuba ɗauke. To don kar ka …

Le Muezzin : Je sais que tu te demandes où j'ai trouvé tous ces moyens. Ne pense pas…

Amadu : To, abu na Ubangiji !

Amadou : Mais non, Dieu est tout puissant !

Ladan: Ashe kana da hankali! Ashe kana a hankali !

Le Muezzin : Tu es vraiment sage ! Tu es sage !

Amadu : Sha'anin arziki na Ubangiji, ai …ba mamaki.

Amadou : Allah peut te rendre riche en un rien de temps, rien d'étonnant.

Ladan: Ka san ana ganin mu muna kiran sallar nan …

Le Muezzin : Comme nous sommes muezzin …

Amadu : Ana dibin ku à tsiyace

Amadou : … On vous considère comme des misérables !

Ladan: E, a tsiyace! Ba a san irin ajiyar da Allah ya yi mamu ba.

Le Muezzin : C'est bien ça, comme des misérables. Ne sachant pas ce que Dieu nous a réservé.

Amadu : Ka gani ?

Amadou : Tu vois. ?

Ladan: E to shi kenan. Ko ɗiyar wace, ka ce su kwantar da hankalinsu. Kuma a faɗa maka abin da za a biya, ka zo ka gaya mini.

Le Muezzin : Oui, je vois. Quel que soit sa famille, dis-leur qu'ils n'ont pas à s'inquiéter. Qu'ils te disent seulement le montant de la dote et tu viens me le communiquer.

Amadu: Shi kenan, an ƙare.

Amadou : C'est bon. On fait comme cela.

Suka tashi yayin da suka ƙare zancen da suke yi.
Ils se lèvent tous les deux à la fin de leur conversation.

Ladan : Eh, da ma dan in faƈa ma wannan ne, sai mu tafi. Kuma sauran zance sai kuma in ka dawo.

Le Muezzin : Voilà, c'était pour te dire cela. Alors allons-y. A ton retour pour la suite.

Amadu : Shi kenan.

Amadou : D'accord ; c'est bien.

Ladan : Uhm, tsaya, ai ka san aka ce "mafarin dare…

Le muezzin : Uhm, attends. Un adage dit que « le début d'une nuit … »

Amadu (*Ya ida karin maganar*) : Almuru !

Amadou (il complète l'adage) : … le crépuscule !

Ladan: To riƙe wannan taka ce.

Le Muezzin : Donc prend cet argent. C'est pour toi.

Ya ba wa Amadou takardar kuƈi ta jika guda. Shi kuwa, ya ji daƈi yana ta murna wannan kyautar.
Il remet le billet de mille francs à Amadou qui s'en réjouit.

Amadu: Kap, duk wannan gaba ɗaya?

Amadou : Ah, tout ça pour moi ?

Ladan ya amsa masa da « e, duk » tare da gyaƈa kai don nuna cewa wannan kyautar ba wani babban abu ne ba dubin da abin da yake da.
Le muezzin répond que « oui, tout l'argent*. » Il accompagne son geste d'un mouvement de la tête qui minimise le cadeau, imaginant la cantine pleine d'argent dont il dispose.*

Ladan: Wannan, ai sai ma ka dawo tukuna!

Le Muezzin : Ce n'est pas grand-chose. J'attends ton retour !

Amadu : Bari in sa ta a aljihu don kar wani ya gani

Amadou : Je cache mon billet dans la poche avant que quelqu'un ne le voit…

Ladan : Sai ka dawo ma.

Le Muezzin : Tu verras à ton retour !

Amadou: To, shi kenan.

Amadou: D'accord, c'est bon!

Suka bar masalacin cikin farin ciki.
Ils quittent la mosquée dans la joie

Ladan ya koma gidanshi fuska a ɓace. Ya tarar da maiƈakinsa ta farka har ma ta shimfiƈa masa tabarma. Ta gayar da shi kamar haka :
Le muezzin rentre chez lui le visage crispé. Son épouse Tanungo, déjà réveillée, a déjà étalé la natte. Elle le salue en ces termes :

Tanungo : Sannu da zuwa Ladan.

Tanoungo : Bonne arrivé Ladan.

Ladan ya juya kai ya yi kamar bai ji ba.
Ce dernier détourne sa tête et fait comme s'il ne l'avait pas entendue.

Tanungo : Sannu da zuwa Ladan, (*ta ƙara nanatawa).*

Tanoungo : Bonne arrivée, Ladan, (elle *insiste).*

Ladan : Yawwa ni ce ; ko ko ? Kai !

Le Muezzin : Je dis-merci, c'est quoi cette manière !

Ya yi tsaki, ya juya kansa.
Matar ta kawo masa farau-farau ; ta durƙusa, ta aje ƙwaryar tare da cewa :
Il siffle son mécontentement et détourne sa tête.
La femme lui amène du foura dilué. Elle s'accroupit et dépose la calebasse en disant :

Tanungo: ga farau- farau, ka sha.

Tanoungo : voici du foura dilué ; bois.

Ladan : Akuya nike ?

Le Muezzin : Me prends-tu pour une chère ?

Tanungo : Assha, Ladan !

Tanoungo : Bien sûr que non, Ladan !

Ladan : Ai ce miki ni ki yi zazahe[5]... Ya ki ɗauki kayanki, kin ji !

Le Muezzin : Je t'ai demandé de me réchauffer le touwo ... Viens reprendre ton foura, tu m'entends !

Ya ci gaba da faƈa. Ya ciro wannan, ya ciro wannan kamar haka.
Il continue à la sermonner. Il lui fait des reproches par-ci par-là.

[5] Le touwo rechauffé

Ladan : Haka nan kullum kina kawo mini farau-farau da wani tsattsama nono da sai ya kwan wajen ukku, ki damo ki kawo mini ; duk cikina na ruɗewa !

Le Muezzin : Toujours c'est pareil. Tu prépares du farau-farau avec du lait décomposé et tu m'amènes. Ce qui me donne de graves problèmes de digestion !

Tanungo : Yi hanƙuri Ladan.

Tanoungo : Pardonne-moi Ladan.

Ladan : Na ƙi ba ni yi !

Le Muezzin : Je refuse de te pardonner !

Tanungo : Yi hanƙuri Ladan.

Tanoungo : Pardonne-moi Ladan.

Ladan : Ni ce na ƙi. Zo ɗauke kayanki, ko mi ! Ba ni sha !

Le Muezzin : J'ai dit non. Viens prendre ton foura ! Je n'en bois pas !

Tanungo: Assha Ladan! Ban saba ganin haka ba gare ka, Ladan!

Tanoungo : Je te trouve étrange, Ladan ! Je ne te reconnais plus, Ladan !

Ladan: To, yau kya gani. In ba ki saba ba, to yau kya gani. Tanungo abin naki ya ishe ni! Dare da rana dai, ni ba ni, ba ta… ; in ban da tashin hankali babu abin da nike gani.

Le Muezzin : Bon, aujourd'hui tu vas voir. Tu dis que tu n'as pas l'habitude de me voir ainsi ! Aujourd'hui tu vas mieux me connaitre. Tanoungo, trop et c'est trop ! Jour et nuit, tu ne fais que me causer des problèmes.

Tanungo: Tashin hankali na! Mi na yi ma? Yi hanƙuri.

Tanoungo : Tu as des problèmes avec moi ! Mais qu'est-ce-que je t'ai fait ? Pardonne-moi.

Ladan : Sai kin kashe ni ! Tashin hankali ! Yanzu abin da za ni tambaye ki, ke Tanungo !

Le Muezzin : Tu vas me tuer ! Que des problèmes ! A présent ce que je te demande, Tanoungo… !

Tanungo: To, ina jinaka.

Tanoungo: Oui, je t'écoute.

Ladan: Wai shekarmu nawa muna tare?

Le Muezzin : Combien d'année avons-nous passé ensemble ?

Tanungo : Talatin da ukku.

Tanoungo : Trente-trois.

Ladan : Yawwa, har da ukku, ko ?

Le Muezzin : Très bien, trente-trois ; n'est-ce pas ?

Tanungo : Uhum.

Tanoungo : Uhum.

Ladan : To, yanzu tun da ki zo gidan nan ban ce saniya ba ko Akuya zuwa tumkiya ; daidai da yar guntuwar kaza nan an taɓa… maƙwabta ko gori su yi mini ; a ce yaka Ladan, ga kazarka ta yi ɓanna !

Le Muezzin : Bien, depuis que tu es venue dans cette maison, je n'ai même pas eu un poulet à plus forte raison une brebis, une chèvre ou une vache ! Aucun voisin n'est venu se plaindre de quoi que ce soit m'appartenant !

Tanungo : To, a talauce, ba a sarauce ba, mu ma muna da iyakar namu, Ladan.

Tanoungo : Mais n'étant pas d'une famille royale, nous pouvons quand même nous satisfaire de ce que nous avons, Ladan !

Ladan: To ni, iyakar nakun ne ban gan shi ba.

Le Muezzin : Mais moi je ne vois pas ce que nous avons.

Tanungo : Muna da shi.

Tanoungo : Nous avons quelque chose !

Ladan: Tunda kika zo gidan nan, kin ga ba haifuwar rana, ba ta dare! Abin da za ni gaya miki; zama da ke ya ishe ni, tashi tafi gidanku!

Le Muezzin : Depuis que tu es venue dans cette maison, tu es restée stérile ! Ce que j'ai à te dire c'est que j'ai marre de rester avec toi, vas chez tes parents !

Tanungo ta yi tagumi, tana mamakin ikon Allah.
Etonnée par les agissements étranges de son époux, elle s'assoit une main contre la mâchoire[6]*.*

Tanungo : Yi hanƙuri Ladan.

Tanoungo : Je t'en prie, Ladan.

Ladan : Na ce ba ni yi !

Le Muezzin : Je refuse !

Tanungo : Nemo yan shaida.

[6] Cela signifie que la personne est malheureuse.

Tanoungo : Cherche des témoins

Ladan : Shaida ?

Le Muezzin : Quels témoins ?

Tanungo : E.

Tanoungo : J'insiste !

Ladan : Hun, lokacin da na je na auro ki, ba ni na sa kai na ba ! Mutane !

Le Muezzin : Hun, n'est-ce pas de mon propre gré que je t'ai épousée ? Voyons !

Tanungo : Nemo ɣan shaida.

Tanoungo : Cherche des témoins.

Ladan : Tsaya, ba wani ɣan shaida ! A musulunce, sau nawa ake sakin mace?

Le Muezzin : Ecoute, ne me parle pas de témoin ! Selon la loi coranique combien de fois un mari peut répudier sa femme ?

Tanungo: Sau ukku.

Tanoungo: Trois fois.

Ladan: To, tahi; na sake ki sau goma sha biyu! Tashi, tahi gidanku !

Le Muezzin : Bien, vas-t-en, je te répudie douze fois ! Va chez ta famille !

Ta yi zaman ta kamar ba da ita yake magana ba.
Da ya ga haka, cikin fushi, ya ce mata :
Elle reste assise comme s'il ne parlait pas à elle.
Enervé par le comportement de sa femme, il lui dit :

Ladan: Ko gidan ba nawa ba ne? Ko arme cillas ne ?

Le Muezzin : ou bien la maison ne m'appartient pas ? Suis-je obligé de rester marié avec toi ?

Tanungo : Yi haƙuri, Ladan.

Tanoungo : Pardonne-moi, Ladan.

Ladan : Ni ce ba ni yi ! Hin, taho ɗauki ɣar ƙwaryarki, iya dai ita a ki cewa kin ka wannan gidan. E ; gangama tahi. Kasma hanya !

Le Muezzin : Je refuse ! Rassemble tes bagages, bien que tu n'aies rien apporté ici à part ces quelque calebasses ! Oui, rassemble tes bagages et vas-t-en !

Ya tura mata ƙwarya. Ta karɓa tare da cewa :

Il lui remet une calebasse. Elle l'a saisi en disant :

Ladan : Da gaskiya kakai ?

Le Muezzin : Tu es vraiment sérieux ?

Ladan : Yau ! Da gaske nikai mana !

Le muezzin : Bien sûr je suis sérieux !

Tanungo : To, na tahi.

Tanoungo : D'accord, je m'en vais.

Ladan : Ɗauki ɣar tabarmarki… Ɗauki… Ɗauri kar ki tahi !

Le muezzin : Prends ta soi-disant natte… prends… J'allais te montrer de quel bois je me chauffe !

Ta juɣa baɣa ba tare da ɗaukar tabarmar ba. Ya ci gaba da takalar ta :
Elle tourne le dos sans prendre ladite natte. Il continue à la provoquer :

Ladan: Zekekiyar wofi, kai! Mutane! Ta tahi, munafuka Allah ».

Le Muezzin : Putin de merde ! Mon dieu ! Va-t'en, espèce d'hypocrite.

Ya kira ta don ɣa ga in har ta tafi.
Pour s'assurer qu'elle est réellement partie, il l'appelle.

Ladan: Tanungo, Tanungo!

Le Muezzin: Tanoungo, Tanoungo!

Ya leƙa ɣa ga lalle ta tafi. Sai ƙara zagawa :
Il regarde à travers la porte où il voit qu'elle est réellement partie. Il l'insulte à nouveau :

Ladan : munafuka.

Le Muezzin : Hypocrite !

Ya je wurin da ɣa ɓoye akwatin, ɣa tattalo ta da kyar amma cikin fara'a. Yana tahe ɣana dariya. Yana faɗin :
Il va là où il a caché sa cantine et la prend tout joyeux en louant Allah :

Ladan: Allah sarki; Allah na yi ma godiya! Allah mai ba kowa! Allah uban kowa!

Le Muezzin : Allah le tout Puissant ; Je Te remercie Allah ! Allah qui donne à tout le monde ! Allah le père de tous !

Ya aje akwatin yace :
Il dépose la cantine et se dit :

Ladan: Barin in ɗan huta.

Le Muezzin : Je me repose un peu.

Ya zauna bisan akwatin ya yi kwance da dariya, sa'annan ya ci gaba da magana.
Il s'assoit sur la cantine en s'éclatant de rire et en continuant son monologue.

Ladan : Ni Ladan, akwati cike da kuɗi ! In ba dan ni da Allah ya yi mini ƙarhin arziki, aka yi mini Ladan. Da yanzu Liman zai samun waɗannan kuɗin. Don wannan ni sarauta in dai ta salla ce, daga Ladan ba ni son ko wace. Ladan kurum !

Le Muezzin : Moi e Muezzin, avec une cantine pleine d'argent ! Si on m'avait fait Imam, je n'aurais pas eu cette cantine ! Moi, je ne veux rien d'autre que la fonction de Muezzin ! Muezzin seulement !

Ya fashe da dariya. Ya ƙare ta da cewa :

Il éclate de rire une fois de plus et dit :

Ladan : Ah ni Ladan ! (*Ya zazzagaya.Ya dawo kan akwatinshi).*

Le Muezzin : Ah ! Moi Le Muezzin ! *(Il fait des va-et-vient avant de s'assoir sur la cantine.)*

Ya ci gaba da maganarshi shi kaɗai.
Il continue son monologue.

Ladan : Allah Sarki, ni Ladan. Da ma ni na sani ; wannan mafarkin ada nike ta yi. Ina ga kullun ina bisa farin doki. Na san arziki ne !

Le Muezzin : Gloire à Allah. Moi Ladan, je l'ai toujours su à travers mes rêves répétitifs dans lesquels je me vois chaque fois sur un cheval blanc ! J'ai su que c'était de la richesse.

Ya ƙara tattaɓa akwatinsa tare da cewa
Il tâte la caisse une fois de plus en se disant :

Ladan: Akwati cike da kuɗi. Jamma'a !
Le Muezzin : Une cantine pleine d'argent. Voyons!

Ladan ya sake fashewa da dariya. Wata alamar samata ce ta katse masa dariyar. Sai cewa ya yi :
Il éclate de rire de nouveau. Un de bruit l'interrompt et il dit :

Ladan : cewa nikai salamata ce...

Le Muezzin : J'ai cru entendre un bruit…

Ya tashi sannu ya leƙa cikin kwarkwaɗar ƙofar da ma ba kowa a cikinta. Ya dawo wurin akwatin. Bayan ya ƙare murna, sai ya ci gaba.

Il se lève doucement et regarde à travers le couloir où rien ne se dessine. Il revint vers sa caisse. Après cette réjouissance, il décide en fin de l'ouvrir :

Ladan: Allah Sarki! Barin in buɗa in ga abuna!

Le Muezzin : Gloire à Allah ! A présent je vais ouvrir la cantine pour voir ma fortune !

Da ya kasa buɗe akwatin sai ya ce :
N'arrivant pas ouvrir la caisse, il se dit :

Ladan: Ai ba tsintuwar ba… abinda mutum bai saba ba.

Le Muezzin : ramasser une cantine est une chose, l'ouvrir en est une autre !

Ya duba ko'ina ba tare da gano wurin da ake buɗa akwatin ba. Sai ya ci gaba da maganarshi shi kaɗai :
Il vérifie partout sans pouvoir identifier l'ouverture de la caisse. Il continue son monologue :

Ladan : A'a, Allah waddan abinda ba ka saba ba da shi.

Le Muezzin : Ah ! C'est vraiment mauvais d'être ignorant !

Can, sai ya ga wata alama alama ; sai ya ce :
Il découvre l'ouverture et il dit :

Ladan : A'a, ko nan ne dabon yake ; kai ! Asshe nan dai ne.

Le Muezzin : Ah, peut être que c'est ici l'ouverture. C'est bien là !

Yana bubbuɗawa, yana cewa :
Il chatoie la cantine en disant :

Ladan : Ee, nan ne. Wannan safiya ta yau, da kyau take ! Mutum ya je masallaci. Kurum, ya tarar da akwati cike da kuɗi! Har yana amai! Kai, wanda ya kai wannan sadaka masallaci, Ubangiji Allah ya yi mishi albarka!

Le Muezzin : oui, c'est bien là. La matinée d'aujourd'hui est remplie de bonheur ! Je viens à la mosquée et j'y trouve une cantine pleine d'argent ! Une cantine pleine à craquer ! Qu'Allah bénisse celui qui a amené cette aumône à la mosquée !

Bayan wani ƙarin ƙoƙari, can ya samu ya buɗa akwatin. Abin mamaki, mutum ne a mace ya taras. Ya kasa iya haƙuri da abin da ya gani sai ya fashe da kuka, yana faɗin :

Après des efforts supplémentaires, il parvient à ouvrir la caisse. A sa grande surprise il y voit un corps sans vie. Ne pouvant pas supporter ce qu'il voit, il se met à pleurer en disant :

Ladan : yau mi zan gani !

Le Muezzin : Aujourd'hui que vais-je devenir !

Ya taso ya ƙara dubawa sai yana kuka yana faɗin *:*
Il regarde une fois encore le cadavre et reprend ses pleurs en disant :

Ladan: Ashe mutum ne a mace a ciki! Da ma na san ni, ina ni ina arziki ! Kawai yanzu mutane, dan ƙeta sai ku kashe mutum ku kai ku aje a masalaci ! Ladancin da nikai shi ma ya kai a yi kyashi ? An tsane ni ! Allah tsine maka albarka, kai ma da ke ciki, shege !

Le Muezzin : C'est un corps sans vie dans la cantine ! Je le savais, un muezzin ne peut jamais être riche ! Les gens sont vraiment méchants, sinon comment est-ce possible de tuer un être humain et piéger des gens avec ? Que vaut la fonction de muezzin pour être convoitée ? Les gens ne m'aiment pas pour cela ! Qu'Allah te maudisse, toi qui es dans cette cantine ! Imbécile !

Da ya tabbatar da abinda yake gani, sai ya ƙara fashewa da kuka. « Ya fara surutai yana raki yana cewa :
Convaincu que l'homme est bel et bien mort, il se remet à pleurer en disant :

Ladan : Yanzu ina za ni yi ? Sarki kuma ya ce ka da a sabke baƙo ! Kuma mutum ga shi da matacce a cikin gida. Ina za ni shiga ? Kai ni Ladan, na mutu !

Le Muezzin : Que faire ? Le roi a interdit d'héberger des étrangers ! Pire, je me retrouve avec un cadavre chez moi ! Qu'est-ce que je vais devenir ? Je suis perdu, moi Le muezzin !

Ya ƙara shan kuka. Sa'annan ya nemi ya kira Tanungo :
Il continue à pleurer. Il appelle son épouse Tanoungo

Ladan: To yanzu ina za ni shiga? Tanungo !

Le Muezzin : Qu'est-ce que je dois faire ? Tanoungo !

Ya ji shiru, sai ya tuna cewa ya kore ta ; sai cewa ya yi :
Quand personne ne lui répond, il se rappelle qu'il a répudié sa femme :

Ladan : Asshe na kore ta !

Le Muezzin : Ou lala ! je l'ai répudiée !

Ya ci gaba da surutai kamar haka :
Il continue son monologue :

Ladan : Mutane baƙin ciki, baƙin ciki sai ya kashe ku ! Tsaya in tashi in tai in maido Tanungo; ta san yadda zamu yi da shi.

Le Muezzin : Les gens sont méchants ! Votre méchanceté va vous tuer ! Je dois aller chercher Tanoungo. Elle saura trouver une solution à ce probleme.

Ya tashi tsaye sai ya dibi akwatin ya ce :

Il se met debout et regarde la cantine en disant :

Ladan : Allah ya isa ! Da wanda ya aje ka a masalaci da kai na ciki duk allah ya isa ! Allah ya ɗebe muku albarka mutanen banza !

Le Muezzin : Qu'Allah punisse celui qui a amené la cantine à la mosquée et toi qui s'y trouve Qu'Allah vous maudisse, bande de voyous !

Ya jima tsaye yana kallo akwatin Sa'annan ya shiga faɗa da mataccen :
Il reste debout à regarder la caisse pendant un certain temps. Puis il se met à gronder le cadavre :

Ladan: Ba ni ɗaukar ka; sai dai in ja ka! Shege! Kana ba ni wahala!

Le Muezzin : Je refuse de te prendre ! Je vais te traîner par terre ! Imbécile ! Tu m'as fait souffrir.

Ya ja shi, yana nanata :
Il traîne le cadavre en répétant :

Ladan : Ni ba ni ɗaukar ka ! Ba ni ɗaukar ka, nicce !

Le Muezzin : Je refuse de te prendre ! Je refuse de te prendre. Je m'en moque !

Ya aje shi ya dawo yana faɗin :
Il laisse la cantine et rebrousse chemin en disant :

Ladan : Mutane cikin gari, ba abinda suka sani sai baƙin ciki !

Le Muezzin : Dans ce village les gens ne savent que poser des actes ignobles.

Ya ɗauki sandar ladancinsa yana faɗin:
Il prend sa canne en disant :

Ladan: Ɗan ladancin da nike yi ake ƙyashi! Bari in tafi, in nemo Tanungo.

Le Muezzin : C'est à cause de cette minable fonction de muezzin que j'ai des ennemis ! Je vais aller ramener Tanoungo.

Yana cikin wannan, sai ga abokinsa malam Amadu da ya aika neman mata, ya iso cikin fara'a.
En ce moment, son ami Malam Amadou, qui était parti lui demander la main d'une fille pour mariage, arrive tout souriant :

Malam Amadu : Salama alaikum !

Monsieur Amadou : Que la paix d'Allah soit avec toi !

Ladan : A ina ?

Le Muezzin : Où ça ?

Malam Amadu ya ƙara yin sallama.
Monsieur Amadou s'annonce une seconde fois.

Ladan : Amin alaikum masalam !

Le Muezzin : Amen, que la paix d'Allah soit sur toi aussi !

Ladan ya amsa amma cikin damuwa, harma Amadu ya fahinci hakan.
Le Muezzin répond avec souci au point que son ami Amadou s'en rende compte :

Malam Amadu : Yau, Ladan ?

Monsieur Amadou : Qu'y-a-t-il, Ladan ?

Ladan : In ?

Le Muezzin : Comme quoi ?

Malam Amadu : Albishirinka !

Monsieur Amadou : Bonne nouvelle pour toi !

Ladan : Mine ne na Albishir ?

Le Muezzin : Quelle bonne nouvelle ?

Malam Amadu : Uhum, ƙaƙa ina yi maka albishir kana maida albishir ! Auren nan da ka tura ni in nemo ma, yarinyar nan ! An lisafa, an yi komi, an ƙare. Kurum kai ake jira, ka kawo kuɗi a tahi a ɗauro aure.

Monsieur Amadou : Uhum, comment ce fait-il que je t'annonce une bonne nouvelle et tu la récuses ? Ne m'as-tu pas envoyé demander la main d'une fille ? C'est ça la bonne nouvelle car j'ai réussi. On n'attend que toi pour le mariage !

Ladan: To, Malam Amadu, ka haukace; halan?

Le Muezzin : Monsieur Amadou, depuis quand tu es devenu fou ?

Malam Amadu : Da anka yi mi ?

Monsieur Amadou : Pourquoi me poses-tu cette question ?

Ladan : A ina na gane ka har za ni aikin ka. Arme… ?

Le Muezzin : Où est-ce que t'avais-je vu, pour te charger d'une mission ? Mariage… ?

Malam Amadu : A masalaci, ka ba ni jaka guda ; ka ce in je in nemo ma aure ! na je gidan su yarinya ; da darajata da komi ! An ba ni yarinya; an ce in zo in gan ka! Yanzu za ka cewa ba ka san zancen ba !

Monsieur Amadou : N'est-ce pas, à la mosquée où tu m'as remis un billet de mille francs et m'as chargé de te demander la main d'une fille ? Je reviens de chez les parents de la fille. Ils me l'on donnée et tu viens maintenant me signifier que tu as renoncé ? Tu as sali ma réputation auprès de cette famille !

Ladan : La'ilaha'illahu mahama rasulullahi salla lahu alai… amma kai ba ka kumya ! Yo ni a kwana… !

Le Muezzin : Il n'y a d'autres dieux qu'Allah et Mohamed est son messager … ! N'as-tu pas honte ? Moi, même… !

Malam Amadu : Ashe ƙwayan nan da anka ce kana sha ; ashe tsohon banza ne kai !

Monsieur Amadou : Donc les rumeurs sur ta consommation de drogues sont vraies ! Tu es un irresponsable !

Ladan : Kai, ga ka tsohon banza… Ka ga munafuki !

Le Muezzin : C'est toi l'irresponsable ! … Espèce d'hypocrite !

Malam Amadu : Da girmana, da darajata, ka tura ni in tambayo maka yarinya…

Monsieur Amadou : Sans considération pour mon honneur, tu viens de nier que tu m'as envoyé demander la main d'une fille ?

Ladan: Ina ka ga girman? Wa ya ba ka ita?

Le Muezzin : De quel honneur parles-tu ? Qui t'a donné sa fille ?

Malam Amadu : In nemo ma arme, yanzu ka ce a'a ba ka aike ni ba !

Monsieur Amadou : … Je viens de demander la main d'une fille pour toi et tu me dis que tu ne m'as jamais envoyé ?

Ladan : Da ma na ji an ce ku ne shaggun garin nan, Malam Amadou.

Le Muezzin : J'ai appris que tu fais partie des bandits de la cité, Amadou.

Malam Amadu: Kai ne shegen!

Monsieur Amadou : C'est toi le bandit !

Ladan : Wallahi ka lalace !

Le Muezzin : Tu es perverti !

Malam Amadu: Kai ne shegen!

Monsieur Amadou : C'est toi le bandit !

Ladan: Ka ga mutumen baza, kai! Ni a kwana goma ma na gan ka ! Ka ce na aike ka !

Le Muezzin : Espèce de voyou ! Même en dix jours moi je ne t'ai pas vu ! Comment je peux t'envoyer ?

Malam Amadu : ni ?

Monsieur Amadou : Moi ?

Ladan: … Ka tambayo mini arme! Armen wa?

Le Muezzin : Tu m'as demandé une fille en mariage ? Quel mariage ?

Malam Amadu : Tsakani na da kai Allah ya isa !

Monsieur Amadou : Je me confie à Allah pour qu'Il fasse justice.

Ladan : Ni ma, Allah ya isa tsakanina da kai ! Ashe ? Kaɗan ma ka gani !

Le Muezzin : Moi aussi je me confie à Allah pour qu'Il rende justice. Quoi ? Tu n'as rien vu encore !

Ladan ya ciri gorarshi sama tare da nufar Malam Amadu da ita. Amadu ya bada baya ya nana cewa:
Ladan soulève sa canne et la dirige vers Malam Amadou qui qui prend la direction de sortie en répétant :

Malam Amadu: Allah ya isa tsakanina da kai!

Malam Amadou : Qu'Allah rende justice !

Ladan : Ka ga lalataccen banza ! Mutane ?

Le Muezzin : Un vrai perverti ? N'est-ce pas ?

Ladan ya ci gaba da faɗa :
Le muezzin continue à vociférer :

Ladan: Ɗan karen dabo-dabon wohi, kai! Da ma da kake zuwa nan gidan kana leke-leke; duk kai kake gama ni ma da Tanungo! Mutumin banza! Birin wohi, kai! Ka ga lalataccen tsoho, kai!

Le Muezzin : Espèce d'hypocrite ! Tes va-et viens chez moi ont fini par me mettre en confit avec mon épouse ! Espèce de malhonnête ! Vieux singe ! Prostitué !

Tanungo tare da ƴan biko mata biyu suka shigo.
Tanoungo et deux accompagnantes entrent.

Mai biko 1 : A'a, Ladan, ana nan ?

Accompagnante1 : Ah, Ladan ! Vous êtes à la maison ?

Ladan ya amsa masu cikin murna da kuma falgaba :

Le Muezzin leur répond avec un mélange de joie et d'appréhension

Ladan : E, ina nan. Ku wuce ga tabarma nan.

Le Muezzin : Oui, je suis là. Entrez et installez-vous sur la natte que voici :

Mai biko 1 : To.

Médiatrice 2 : D'accord.

Tanungo: Ku wuce.

Tanoungo: Entrez.

Suka zauna su duka uku.
Elles prennent place toutes les trois.

Ladan : Marhabin ! Marabá ; martaba !

Le Muezzin : Soyez les bienvenues. Soyez les bienvenues !

Mai biko 1 : Ina ini ?

Accompagnante1 : Comment allez-vous ?

Ladan : Ah, lafiya lau.

Le Muezzin : Ah, je vais très bien.

Mai biko 2 : Ina ini ?

Accompagnante : Comment allez-vous ?

Ladan : Lafiya lau. Baba lafiyarsu lau, ko ?

Le Muezzin : Je vais très bien. Comment va beau-père ?

Mai biko 2 : Lafiya lau.

Accompagnante2 : Il se porte très bien.

Ladan : To, madalla.

Le muezzin : Rendons gloire à Allah.

Mai biko 2 : Da ma dai, shi ya aiko mu.

Accompagnante 2 : C'est d'ailleurs lui qui nous a envoyé ici.

Ladan ya sosa kai kamar yana mamaki sannan ya ce :
Ladan passe la main sur la tête comme si cela le surprenait et dit

Ladan : Baba, ko ?

Le Muezzin : Beau-père, n'est-ce pas ?

Mai biko 1 : I.

Accompagnate1 : Oui.

Ladan : Ahum ; to.

Le Muezzin : Ahum ; je suis à l'écoute.

Mai biko 1 : Ya ce mu zo mu ji, shi zancen da Tanungo ta gayi ; shin da gaske ne ?

Accompagnante1 : Il nous a instruit de venir nous informer si ce que Tanoungo lui a raconté est vrai.

Kai duƙe, Ladan ya yi musmushi sannan ya ce :
La tête baissée, Ladan sourie et dit :

Ladan : Hum, ikon Allah ! Wani abu ta gayi, halan ?

Le Muezzin : Qu'est-ce qu'elle a raconté ?

Mai biko 1 : Cewa dai ta yi ka sake ta, har kuma sau goma sha biyu !

Accompagnante 1 : Il a dit que tu l'avais divorcée jusqu'à douze fois[7] *!*

Ladan: Wai, wai! Wasa ne dige, baba nike yi mata! Wasa. Yau duk a cikin gidan nan; in ba da Tanungo ba, da wa za ni yi wasa?

Le Muezzin : Quelle incompréhension ! Je plaisantais en réalité. C'était une plaisanterie ! Si ne plaisante pas avec Tanoungo alors avec qui je vais me détendre dans cette maison ?

Tanungo: Ba wasa ba ne wannan!

Tanoungo : On ne plaisante pas de cette façon !

Ladan : Na rantse da Allah, wasa ne. Haba Tanungo !

Le Muezzin : Tanoungo, je jure par Allah que je plaisantais !

Tanungo : Zancen nan da kunka ji na gaya muku da gaskiya ne ! Haka nan ne !

Tanoungo : Ce que je vous avais dit est bien vrai ! C'est la vérité.

Ladan : Cap ; kai ! Shin wai a gidan nan; daga ni sai ke; in ban yi wasa da ita ba; da wa zan yi?

Le Muezzin : Comprenez-moi ! Nous ne sommes que deux dans cette maison ; si ce n'est pas avec elle alors avec qui je plaisanter ?

[7] Pronnoncer un divorce douze fois relève de l'humiliation, la norme religieuse étant trois fois et le couple ne pourra plus se remarier sans que chacun des deux ne se marie avec une tierce personne.

Mai biko 1: To, da wa za ka yi?

Accompagnante : En effet, avec qui ?

Ladan ya ci gaba da ƙoƙarin gamsar da su kamar haka :
Le Muezzin continue à essayer de les convaincre :

Ladan: Uhum, a duba zancen nan mana! Yanzu ni ko… Allah na tuba; wai in sake ki! In na sake ki, to, in zauna da wa? Haba Tanungo!

Le Muezzin : Uhum, faites-moi confiance ! Vraiment, qu'Allah m'accorde Sa clémence ; moi te répudier ! Si je le fais, avec qui je vais vivre ? S'il te plait, Tanoungo ?

Tanungo ta katse mai magana :
Tanoungo l'interrompt :

Tanungo : Ya sake ni ; ya kama hannuna ; ya fidda ni waje ; ya ɗauki kayana ya yi watsi da su !

Tanoungo : Il m'a divorcé, a pris ma main, m'a expulsé de la maison et a jeté mes effets dehors !

Ladan ya kame kai yana cewa:

Ladan tient sa tête, faisant semblant d'être étonné et dit :

Ladan : Kai ! Kai ! A'a !

Le Muezzin : Non ! Non ! Ce n'est pas vrai !

Mai biko 2 : Har da kayan ?

Accompagnante 2 : Il a même jeté tes effets dehors ?

Ladan: Dan Allah a rinƙa faɗin… A rinƙa zance na gaskiya !

Le Muezzin : Au nom d'Allah, il faut dire ce qui s'est réellement passé !

Mai biko 2 : Wannan zance ma a bar shi.

Accompagnante 2 : Arrêtons cette polémique.

Tanungo : Ya ce tun da ya auro ni ko kaji bai taɓa ajewa ba.

Tanoungo : Il a dit que depuis qu'il m'a épousé, il n'a même pas pu s'acheter un poulet.

Mai biko 1 : Haba, ya ce wannan zance a bar shi. Wannan ai daga Allah yake !

Accompagnante1 : Vraiment je vous demande de ne plus en parler. C'est Allah qui rend riche ou pauvre !

Mai biko 2 : Ke, ko ya gaya miki haka ; bar shi da kumyarshi…

Accompagnante 2 : Même si c'est ce qu'il t'a dit, laisse-le avec sa honte…

Ladan: A'a babu ma abin kumya ciki!

Le Muezzin : Non, ce n'est même pas question de honte !

Mai biko 2 : Ladana gare ki. In abin duniya ƙarfi na ; ya je ya ƙwato ma kanshi mana !

Accompagnante 2 : Allah va te récompenser Si la force suffisait pour se faire fortune ; qu'il l'utilise pour s'enrichir !

Mai biko 1: To mu, ko can ma baba bai kama ba. Da ta je ta gayi, ya ce mu zo mu ji. Tunda mun ji, ba gaskiya ba ne, za mu je mu shaida mishi.

Accompagnante 1 : Quoi qu'il en soit, notre père n'est pas d'accord. Quand elle a donné sa version, il nous a demandé de venir vérifier. Nous avons compris que ce n'est pas vrai, nous retournerons le lui dire.

Ladan : Yawwa ; ku ce mishi, ya kwantar da …

Le Muezzin : Voilà qui est bien dit ; dites-lui de ne pas se faire de soucis….

Mai biko 2 : Ai bai kamata ba, wallahi !

Accompagnante 2 : Tout cela est vraiment malheureux !

Ladan : Ni in ba ta son wasan, daga yau ni na bari !

Le Muezzin : Vraiment si elle n'aime pas mes plaisanteries, je les arrête dès maintenant

Mai biko 2 : In ba ka yi wasa da ita ba ; yau da wa za ka yi ?

Accompagnante 2 : Si tu ne plaisantes pas avec elle, alors avec qui tu vas le faire ?

Ladan : Ni ma haka ni gani.

Le Muezzin : C'est la question que je me pose aussi.

Mai biko 2: Cikin gidanka! In mutum bai walwala ba cikin shi; ta ina za ya walwalawa?

Accompagnante 2 : Dans ta propre maison ! Si tu ne peux pas te défouler chez toi, oú est-ce que tu peux le faire ?

Ladan : Daga nan fa sai masallaci !

Le Muezzin : Si je ne suis pas chez moi, je suis à la mosquée !

Mai biko 1: In dai za ka wasa da matarka, ka san wasar da ka kai mata. Ko kaza… ?

Accompagnante 1 : Il faut tout de même savoir plaisanter même avec sa femme ! Cette histoire de poulet….

Mai biko 2 : To !

Accompagnante 2 : Ah oui !

Mai biko 2 : Ke ; ko kaza, ita za ta ba kanta ?

Accompagnante 2 : Même pas un poulet ? N'est-ce pas Allah qui donne ?

Mai biko 1 : To, mu dai za mu tahiya !

Accompagnante 1 : Bon, nous allons partir.

Ladan : Ni dai, wasa ne ni kai. Tunda ba ta son wasar na bari.

Le Muezzin : En tout cas je plaisantais ; mais comme elle n'apprécie pas je n'en ferai plus.

Mai biko 1 : Shekarunku, yau, talatin da uku, duk ba ka ga wani tsegumi ba, sai yanzu da kuka tsufa gele-gele !

Accompagnante 1 : Si vous avez pu passer trente-trois ans ensemble sans aucun problème, ce n'est pas aujourd'hui avec votre âge que vous allez en trouver un !

Ladan ya ci gaba da bada haƙuri.
Le Muezzin continue à les supplier.

Mai biko 1 : To kin gan ni ! *Ta faɗa yayin da ta ɗauki takalmanta ta fita.*

Accompagnante 1 : Je m'en vais ! (Elle prend ses chaussures pour sortir).

Abokiyar tafiyarta ta bi tare da cewa :
Sa coéquipière la suit en disant

Mai biko 2 : A ɗauki haƙuri, mu mun tafi.

Accompagnante 2 : Soyez plus patients, nous prenons congé de vous.

Ladan: To, A gaida min su!

Le Muezzin : Saluez toute la famille de ma part !

Ladan su biyu shi da mai ɗakinshi suka rage. Aka yi shiru na wani lokaci. Can sai Ladan cikin murmushi, ya ce :
Ladan et son épouse seuls. Un silence lourd règne un instant. Puis Ladan sourit et dit :

Ladan *:* Tina (*Ya rage sunan*), ɗan wasan da nike yi miki, shi ne kika je kika ce na kore ki !

Le Muezzin : Tina (diminutif de Tanoungo), ce n'était qu'une plaisanterie ! Tu es allé leur dire que je t'ai répudiée !

Tanungo : Ka kore ni mana !

Tanoungo : Tu m'as bel et bien chassée !

Ya shiga wasa da ita ya sa ta saki jiki da shi.
Il se met à faire des blagues pour décrisper la situation.

Ladan: Haba Tanungogo! Tanungogo, garin na in ban yi wasa ba da ke, duk garin da wa zan yi? Haba huce ranki !

Le Muezzin : Ma Tanoungogo ! Tanoungogo, dans ce village si je ne plaisante pas avec toi ; avec qui voudrais-tu que je plaisante ? S'il te plait laisse passer !

Tanungo : To, na huce.

Tanoungo : D'accord, s'en est fini.

Suka ɣi murmushi su duka biɣu.
Tous les deux sourient.

Ladan : To, tsaya ; Albishirinki !

Le Muezzin : J'ai une bonne nouvelle pour toi !

Tanungo : Goro !

Tanoungo : Qu'elle soit la bienvenue !

Ladan: To, ni wasar ma dan in gwada ki ne. Kya san ba ni da wani abokin arziki in ba ke ba; ko?

Le Muezzin : La plaisanterie c'était pour te tester. Tu sais bien que tu es ma seule vrai amie, n'est-ce pas ?

Ta gɣaƈa kai alamar gamsuwa da abin da ɣake nunawa.
Elle secoue la tête signe d'acceptance de ce qu'il dit.

Ladan : Diba, shekara talatin da uku ai ba kwana talatin da uku ba ne, Tanungo ko ? To da ma rana ce ta arziki, Allah ya kawo ta !

Le Muezzin : Tu sais bien que trente-trois ans, ce n'est pas trente-trois jours, n'est pas Tanoungo ? Au jourd'hui est un jour de bonheur, Allah en a décidé ainsi !

Tanungo: To.

Tanoungo: Je t'écoute.

Ladan: Ai kina kwana da na dawo daga masalaci.

Le Muezzin : Tu dormais quand je suis revenu de la mosquée ; n'est-ce pas ?

Tanungo : E, haka ne.

Tanoungo : Oui, c'est vrai.

Ladan: To, tsintuwa ni yo a can.

Le Muezzin : J'y ai trouvé quelque chose.

Tanungo : Ta mi, Ladan ?

Tanoungo : C'est quoi cette chose, Ladan ?

Ladan: Tanungo, ba akwati cike da kuɗi ba, na tsinto.

Le Muezzin : Tanoungo, c'est une cantine pleine d'argent que j'ai trouvée.

Tanungo: Akwati?

Tanoungo: Une cantine?

Ladan : Cike da kuɗi !

Le Muezzin : Pleine d'argent !

Tanungo: Akwati, Ladan?

Tanoungo: Une cantine, Ladan?

Ladan : Har yana amai !

Le Muezzin : Pleine à craquer !

Ta yi babban lumfashi alamar jin daɗi.
Elle pousse un grand soupir d'allégresse.

Ladan : Jap hum, ai da, so na yi, in ba ki zo ba… ni ce kai Ladan ! Kai Ladan ! Ɗan wasar nan da nike miki, ƙwonda in tai in maida ki mu ci arzikin nan tare.

Le Muezzin : Tu sais j'avais voulu juste t'acheter une bague mais j'ai changé d'avis Comme je blaguais, je me suis dit qu'il serait mieux de te ramener pour qu'on profite de cette fortune ensemble.

Ya tashi yana cewa :
Il se lève en disant :

Ladan : Taso da ma na ce ba ni buɗawa sai a gaban ki. Don ni ba na cuce ki ba duniya da lahira.

Le Muezzin : Viens, j'avais dit que j'allais l'ouvrir en ta présence parce que jamais je ne te trahirai.

Ta tashi ta bishi tana ganin kawai abinda yake gayi gaskiya ne :
Persuadée qu'il lui dit la vérité, elle le suit en disant

Tanungo *:* gaskiya ne, Ladan.

Tanoungo : C'est juste, Ladan.

Ladan : Taho kama min, don yau da kyar na kawo shi gida.

Le Muezzin : Viens m'aider car c'est difficilement que je l'ai amené ici ce matin.

Suka shiga suka fito da akwatin waje.
Ils sortent la caisse d'une chambre.
Ladan : Riƙe ƙwarai. Kada ki sake ya faɗi.

Le Muezzin : Attrape bien. Ne le laisse pas tomber.

Tanungo: A'a, ban yarda. Dukiyar tamu!

Tanoungo : Non, je ne lâcherai pas prise. C'est notre fortune !

Ladan : Na ce miki… Kawo shi nan. Aje. Wannan abu ne Allah ya ba mu.

Le Muezzin : Je te dis de l'amener ici. Dépose. Ça c'est un cadeau d'Allah.

Tanungo: Ladan!

Tanoungo: Ladan!

Ladan: Ke gani ko!

Le Muezzin : Tu as vu !

Tanungo : Ladan ; ni tunda nike ban taɓa ganin …

Tanoungo : Ladan, moi je n'ai jamais vu …

Ladan : Mai girma irin wannan, ko ?

Le Muezzin : Aussi grande que celle-ci ; n'est-pas ?

Tanungo: Mai girma irin wannan. Ah, wanga akwati !

Tanoungo : Aussi grande que celle-là. Ah, quelle cantine !

Ladan : Cewa ni yi, ba ni buɗawa. Yanzu zamna mu yi shawara.

Le Muezzin : Je m'étais dit que je n'allais pas l'ouvrir seul. Maintenant assois toi, nous allons décider ensemble

Suka zauna su duka bisan akwatin. Sannan suka ci gaba da shawara.
Ils s'asseyent tous les deux sur la cantine et continuent à se concerter.

Ladan : Kin ga dai ; arziki ne ga shi mun samu.

Le Muezzin : Comme tu peux le voir, nous avons eu de la fortune.

Tanungo : Ƙwarai kuwa !

Tanoungo : Effectivement !

Ladan : Yanzu ke ; mine ne burinki a duniya ?

Le Muezzin : Quelles sont des besoins dans la vie ?

Tanungo: Ni gurina a duniya?

Tanoungo : Mes besoins dans la vie ?

Ladan : Uhum.

Le Muezzin : Uhum.

Cikin farin ciki ta shiga zaɣɣana abubuwan da take so.
Avec joie elle commence à dresser la liste de ses besoins.

Tanungo: Zinare da awarwaron zinare da sarƙar da ɣankunne.

Tanoungo : L'or, des bracelets en or, une chaîne et des boucles d'oreilles en or.

Ladan: Duka wannan kin samu. Duka wannan kin samu. Kuma hwa?

Le Muezzin : Considère que tu as déjà acquis tout cela. Considère que tu as déjà acquis tout cela. De quoi d'autres as-tu besoin ?

Tanungo : Da "grand boubou" kala- kala.

Tanoungo : De grands boubous de styles différents

Ladan : Wacce ce "grand boubou" ?

Le Muezzin : Qu'appelles-tu « grand boubou » ?

Tanungo : Wannan irin tamu ta mata, wadda ake yi.

Tanoungo : Le grand boubou là que portent les femmes.

Ladan : Gari-garin nan da kuke yi ?

Le Muezzin : Cette redingote façon là ?

Tanungo : E ; e.

Tanoungo : Oui, oui.

Ladan : Yo, wannan duk ma ba kaɗan ne ba. Diba hwa abin nan duk kuɗi ne !

Le Muezzin : Je vois. Mais tout cela n'est rien du tout. Il faut bien voir ce que cette cantine est pleine d'argent !

Tanungo: To, kuma da gado.

Tanoungo : J'ai aussi besoin d'un lit.

Ladan : AP ! Ce gadaje !

Le Muezzin : Ah ! Dis plutôt plusieurs lits !

Tanungo : Gadaje ?

Tanoungo: Plusieurs lits?

Ladan: Yo! To kya yi mantuwa! Sai mun tai gabas !

Le Muezzin : Pourquoi pas ? Et puis tu as fait un grand oubli ! Nous irons au pèlerinage !

Ya yi kwance da dariya, sai ya idasa da kiran ta : Tanungo !
Il s'éclate de rire et finit par appeler Tanoungo !

Ta yi dariya, ta taɓa ; sannan ta ce :
Elle rit, applaudit et dit :

Tanungo: Allah ya kai Ladan! Allah ya kai Ladan!

Tanoungo: Amen Ladan! Amen Ladan !

Ladan : Ni kau, ke ga wannan doki iri na biyamaradi. Farin wannan. Da ma sai da na yi mafarkin na sai farin doki.

Le Muezzin : Quant à moi ; tu connais le cheval du Prince ? Son cheval blanc. J'ai même rêvé avoir acheté un cheval blanc.

Tanungo: To, Allah ya sa!

Tanoungo: Alors, Amen!

Ladan: Sai na zuba mishi kaya sosai in yi ta bin garin nan; in yi ta yin sukkuya; ina zagaya kowa na gani. A ce kun ga Ladan. Kun ga arziki.

Le Muezzin : Je vais le harnacher correctement, ensuite trotter dans le village. Puis je vais galoper en toute vitesse devant tout le village pour qu'on dise « as-tu vu Ladan ? » « Tu as vu ce que l'argent peut accomplir ? »

Tanungo : To.

Tanoungo : D'accord.

Ladan : E.

Le Muezzin : Oui.

Ladan: To yanzu sai mu buɗa mu ga ko wane irin kaɗì ne ciki.

Le Muezzin : Maintenant, nous allons ouvrir et voir ce qu'il y a à l'intérieur.

Suka tashi daga kan akwatin don su buda su ga abinda ke cikinta.

Ils se lèvent tous les deux pour ouvrir la cantine et voir ce qu'elle contient.

Ladan : Ke, kya fi ni dabara ! Ta ina ake buƈa wannan abu dai?

Le muezzin : Toi tu es plus stratège que moi ! Par où ouvre-t-on ce truc ?

Suka shiga neman mabuƈin akwatin.
Ils se mettent à chercher comment ouvrir la cantine.

Ladan: Ni kin san, abin da ba ka saba ba da shi.

Le muezzin : Tu me connais, je ne suis pas familier avec ces choses-là !

Tanungo: Abin ma ko ina ne ake buƈe shi Ladan?

Tanoungo : Cette chose par où peut-on l'ouvrir, Ladan ?

Ladan : Anya ba nan ne ba ?

Le muezzin : Est-ce que ce n'est pas ici ?

Asshe nan ne. Akwatin ta fara alamar buƈewa.
C'est bien l'endroit t La caisse commencer à s'ouvrir.

Tanungo: To, tsaya mu gani.

Tanoungo : Bon, attends on va voir.

Ladan : Ke gani ; na gaya miki !

Le Muezzin : Tu as vu. Je te l'ai dit !

Tanungo : Ɗaga Ladan. Ɗaga mana!

Tanoungo: Ouvre Ladan. Ouvre-la vite !

Ladan : Ap ; Kama mu gani.

Le Muezzin : Sans problème ! Aide-moi.

Tanungo : Uhum.

Tanungo : Uhum.

Da akwati ta buƈu, dubawar ga da sukai, maimakon kuƈi, sai suka ga mutum a mace.
Ladan ya faƈi ya suma, ita kau Tanungo ta yi kara yanan ta rufe akwatin da sarmi :
Quand la cantine est enfin ouverte, au lieu de voir de l'argent ils y trouvent un homme mort. Liman tombe en syncope alors que Tanungo s'exclame en laissant la cantine se refermer.

Tanungo: To; mine ne wannan Ladan! Soubahanallah ! Mine ne wannan Ladan ?

Tanoungo : Mais, qu'est-ce que c'est que ça, Ladan ? Que Dieu nous en garde ! Qu'est-ce que c'est que ça, Ladan ?

Ladan ɣa faƈi ɣana ta kiran sunan Allah.

Le muezzin s'effondre en invoquant les noms d'Allah.

Tanungo : Da ma saboda wannan na ka je ka maido ni Ladan ?

Tanoungo : C'est donc pour cela que tu m'as ramené ?

Ladan: Tsaya tukwan, gabana ya faƈi.

Le Muezzin : Attends un instant, je suis désemparé.

Tanungo : Ya faƈin mi. Da gangan.

Tanoungo : Comment désemparé ? Tu l'as fait exprès

Ladan : Ba da gangam ba ne.

Le Muezzin : Je ne l'ai pas fait exprès.

Tanungo : Ka sani sarai Ladan.

Tanungo : Tu savais ce qu'il ɣ a dans la cantine, Ladan.

Ladan: Na rantse miki ban sani ba!

Le Muezzin : Je te le jure, je ne le savais pas !

Tanungo : Ka sani !

Tanoungo : Tu le savais !

Ladan : Na ratse miki, ni ce miki, ban sani ba. Mine ne ke ciki Tanungo ?

Le Muezzin : Je te le jure, je ne savais pas ce qu'il ɣ a dedans. Qu'est-ce qu'il ɣ a dedans, Tanoungo ?

Tanungo : Wani hida hida ne a ciki.

Tanoungo : C'est quelque chose de grand qu'il ɣa dedans.

Ladan: Buƈa kaƈan in gani.

Le Muezzin : Ouvre de nouveau je vais voir.

Ta ƙara buɓawa.

Elle ouvre une seconde fois :

Tanungo : Subanallahi, Ladan.

Tanoungo : Que Dieu en garde, Ladan !

Ladan: Allahu Akbar! A, ni Ladan na shiga uku.

Le Muezzin : Allah est grand ! Moi le Muezzin je suis dans des problèmes.

Tanungo : Ka shiga uku, ko ni dai na shiga uku, Ladan ; ni da na komo.

Tanoungo : Tu es dans des problèmes Ladan, ou bien c'est moi qui suis dans des problèmes après mon retour ?

Ladan: Ke da ki ka komo?

Le Muezzin : Toi qui es revenue ?

Tanungo : I.

Tanoungo : Oui.

Ladan : Yau ; ni ba cewa nikai kuɗi na ba ne. Abin da ban buɗa ba, na gani.

Le muezzin : Vraiment je pensais que c'était de l'argent. Je ne l'avais pas ouverte.

Tanungo: Ka san da haka nan; ka zo, ka nemo ni.

Tanoungo : Tu le savais bien quand tu es allé me ramener.

Ladan: A'a. To, ai ke tuna mini, babu zama.

Le muezzin : Non, non ; d'ailleurs tu viens de ma rappeler que je dois faire quelque chose !

Ya shiga kuka kuma yana magana:
Il commence à pleurer en monologuant :

Ladan : Za ni barin garin. Ga shi sarki ya yi doka, ya ce duk wanda aka tarar da baƙo gidanshi zai yanke mishi wuya.

Le Muezzin : Je dois quitter la cité. Le roi a interdit d'héberger un étranger sous peine d'être décapité

Ladan: Wannan lalataccen Malam Amadu ya ramta mini dala biyar wadda na sayo daudawa ran nan.

Le muezzin : Malam Amadou ma prêté cinq francs avec lesquels j'ai acheté du soumbala (une épice pour assaisonner une sauce).

Tanungo: To.

Tanoungo: D'accord.

Ladan: Malam Sanusi ma, ko dala goma ce yake bi na.

Le Muezzin : Je dois aussi dix francs à Malam Sanoussi.

Tanungo: To.

Tanoungo: D'accord.

Ladan: Ki yi ƙoƙari ko zane ki saida ki biya su. Don kar ace na gudu da bashi.

Le Muezzin : Fais tout pour leur rembourser leur argent ; pour qu'on ne dise pas que j'ai fui avec l'argent d'autrui.

Tanungo: To.

Tanungo: D'accord.

Ladan: In bar garin.

Le Muezzin : Je vais quitter la cité.

Ladan ya kama hanya ; matar ta maido shi da kira.
Le Muezzin se dirige vers la sortie de sa maison quand sa femme le fait revenir.

Tanungo: Yaka Ladan.

Tanoungo: Viens Ladan.

Ladan : Uhum.

Le Muezzin : Uhum.

Tanungo: Zo, in koya maka dabararmu ta mata.

Tanungo : Viens je vais t'apprendre notre manœuvre de femmes.

Ladan : Dubara ?

Le Muezzin : Manœuvre ?

Tanungo : I !

Tanoungo : Oui !

Ladan : Ana yi ma matacce dubara ?

Le Muezzin : Quelle manœuvre peut-on faire avec un cadavre ?

Tanungo: Ana iya yi mishi. Wadda za mu samu mu futa.

Tanoungo : On peut en trouver une qui va nous sortir de cette situation.

Cikin kuka-kuka Ladan ya amince.
Le Muezzin accepte en pleurnichant.

Ladan: To, ke nike saurare.

Le Muezzin : Bon, je t'écoute.

Tanungo: A ina ka ɗauko akwatin?

Tanoungo : Où est-ce que tu as trouvé la cantine ?

Ladan: Yau a ina ko zan ɗauko? A masalaci mana.

Le Muezzin : Où est-ce que je pourrais la trouver si ce n'est à la mosquée ?

Tanungo: Ina rigar wannan taka?

Tanoungo : Où est boubou là ?

Ladan : Wacce ?

Le Muezzin : Lequel ?

Tanungo: "grand boubou" taka.

Tanoungo: Ton grand boubou.

Ladan: Wadda kika saya mini kwanan nan?

Le Muezzin : Celui que tu m'as acheté récemment ?

Tanoungo: E.

Tanungo: Oui.

Ladan: Tana nan rataye.

Le Muezzin : Il est là accroché.

Tanungo : Yadda ka ɗauko shi da jikar nan, a kawo rigar nan a lullubɓa mishi, a fiddo ɗan bakin nan ciki ; wanda ya zo ɗauka shi ma ya ɗauka haka nan.

Tanoungo : De la même manière que tu l'as trouvé, avec le billet là accroché, nous allons mettre ce boubou-là à l'intérieur en laissant apparaitre un pan à l'extérieur. Comme cela quelqu'un va voir et prendre aussi !

Ladan : Yo ina za mu kai shi ?

Le Muezzin : Alors où-est-ce que nous allons l'amené. ?

Tanungo: Masalacimana!

Tanoungo: A la mosquée!

Ladan: To shiga ta ɗauko rigar.

Le Muezzin : D'accord va prendre le boubou.

Shi kuwa yana nan yana kai-kawo da gorarshi a hannu, fuska a murtuƙe. Ta dawo, suka buɗa akwatin, suka lulluɓa wa gawar ita, sannan suka fiddo ɣar jelar waje; don wani ya ɗauka cewa wasu kaya ne masu daraja suke ciki. Da suka gama, suka maryar da ita masalaci.
Pendant ce temps Ladan, le visage crispé, faisait des vas-et-viens muni de sa canne. Sa femme revint avec le boubou qu'ils placent dans la cantine en laissant un pan du boubou à découvert. Ils la retournent à la mosquée.

Ladan : Ɗora mini, in je.

Le Muezzin : Place-la sur la tête.

Tanungo : Kama dai mu tahi.

Tanoungo : Tiens un côté, nous irons ensemble.

Ladan : Asshe !

Le Muezzin : Est-ce vraiment nécessaire ?

Tanungo : I.

Tanoungo : Oui.

Ladan : To in mun kai ƙofar gida ki aza mini ita don in kai ta masalaci ni ɗai.

Le Muezzin : Bon arrivé à la porte tu me la place sur la tête pour que j'aille seul à la mosquée.

Tanungo: Ina aza ma. In mun kai ƙofar gida ina aza maka. To mu je.

Tanoungo : Sans problème. Arrivé à la porte je vais te la placer sur la tête. Allons-ɣ.

Ladan : Wanda ya yi muna wannan, Tanungo ce mishi : « Allah-ya-isa ».

Le Muezzin : Tanoungo, dis à celui qui nous a joué ce tour : « Allah va rendre justice ».

Tanungo : Allah ya isa !

Tanoungo : Qu'Allah nous rende justice !

Ladan : Yawwa.

Le Muezzin : Très bien.

Tanungo : Allah ya isa !

Tanoungo : Qu'Allah nous rende justice !

Suka je tare suka kai shi masalaci, kamar ɣadda suka tsara.

Can sai Liman ya shigo yana hailala.
Les deux ramènent la cantine à la mosquée comme prévu.
Peu après l'Imam arrive à la mosquée.

Liman : la'ilha illallahi ! la'ilha illallahi !

Le marabout qui dirige la prière : Il n'y a de Dieu qu'Allah ! Il n'y a de Dieu qu'Allah !

Ganin akwati da ya yi shi ne ya katse shi yin hailala. Da farko ya ɗauka ko mutum ne, har sa kira.

L'irruption de la cantine dans son champ visuel lui fait arrêter ses invocations. Au début, la cantine ressemblait à une personne.

Liman : Kai wane ne a masalaci ?

L'Imam : Hé, qui est dans la mosquée ?

Ya ɗauka ko malam Umaru ne. Ya kira shi.
Il songe à Malam Umaru et l'appelle.

Liman : Malam Umaru ?

L'Imam : Monsieur Oumarou ?

Da ya ji shiru sai ya ƙara kusa don ya ƙwanƙwance abin da yake gani. Sai ko ya gane ba mutum ba ne.
Quand il n'a pas eu de réponse, il s'approche davantage de la mosquée pour mieux voir et réalise que ce n'est pas un être humain.

Liman : Kap, kai, ai ba mutum ba ne ! Me nike shirin gani?

L'Iman: Ah! Ce n'est pas une personne ! Qu'est-ce que c'est ?

Da ya matso kusa sai ya ga akwati ne tsike da tufafi.
Quand il s'approche de la cantine il réalise qu'elle est une pleine des vêtements.

Liman : Akwati ? Kai, Wannan launi ne ? Cike da kuɗi ? *(Ya kyakkewaya yana magana)* La ilaha illallahu ! Allah sarkin baiwa! Allah na gode ma! Ladan, babu rabo a jikinshi. Yanzu wannan; in ba ni ba. Da ma na san rohonin nan da nike jn wuridinsu: su Tattara ya'idu, Gangama ya'idu duk kap, na san banna taɓewa.

L'Imam : Cantine ? Ça c'est quelle couleur ? Une cantine pleine d'argent ? (Il fait le tour de la cantine) Allah est grand ! Allah le Miséricordieux. Je Te remercie, Allah ! Le Muezzin n'a vraiment pas de chance de devenir riche ! Il n'y a que moi pour avoir une telle chance ! Je le sais avec tous les génies tels que Tattara Yai'idou, Gamgama Ya'idou, Gafat-Gafat que j'invoque chaque fois ! ... je sais que je serai récompense.

Ya fashe da dariya ya ci gaba da yi wa Allah godiya.
Il éclate de rire en continuant à remercier Allah

Liman : Alhamdu lillahi rabil alamina. Fatiya, Amin, Allah na gode ma. Na gode ma aihuwa kiyaye da kakanni !

L'Imam : Je remercie Allah. Invocation. Je remercie les parents et les ancêtres !

Ya ƙara tintsirewa da dariya. Ha ! Ha ! Ha ! *Ya taɓa hannuwa ; sannan ya zauna kan akwatin. Ya kama hannun rigar, ya rawaya.*
Il rit une fois de plus en applaudissant. Il s'assoit sur la cantine et prend le pan du boubou pour l'apprécier davantage.

Liman: *(Ya ci gaba da Magana)* Wannan riguna jibga- jibga, in na same su…Ɗauka zani yi in kai abuna gida! Allah na gode ma !

Limam : (Il continue à parler) Tous ces grands boubous sont donc à moi ! Bien, ma chère cantine je vais te prendre et t'amener chez moi ! Je remercie Allah !

Liman : Yaya zan yi ? Bari ka gani… ! *(Ya tashi tsaye ya ɗauki niyyar kai akwatinsa gida) :* Ha ! Hum! (*Ya ɗora a bayansa yana faɗin*) Allahu Akbar! Allahu Akbar!

Limam : Comment faire ? Attends tu vas voir ! (Il s'arc-boute pour prendre la continue)
Ha ! Hum ! (Il la porte sur son dos en disant) : Allah est grand ! Allah est grand!

Liman: To, akwatina. In kai abina gida.

L'Imam : Ma cantine. Je l'amène à la maison.

Ya shirya ya yunƙura, ya ɗauka. Bai iyawa. Akwatin ga nauyi Ya yi, ya yi da kyar ya samu ya ɗauka ya kai gida. Kafin ya dawo, masalaci ya haɗe. Can ya shigo tare da rakiya ɗan almajiri ɗauke da wani ƙumshi. Ana iya fara salla. Liman cikin murmushi, ya jagoranci sallar. Cikin matuƙar sauri, yana yi, yana murmushi. In ya duƙa, kafin sauran su duƙa har ya taso. Haka yake yi, ɗan lokaci kaɗan ya gama salla. Ya juyo mabiyansa ya yi adu'a ; suka shafa gaba ɗayansu. Sa'annan suka gama hannun wasu wajen gaisuwa. Sauran masallatan suka tashi za su fita sai liman ya ce su dakata. Suka dakata.

Il se prépare et essaie de prendre la cantine. Il ne parvient pas. La cantine est très lourde. Il essaie et essaie, difficilement il l'amène à la maison. Avant son retour la mosquée est pleine de fidèles Il arrive accompagné de son disciple qui tient un colis contenant des habits. La prière commence. L'Imam, très ému, dirige cette prière en souriant et avec un rythme rapide au point que les fidèles ont du mal à le suivre. A la fin de la prière, il se tourne vers les fidèles et fait la traditionnelle invocation. Après les invocations L'imam fait attendre les fidèles.

Liman : Ɗan almajiri !

L'Imam: Talibé!

Ɗan Almajiri: Na'am.

Le Talibé : Oui.

Liman : Kawo min kayan wannan.

L'Imam : Donne-moi ces habits-là.

Ɗan Almajiri ya kawo mai kayan.
Le talibé lui amène les habits.

Liman: Eee kun san da can, zamanin iyaye da kakanni…

L'Imam : Eh vous savez que depuis des générations, …

Jamma'a : Uhum !

Les fidèles : Uhum !

Liman : Akwai abinda muka gada muke yi, na gida. Lokaci bai yi ba; to, amma bana lokaci ya yi.

L'Imam : Il est de notre tradition de faire certains gestes que je n'ai pas pu faire avant. Cette année les conditions pour faire ces gestes sont réunies.

Jamma'a : To, madalla !

Les fidèles : Donc c'est bien !

Liman: A cikin shi duk zan gama ku da kyautar!

L'Imam : Je vous donner des cadeaux !

Jamma'a, wasu na cewa madalla*, wasu na cewa* haka ake so, *wasun kuwa na* in ana zama tare ; *sai masu cewa* ba dan iyaye da kakanni ba, ai da a gada ba. *Shi Ladan, bai ce komi ba. Yana dai kallon Liman.*

Les gens interviennent, qui pour dire c'est bien ; qui pour dire que c'est ce qu'il faut quand on vit en ensemble. D'autres disent qu'on doit tout aux ancêtres. Ladan, lui, ne dit rien. Il se contente de les regarder.

Liman : Allah ya yarda. Alhamdu lillahi ! Haba, Ɗan almajiri !

L'Imam : Allah a été miséricordieux ! Merci Allah ! Talibé !

Ya buɗa ƙumshi, ya fara rabon kaya.
Il ouvre le colis et commence à distribuer des habits.

Liman: Ɗan almajiri, kai amshi wannan.

L'Imam : Talibé, prend celui-ci.

Ɗan almajiri : Ahan.

Le Talibé : D'accord.

Limam : E ; riƙe wannan ; ka sa.

L'Imam : Oui ; prends ceci ; tu peux t'en servir.

Ɗan almajiri ya amsa yana cewa:
Le Talibé prend en disant :

Dan Almajiri: To, na gode.

Le Talibé : Merci.

Liman : E. Malam Ɗayabu ?

L'Imam : Eh, Monsieur Ɗayabou ?

Malam Ɗayyabu : E !

Monsieur Daya Bou : Oui !

Liman : Kai ma wannan taka ce.

L'Imam : Toi aussi, ça c'est pour toi.

Malam Ɗayyabu : Ni ma na gode.

Monsieur Ɗayabu : Moi aussi je dis merci.

Liman : Ehen, madalla !

L'Imam : Eh, bien !

Malam Ɗayyabu : Allah ya yi ma albarka.

Monsieur Dayyabou : Puisse Allah te bénir.

Da Liman ya kawo ga Ladan sai ya tsallake shi ya je ga na gaba.
Arrivé au niveau de Ladan l'Imam le saute et poursuit avec le suivant.

Liman : Malam Abdu, kai wannan da wandon da rigar duk riƙe. Naka ne.

L'Imam : Monsieur Abdou, prend cet ensemble, c'est à toi !

Shi kuwa yana ɗaya ɓangaren yana ta cewa akaramakallah. Yana faɗa yana ƙarawa. Ya amsa ya, yi godiya.

Lui (monsieur Abdou) se trouvant à l'écart répète qu'Allah bénisse l'Imam Il prend le cadeau et remercie de nouveau le donateur.

Liman: To madalla. Malam Zanaidou…

L'Imam : Eh bien. Monsieur Zanaidou…

Shi maa ya amsa yana cewa madalla:
Lui également, il prend sa part en disant :

Malam Zanaidou : Madalla. Masha Allah. Alhamdu lillahi.

Monsieur Zanaidou : C'est bien, c'est bien ça ; c'est la volonté d'Allah. Gloire à Allah.

Sauran Massalata daga mai cewa Allah ya sa albarka*, sai mai cewa* amin*. Shi dai Ladan kar yake kallon su, da yake ya san abinda ake ciki.*
Certains parmi les fidèles disent « qu'Allah le bénisse *» et d'autres dirent « Amin » Le Muezzin ne dit rien car in connait ce qu'il ya dans la cantine.*

Liman : Malam Mumuni, kai rike wannan. *(Ya ba shi wata babbar riga.)*

L'Imam : Monsieur Moumouni, tiens ça c'est pour toi. (Il lui remet un grand boubou.)

Malam Mumuni ya amsa ya yi godiya. Sannan ya ce :
Malam Moumouni prend le cadeau et remercie le donateur :

Malam Mumuni : Allah ya gwada muna baɗi warhaka*. Sauran masalata suka ce* « amin ! »*.*

Monsieur Moumouni : Qu'Allah nous fasse vivre jusqu'à l'année prochaine Les autres fidèles répondent « Amen ! *»*

Liman : Malam Bala, riƙe wannan.

L'Imam : Monsieur Bala, tiens ça.

Shi ma ya amsa, ya yi godiya. Daga shi kaya suka ƙare ; sai ɗan ƙyalle rawani ya yi saura. Bala prend le cadeau et remercie le donateur. Avec lui les cadeaux sont finis, sauf un petit turban.

Liman: Kai Ladan! Sai wannan!

L'Imam : Hei Ladan ! Il ne reste plus que petit turban !

Ladan : Ba komi.

Le Muezzin : Ce n'est pas grave !

Liman: Ɗan almajiri, ai ya ishe shi, ko?

L'Imam : Talibé Ce petit turban lui convient, n'est-ce pas ?

Ɗan almajiri : Allah ya sa Albarka. *(Sauran suka ce amin)*

Le Talibé : Puisse Allah le bénir ! (Le reste des fidèles disent Amen !)

Ya miƙa ma Ladan, a walakance. Shi kuwa, ya amsa yai yi godiya, sannan ya ɗauki magana.
Il tend le turban à Ladan avec mépris. Ce dernier le remercie avant de prendre la parole.

Ladan : Jamma'a !

Le Muezzin : Messieurs !

Jamma'a : Na'am !

Les fidèles : Oui !

Ladan : Kun sa wanga abu, ai mai kyau ne ; ko ?

Le Muezzin : Ce que l'Iman a fait est acte salutaire, n'est-ce pas ?

Jamma'a : E, haba ; sosai kuwa !

Les fidèles : Oui bien sûr !

Ladan: Ina so a yiwa Liman fatiya wannan rabo da ya yi, Ubangiji, Allah kiyashe shi da maƙiya.

Le Muezzin : Je voudrais que nous priions Allah pour qu'il le préserve de tout mauvais sort.

Jama'a : Amin !

Les fidèles : Amen !

Suka yi adu'a. Suka shafa. Yayin da ake yin wannan Liman ya maida ma Ladan martini ; yana cewa :

Ils font des invocations. En ce meme moment l'Imam réagit aux propos du Muezzin en disant :

Liman : Mu katari sai na alheri, E, sai na alheri !

L'Imam : Nous le destin ne nous réserve que le bonheur !

Ladan : Allah ya kiyaye !

Le Muezzin : Qu'Allah nous protège !

Liman : Mu Allah ya kiyaye !

L'Imam : Allah nous a déjà protégé !

Jama'a : To !

Les fidèles : D'accord !

Liman: Allah ya riga... E!

L'Imam : Allah a déjà… Oui !

Suka tashi. Kowa ya yi gidansa.
Liman ne ya fara fita tare da cewa :
Ils se lèvent et rentrent chez eux.
L'Imam sort en premier en disant

Liman : Ni za ni gida (*cikin zumuɗi*)

L'Imam : Moi je rentre à la maison (tout ému).

Liman ya je gida.
L'Imam arrive chez lui.

Liman: *(Yana magana shi kaɗai)* To, Alhamdu lillahi. Na gode Allah. Na ƙare rabo. Kuma bari mu zo ; mu jingine sanda kuma, mu shiga mu gani.

L'Imam (monologuant) : Gloire à Allah. Le miséricordieux. J'ai fini le partage. Maintenant, je dépose ma canne et je vais ouvrir la cantine.

Ya yi wurin akwati, kuma ya dawo, tare da cewa:
Il se dirige vers la cantine mais vérifie d'abord s'il n'ya personne dans la maison, en disant :

Liman: Bari in leƙa ko ba kowa cikin gida! (Ba kowa.) To, bari in jawo akwatin nan nawa in ga abin da ke ciki.

L'Imam : Voyons d'abord s'il n'y a personne dans la maison ! (Il n'y a personne). Voyons ce qu'il y a dans ma cantine

Liman : (Yana magana shi kaɗai) Wai, Allah alhamdu lillahi. Madalla ! Wayyo, Allana ! Ni Liman, na gode ma aifuwar uwaye. Na gode ma Allah ! Na gode ma Annabi !

L'Imam : (Il monologue) Ah Gloire à Allah ! Moi l'Imam, je remercie Allah et mes ancêtres ! Je remercie également le Prophète de l'Islam !

Liman :(Ya ci gaba magana shi kaɗai) Wannan sanduƙi cike da kuɗi ! Ladan matsiyaci, kai ya kamata ka riga kowa… Allah bai yi ba zai yi arziki.

L'Imam : (Il continue son monologue) Toute une cantine pleine d'argent ! Ladan (le Muezzin), c'est toi qui aurais pu la trouver si tu n'étais pas destiné à rester misérable toute ta vie ! Tu aurais dû être le premier à la mosquée, mais Allah n'a pas voulu que tu sois riche !

Da ma wannan wuridi da nike ja : na iyaye da kakannu ; na manyan rufannai su Gamgam Ya'ilu, su Tattara Ya'ilu… Alhamdulillahi, Allah na gode ma. Allah Sarkin kyauta !

D'ailleurs, j'étais persuadé que les incantations de nos ancêtres que je faisais aux des grands génies tels que Gamgam Ya'ilu, Tattara Ya'ilu… Oh Dieu, Merci ! Dieu, le pourvoyeur !

Liman : (Da ya jayo akwatin sai ya ce) : Bari mu buɗa mu ga abin da muka samu ! Kai, in samu algyabba irin ta Sarki ! Wannan ruwan tsanwa-tsanwan nan, ma ruwan… mine ne ake ce mata ?

L'Imam : (Il tire la cantine et dit) : J'ouvrons donc la cantine pour voir ce que je viens d'obtenir ! Oh (Allah) fait en sorte que j'y trouve un grand boubou comme celui du roi ! Le boubou multi couleur D'ailleurs comment appelle-t-on ce boubou ?

Ya lalaba, yana neman wuri buɗa akwatin.
Il se met à chercher l'ouverture de la cantine.

Liman : Ah, ni ina ne ma ? Eee ! Eee ! Nan ne ! Mine ne aka ce mata ? Algyabba irin ta Sarki, mai ruwan … Wane ne ma ake ce mata ? ko ceɗiya… ? ko ceɗiya… ? Yawwa ! Ita ba tsawa ba…, ta ba …, abun nan … ?

L'Imam : Ah, où est-ce donc ? Ah ! Ah ! C'est ici ! Comment est-ce qu'on l'appelle ? Le boubou du roi dont la couleur est verdâtre ? Oui, c'est ça !

Can, sai ya samu ya buɗa akwatin. Amma sai ya ishe mutum a mace a ciki maimakin kuɗin.
Enfin, il parvient à ouvrir la cantine. Mais au lieu de la fortune, il y trouve un cadavre.

Liman : La'ilaha illahu, muhammadan rasululalla sallahu, alaihi wasallama. Ni Liman ! Ni, mi za ni gani ! Allahu akbar ! Asshahadu Alla laha illallah ; asshadu annan muhamadan rasulullah… !

L'Imam : Il n'y a de Dieu qu'Allah. Mohamed est son messager. Paix et salut sur lui ! Moi l'Imam qu'est-ce que je vois ! Allah est grand ! Je témoigne qu'il n'y a de Dieu qu'Allah ! Je témoigne que Mohamed et son messager … !

Da jin hakan sai makwabta har da Ladan suka shigo su gani, ko lafiya.
Entendant ces invocations les voisins accourent pour voir ce qui se passe.

Ladan : Allah ya gafarta, Nagudu, wai wannan kiran salla… ! Mi ake yi ? Lafiya, Liman ? Mi ake yi Liman ?

Le Muezzin : Votre sainteté. Nagoudou, c'est quoi cet appel à la prière… ! Que se passe-t-il, Imam ?

Liman ya nunama mutanen akwatin tare da cewa :
L'Imam pointe du doigt la cantine en disant :

Liman : Ku diba dai abun da ke ciki !

L'Imam : *Regardez ce qu'il y a là-dedans* !

Ladan : Liman lafiya ?

Le Muezzin : Qu'y a-t-il ?

Liman: Diba dai Abin da ke ciki!

L'Imam : Vois de toi-même ce qu'il y a dedans !

Ladan : Mu mun dai ji kiran salla muka ce ba banza ba !

Le Muezzin : Nous avons simplement entendu l'appel à la prière et nous nous sommes dit que quelque chose n'allait pas bien !

Liman *(Ya matsa)* : Diba yana nan !

L'Imam (Il insiste) : Regarde, il est là !

Ladan ya je ya duba tare da cewa :
Ladan jette un coup d'œil dans la cantine en disant :

Ladan : Mine ne ? A'a, ku ɗaga mu gani ! Ɗaga ba komi !

Le Muezzin : C'est quoi ça ? Non, ouvrez pour qu'on voit ce que c'est ! Ouvrez la cantine il n'y a rien de grave !

Da ya ɗaga ya ga mutum a mace a ciki, sai ya yi tsalle tare da cewa :
Quand il ouvre la cantine et voit un corps sans vie ; il sursaute en disant :

Le Muezzin : La'ilaha illallaha ! Subahanallahi ! Wayyo! Wayyo, Liman! Yaya ankayi yi wannan mugun abu ya faru? Ina kai, ina kasha mutum; har da sawa a sanduƙi!

Le Muezzin : Il n'y a de Dieu qu'Allah ! Allah soit loué ! C'est grave ! Liman, comment une telle atrocité a-t-elle pu se produire ? Liman, comment as-tu pu tuer une personne et la mettre dans une cantine ?

Liman : *(Cikin raki ya ce)* Ina ni ina kasha mutum ! A masalaci na tsince shi!

L'Imam : (L'Imam pris de panique) Comment puis-je tuer une personne, moi ? Je l'ai trouvée à la mosquée !

Ladan : A masallaci ? Wallahi ; mutum ne ɗibgege a mace a cikin nan !

Le Muezzin : A la mosquée ? Au nom d'Allah c'est le cadavre d'un gaillard qu'il y a dans cette cantine !

Liman : Masallaci, wallahi Ladan ! Yaya za a yi yanzu ?

L'Imam : A la mosquée, je le jure Ladan ! Que faire à présent ?

Ladan : To wannan, yanzu ba haka ba za'a yi.

Le Muezzin : Bien, maintenant laisse-moi réfléchir un peu.

Liman : Mi ka ce ɗan'uwana ? *(Har ya mance abinda ya yi wa Ladan)*

L'Imam : Que dis-tu mon frère ? (Il a déjà oublié ce qu'il a fait à Ladan)

Ladan: Wannan ɓarnan taka! *(Ya maida martini.)*

Le Muezzin : Tu as vraiment commis une forfaiture ! (Il prend sa revanche.)

Liman : A'a, bannata ? Bari cewa ɓannata ! Ina ni ina kashe mutum !

L'Imam : Non, ma forfaiture ? Ne dis pas ça ! Comment puis-je tuer une personne ?

Ladan ya so ya fita amma Liman ya kame shi, tare da ba shi haƙuri.
Le Muezzin tente de sortir de la mosquée, mais l'Imam le retient en le suppliant.

Liman: Ya ka; ba hushi ba za ka yi. Yaya za'a yi ?

L'Imam : Viens ; ne te fâche pas. On va faire comment ?

Ladan ya turza, kamar ba zai yarda ba. Sai Liman ya ci gaba da lallasa shi.

Le Muezzin fait semblant de résister en s'en allant. L'Imam continue à le supplier.

Liman : A'a, bari hushi ! Yaya za mu yi yanzu ?

L'Imam : Non, ne te fâche pas. Comment pouvons-nous trouver une issue ?

Ladan: Yaya za a yi? Ɗauka za mu yi mu kai gidan Sarki. Mu, yanzu wannan ba ɓoyuwa ba zai yi!

Le Muezzin : Que faire ? Nous devons l'amener chez le roi ! Dans tous les cas une telle affaire ne se cache pas !

Liman ya ba da kai bori ya hau.
L'Imam accepte malgré lui.

Ladan: Ɗora mishi ake. A ɗora mishi.

Le Muezzin : Pose-lui la cantine sur la tête. Pose-la sur la tête.

Yana yi yana ƙara ba Liman tsoro.

Le Muezzin met plus de pression sur Liman.

Ladan: Mu tafi, in ya so in roƙa maka Kuma ka san dokar da Sarki ya aza.

Le Muezzin : Allons-y, je vais supplier le roi pour toi Puis tu sauras qu'il a interdit d'héberger un étranger.

Liman : Wannan mutum, ya cuce ni ! Wanda ya yi mini wannan abu!

L'Imam : Celui qui a fait ça m'a fait du tort ! Celui qui m'a fait une chose pareille !

Ladan : A ɗora mishi.

Le Muezzin : Posez la cantine sur sa tête !

Malam Sanusi : Ku ɗauka !

Monsieur Sanoussi : Prenez là !

Tsoro ya kama Liman, sai karkarwa yake yi. Ladan ke rarrashin shi amma yana yi yana ƙara ba shi tsoro.

L'Imam tremble de panique. Ladan le console mais en même temps profite pour mettre plus de pression sur lui.

Ladan: Ba karkarwa ba za ka yi, shi, mine ne wannan abu in Allah ya aiko shi.

Le Muezzin : Ce n'est pas la peine de trembler. On ne peut rien faire contre la volonté d'Allah.

Liman : Ladan ! Ladan ! Ku je ga ni nan tahe !

L'Imam: Ladan! Ladan! Allez-y. J'arrive!

Ladan: A'a, shiga gaba, muna bin ka. Kama hanya mu je. Ku je, mu je. Wannan abu sai dai Allah ya kiyaye !

Le Muezzin : Non, passe devant, nous allons te suivre ! Mets-toi en route. Cette affaire est grave !

Suka ɗauki gawar suka nufi fadar Sarki suna : « La'ilaha illallaha ».
A fadar sarki. Fadawa na zuwa da ɗai ɗai da ɗaiɗai.
Ils prennent le corps et marchent en direction du palais royal en récitant : « Il n'y a de Dieu qu'Allah ».
A la cour du roi. Les notables arrivent l'un après l'autre.

Turaki : Malamai, kun ji saƙon sarki ko ? Kun ji yanda take. Ya ce duk ƙasa.

Touraki : Messieurs, vous avez entendu le message du roi, n'est-ce pas ? Avez-vous bien compris ? L'interdiction concerne tout le royaume.

Fadawa : Ƙwarai kuwa ; ba wanda bai jiya ba !

Les notables : Bien sûr que si ! Il n'y a pas personne qui n'a pas entendu !

Suna cikin haka sai ɗan ƙaunar sarki Mununugi ya shigo. Ya durƙusa ya gaida su.
Pendant ce temps, Mounounougui, le neveu du roi, fait son entrée.

Turaki: Ah, Mununugi!

Touraki: Ah, Mounounougui!

Mununugi : Na'am !

Mounounougui : Oui !

Turaki : Matsa daga nan. Yaushe ka zo garin ?

Touraki : Approche par ici. Quand est-ce que tu es arrivé dans la cité ?

Mununugi : E ! Na ɗan kwan biyu. To da na zo sai na wuce gida wajan tsohuwata.

Mounounougui : Eh, ça fait quelques jours. Quand je suis arrivé, je suis d'abord allé au village pour voir ma mère.

Turaki : Yaya ? Karatu ya ƙare ?

Touraki : C'est comment tu as fini tes études ?

Mununugi : Ah ! Alhamdu lillahi, karatu ya ƙare !

Mounounougui : Ah ! Grace à Allah, j'en ai fini !

Turaki ya gabatar da Mununugi ga Fadawa.
Turaki présente Mounounougui aux notables

Turaki : Wannan, ba ku san shi ba ?

Touraki : Ce jeune homme, ne le reconnaissez-vous pas ?

Fadawa : Kaa ! (*Saura suka girgiza kai alamar ba su gamsu ba.)*

Les notables : Non ! (Certains font des gestes de la tête pour répondre négativement.)

Turaki : Ai ɗan ƙaunar sarki ne ! Wanda aka tura can. Wanda yake karatu na boko, karatu na shari'a!

Touraki : C'est le neveu du roi ! Celui qui a été amené là-bas… Celui qui est allé faire des études de droit !

Wani bafade: Kai! Shekara bakwai!

Un notable : Ah ! Sept ans déjà !

Nagudu : Ai an jima !

Nagoudou : Ça fait vraiment longtemps !

Turaki ya nuna wa Mununugi Malam Bala tare da cewa :
Touraki pointe du doigt Monsieur Bala en parlant à Mounounougui :

Turaki: Kai; ka san shi, wannan?

Touraki : Est-ce que tu connais ce monsieur ?

Malam Bala : Wannan, ina zai sani na ? Yanzu haka, rigar da ya yi mini tana nan gida aje !

Monsieur Bala : Comment peut-il me reconnaitre ? Mais le boubou qu'il m'a acheté est encore là à la maison !

Turaki : Wannan, wannan bayan nashi da kake gani, ya yi doro ; saboda ɗauka ka ne, tun kana ɗan ƙarami.

Touraki : Son dos vouté que tu vois, c'est parce qu'il t'a porté quand tu étais petit.

Malam Bala : Har kanta ya yi mini don goyon shi.

Monsieur Bala : Le fait de le porter m'a meme laissé une trace sur le dos.

Turaki : Mununugi, ka mance mutane, wallahi !

Touraki : Mounounougui, tu ne te rappelle plus des gens, je réalise !

Wani bafade : Ai ba yau ba ne !

Un notable : C'est que cela fait longtemps !

Nagudu : Shekara bakwai, ai ba kwana bakwai ba ne !

Nagoudou : Sept années ; ce n'est pas sept jours !

Turaki : Wallahi ka mance mutane !

Touraki : Vraiment, tu ne te rappelles plus des gens !

Ana cikin haka sai sarki ya shigo. Sarkin dogarai ne ya yi alama kamar haka: to; to! Duk fada kowa ya tashi ya miƙe.
A ce moment le roi fait son entrée. Le chef des gardes fait un signe pour annoncer aux notables l'arrivée du roi. Tout le monde se met debout.

Turak i : Allah ya ba ka nasara ! Allah ya taimake ka !

Touraki : Gloire à sa majesté ! Puisse Allah te protège !

Sarki : Amin !

Le roi : Amen !

Sarki ya zauna. Sannan sauran Fadawa su ma suka zauna. Lokacin da suke zaunawa sai Mununugi ya gyara wa Turaki hannun rigarsa da ke reto. Ya yi masa godiya.
Le roi se met assis et les notables font de meme. Au moment de s'assoir Mounounougui arrange un pan du boubou de Touraki qui trainait par terre. Turaki le remercie pour le geste.

Turaki : A gaishe ka Mununugi !

Touraki : Merci, Mounounougui !

Wannan ya sa sarki ya lura da Mununugi.
Ces propos attirent l'attention du roi sur Mounounougui.

Sarki : Mununugi !

Le roi : Mounounougui !

Mununugi : Ranka ya daɗe !

Mounounougui : Votre majesté !

Sarki: Yaushe ka shigo garin?

Le roi : Quand est-ce que tu es arrivé ?

Mununugi : Shekaranjiya na zo, ranka ya daɗe. Amma da na zo sai na wuce gida na ga Tsohuwa.

Mounounougui : Avant-hier Votre majesté ! Mais dès mon arrivée, je suis allé saluer ma maman.

Sarki : Daidai ne ! Ya yi kyau !

Le roi : C'est juste ! C'est très bien !

Turaki : Shi ne, yanzu da ya zo, na ce ya shiga cikinmu ya zauna. Ka san yaro sai ana sa shi cikin manya yake…

Touraki : C'est ainsi qu'à son arrivée, je lui ai dit de s'assoir parmi nous. Vous savez, les jeunes, c'est en les rapprochant des sages qu'ils…

Sarki: Ka ƙare karatun; ko da saura?

Le roi : As-tu fini les études, ou bien ça reste encore ?

Turaki : Sarki ya ce ka ƙare karatu ?

Touraki : Le roi demande si tu as fini les études.

Mununugi : Na ƙare, ranka ya daɗe !

Mounounougui : J'ai fini, sa majesté !

Turaki : …Kuma ka samu takardun shaida ?

Touraki : … As-tu obtenu tes diplômes ?

Mununugi : E

Mounounougui : Oui !

Turaki : Allah ya baka nasara ; ai yanzu sauran aiki.

Touraki : Votre majesté, il ne lui reste qu'à trouver un emploi !

Sarki : Karatun mine ne ma ka yi ? Saboda ka daɗe kana yi, fa!

Le roi : Qu'as-tu étudié ? Tes études ont vraiment duré !

Turaki : Ya ce mini, karatun shari'a ya yi

Touraki : Il m'a dit qu'il avait étudié le droit.

Sarki: Karatun shari'a? To, madalla!

Le roi : Le droit ? Ah, c'est bien !

Turaki: Yanzu tsal muka yi zancen da shi. Yaro ya yi hankali. Ai, gadon gidanku ne shari'a.

Touraki : Nous venons juste d'en parler avec lui. Le gamin est devenu sage ! La profession de droit est une tradition de votre famille !

Sarki: Ai irin wannan karatu ake so. To ku, da ku nike!

Le roi : Ce genre d'études est très utile. Bon, vous, écoutez-moi !

Turaki : Sarki ya ce ku saurara !

Touraki : Le roi vous demande de l'écouter !

Sarki : Maganata wadda ni aje …

Le roi : La décision que j'ai prise … !

Turaki : Sarki ya ce abin da ya aje mumu…

Touraki : Le roi dit que la décision qu'il a prise concernant le royaume….

Sarki : Akwai ta, ko babu ?

Le roi : Elle est effective ou non ?

Turaki : Akwai, ko babu ?

Touraki : Le roi demande si elle effective ou non.

Sauran fadawa : Ta tsaya !

Les autres notables : Elle est effective !

Sarki : Wallahi, duk wanda ya taka wannan doka … ku fa ina magana da ku fa !

Le roi : Au nom d'Allah, tout celui qui enfreindra cette décision… vous m'entendez ?

Fadawa : Lumfasawa ! Lumfasawa !

Les notables : Que votre volonté soit faite ! Que votre volonté soit faite !

Turaki : Ai yanzu, a karkarar nan kap, babu wanda bai san ba da dokarka ; babu wanda bai ji ta ba !

Touraki : A la date d'aujourd'hui, il n'y a personne qui ne soit pas au courant de ta décision ! Personne ne l'ignore !

Shigowar su Liman ƈauke da akwati ya katse wannan zance.
Aka fara addu'a, da yake kodayaushe idan Liman ya zo fada sai an yi fatiya kana ya zauna. Amma wannan karo ba kamar kullum ba ganin halin da Liman yake ciki.

L'entrée de L'Imam et ses voisins avec une cantine interrompt la conversation.
On commence par la fatiya comme c'est la tradition à chaque fois que l'Imam met pieds à la cour Mais cette fois-ci c'est différent étant donné la situation dans laquelle se trouve l'Imam.

Liman: Allah ya ba ka nasara!

L'Imam: Votre Majesté!

Turaki: *(Ganin sun ƈauko akwati, ji yake yi wasu kaya ko dukiya ne a ciki)* Amin Liman! Amin Ladan ! A gaishe ku ! A gaishe ku !

Touraki : (Voyant l'Imam et ses voisins avec une cantine, il pense que celle-ci est pleine d'objets de valeur) Amin l'Imam ! Bonne arrivée ! Bien fait !

Sauran fadawa ma suka yi ta cewa amin har aka shafa addu'a.
Les autres notables répètent Amin jusqu'à la fin de l'invocation.

Turaki: Wannan ya yi kyau!

Touraki: Ça c'est bien!

Ladan da kodayaushe kusan Liman yake zama, wannan karon sai ya zauna nesa da shi. Ganin haka sai Turaki ya yi tuni.
Le Muezzin qui d'habitude s'assoie à côté de l'Imam s'est assis loin de ce dernier. Remarquant cela Turaki lui fait des reproches.

Turaki : Ladan, shin ɓacewa ka yi ? Ai nan ne wajenka kusan Liman !

Touraki : Le Muezzin, tu t'es trompé de place ? C'est ici ta place à côté de l'Imam !

Ladan: Ka san yau hankalin ba namu ba ne!

Le Muezzin : Tu sais aujourd'hui je ne suis pas la conscience tranquille !

Liman cikin karkarwa, ya ce yi fatiya. Ya ja doguwar fatiya. Sai Amin jama'a suke ta yi Fatiya ta ƙi ƙarewa. Ganin haka Turaki ya katse shi.
L'Imam tremble en faisant la traditionnelle fatiya. Une très longue fatiya ponctuée par les amens des notables au point que Turaki interpelle l'Iman pour en finir.

Turaki : Kai ! Kai ! Liman ! Wannan fatiya ta yi yawa ! Lafiya ma ?

Touraki : Oh, oh Imam ! Cette invocation est trop longue ! Y-a-t-il un problème ?

Liman : Lafiya ba lafiya ba ! Ni dai a masallaci na tsince shi !

L'Imam : Ça va, ça ne va pas ! J'ai trouvé cette cantine à la mosquée.

Sarki : Sarkin Dogarai !

Le roi : Chef des gardes !

Turaki : Sarkin Dogarai ! *(Ya nuna akwati)* A je, a sa wannan cikin gida !

Touraki : Chef des gardes ! (Il montre la cantine) Emmène ça à l'intérieur !

Ladan : *(Yana ƙoƙarin neman izinin dakatar da sarkin dogarai)* Allah ya ba ka nasara, dakata, Sarkin dogarai !

Le Muezzin : (Cherchant l'autorisation de stopper le chef des gardes) Sa majesté ; Attend, chef des gardes !

Sarki : Mine ne, kai ko ?

Le roi : C'est quoi Ladan ?

Ladan: Wannan ba ya shiga gidan Sarki!

Le Muezzin : Cette cantine ne doit pas être amenée à l'intérieur du palais !

Fadawa : A'uzu billahi !

Les notables : Qu'Allah nous en préserve !

Sarki: Watau, don ku yi mini shegantaka ne, da rishin kunya, da lalata! A gidan wa zai shiga?

Le roi : Ainsi donc, vous vous moquer de moi ? Alors chez qui envisagez-vous de l'emmener ?

Ladan : Allah ya ƙara zamaninka ; shi dai wannan abu tsautsayi ne ; ko mutum ne Liman ya rabke a masallaci.

Le Muezzin : Longue vie à votre Majesté ! C'est vraiment un accident, une personne que l'Imam aurait tuée se trouve dans cette caisse !

Sarki : Mutum ?

Le roi : Un être humain ?

Ladan : Um, matacce ba !

Le Muezzin : Oui, un cadavre !

Turaki : Yanzu Liman ka ji sarai dokar da sarki ya aza a gaban ka kuma har ka kama ka kashe mutun ! Ai yau ƙaryarka ta ƙare !

Touraki : Imam tu connais très bien l'interdiction du roi décidée à ta présence mais malgré tout a tué une personne ! Ç'en est fini pour toi !

Turaki ya tashi ya raɗa wa sarki wata magana a kunne.

Touraki se lève et murmure quelque chose à l'oreille du roi.

Sarki : Liman ?

Le roi : Imam ?

Liman : Na'am !

L'Imam : Oui !

Turaki : Sarki ya ce ku malamai, kun soma yanka mutane … ! Don haka kai, ka soma yanka mutane! Kuma don rashin kunya, da kanka, don kana malami, ka kawo fada!

Touraki : Le roi dit que vous les marabouts, vous avez commencé à tuer des gens. Ainsi, tu as commencé à en tuer. Et comme tu n'as de respect pour personne, parce que tu es marabout, tu amènes le cadavre toi-même à la cour !

Ya juya, ya dibi sarki sannan ya yi magana.
Il se tourne vers le roi et lui parle.

Turaki: Allah ya ba ka Nasara, wannan shari'a tana gare ka!

Touraki : Sa majesté, à toi de faire ce jugement !

Sarki : *(Ya nuna wa Liman yatsa tare da yi masa faɗa)* : Ai da ma na ga baƙaƙen riguna nan da kake sawa, kana ɗora musu farare bisa…

Le roi :(Il pointe l'Imam du doigt et le sermonne) : Ça ne m'étonne pas, avec tous tes grands boubous noirs sur blancs…

Turaki : Sarki ya ce, fara da baƙa da tsanwa da ja shuɗin kayan nan da kake sawa…

Touraki : Le roi dit les vêtements blancs, noirs, verts, rouges et bleus que tu portes…

Sarki : Kana kwaikwayo na …

Le roi : En voulant te présenter comme moi …

Turaki : Sarki ya ce, kana tamaƙa irin tashi… !

Touraki : Le roi dit que tu vas jusqu'à imiter sa démarche… !

Sark i: E, kamar ƙasar taka ce…!

Le roi : Oui. Comme si c'était toi qui règnes sur le royaume… !

Turaki : Sarki ya ce kamar kai kake ikon duniya

Touraki : Le roi dit comme si c'était toi le maître du monde !

Sarki : Wai, mine ne Liman, ba ni ba nike sa shi ?

Le roi : Mais qu'est-ce qu'un Imam ? N'est-ce pas moi qui le nomme ?

Turaki : Sarki ya ce, Liman ba shi yake sa shi ba !

Touraki : Le roi dit, est-ce pas lui qui le nomme !

Sarki : Insha ma Allahu kwanakinka sun ƙare !

Le roi : Avec la volonté d'Allah tes jours sont finis !

Turaki : Sarki ya ce daga yau ka ƙare lumfashi !

Touraki : Le roi dit qu'à partir d'aujourd'hui tu ne respireras plus

Sarki : Eee ! Liman ni na naɗa shi ! Kuma yanzu ina iya naɗa wani! Kuma in ina so gobe ma in naɗa wani. Jibi ma in naɗa wani!

Le roi : Oui ! C'est bien moi qui nomme L'imam ! Et, maintenant même je peux nommer un autre si je veux et en faire de même demain, après demain !

Turaki : Sarki ya ce kullum yana naɗa wani !

Touraki : Le roi dit qu'il peut changer d'Imam à volonté !

Sarki : Sarkin dogarai ! Kama mini munafikin nan, ka je ka cire mishi kai !

Le roi : Chef des gardes ! Attrape cet hypocrite et va lui trancher la tête !

Turaki: Maganinka kenan! Duk karatun da ka yi…!

Touraki : C'est bien fait pour toi ! Malgré toutes les études que tu as faites… !

Sarki : Ni za a yi ma shegantaka ; Liman ?

Le roi : Tu oses te moquer de moi ; Liman ?

Turaki : Je ka da shi sarkin Dogarai !

Touraki : Amène le chef des gardes !

Gani an cukwuikwuyi Liman, tausayi ya kama Ladan, don ya san ba laifin shi ba ne. Ya yarda zai faɗin abin da ya sani a kan wannan akwatin, amma yana yi yana jin tsoro. Voyant la manière violant avec laquelle l'Imam a été pris, Ladan a eu pitié de lui sachant qu'il n'est pas responsable de la mort du cadavre. Alors Ladan décide de faire des aveux.

Ladan : Allah ya ba ka Nasara… !

Le Muezzin : Votre majesté… !

Turaki : Dakata Sarkin dogarai ! Zo daga nan kusa… Fidda mini shi nan !

Touraki : Attend, chef des gardes ! Viens par ici… Amène le ici !

Ladan : Allah na gani, bai kamata ba … ! Kiyon Musulmi ya faɗi gaskiya ; ko ba haka ba !

Le Muezzin : Allah nous voit tous, il n'a pas menti… ! Un bon musulman doit dire la vérité ; n'est-ce pas ?

Turaki : Mine ne ?

Touraki : Qu'y a-t-il ?

Ladan: Uhum, Uhum…! Wai shi mataccen wannan…

Le Muezzin : Uhum, Uhum… ! A propos du cadavre …

Turaki: Mine ne? Ka buɗe baki ka yi wa Sarki magana; kana wani…

Touraki : C'est quoi ? Ouvre la bouche et parle au roi ; tu es entrain de…

Ladan : Akwatin, na ce… akwatin… akwatin !

Le Muezzin : Je parle de la cantine, … la cantine… la cantine !

Turaki: Yo akwati mi ya yi? Kai buɗe baki ka yi Magana!

Touraki : Bon qu'a fait la cantine ? Toi ouvre ta bouche et parle !

Ladan : Ni ma na ɗauko shi !

Le Muezzin : Je l'avais aussi retrouvée !

Sarki: Haba Ladan; ka ɗauki mi?

Le roi : Oh non, Ladan ! Tu as pris quoi ?

Turaki : Allah ya ba ka nasara !

Touraki : Votre majesté… !

Ladan : Amma, na rantse da Allah, a masallaci na tarda shi ! Allah na ji ; Allah na gani !

Le Muezzin : Mais, je jure par Allah, je l'avais trouvé à la mosquée ! Allah est témoin !

Sarki : Sarkin dogarai kama shi ka kashe shi !

Le roi : Chef des gardes, attrape-le et tue-le !

Sarkin dogarai ya kama Ladan.
Le chef des gardes s'empare de Ladan.

Ladan: (*Yana magiya)* Sarkin dogarai, na rantse: wabillahillazi, a can na same shi!

Le Muezzin : (Il tente de convaincre le chef des gardes) Chef des gardes, je te jure que c'est là-bas que je l'ai trouvé !

Sarki : Ku wuce, kwanakinku sun ƙare ; munafukan wofi !

Le roi : Avancez, vous êtes morts, hypocrites !

Turaki: Allah ya ba ka nasara! Ai abin da ya yi Liman; shi ya yi Ladan! Ce, kun gamu, ku malamai, kun kashe mutane !

Touraki : Votre majesté ! L'Imam et Ladan sont même pipe même tabac ! (S'adressant à Liman) Vous avez comploté, vous les marabouts, pour tuer des personnes !

Sarki : (*cikin fushi*) Ni za ku yi ma shegantaka a cikin ƙasata ? Ku gama kai Liman da Ladan, ku kashe mutum … ƙasar taku ce ? Ku kuke ikon ƙasar ? Ba ni ba nake naɗa ku ?

Le roi : (Très en colère) Vous osez vous moquez de moi dans mon propre royaume ? Vous vous unissez pour tuer quelqu'un… Est-ce que le royaume vous appartient ? Est- ce que vous êtes le roi ? N'est-ce pas moi qui vous nomme.

Ladan: Tsintuwar da muka yi. In ba masallaci ba ina muke tsintuwa?

Le Muezzin : Nous avions trouvé la cantine à la mosquée. Où est-ce nous pouvions trouver quelque chose si ce n'est pas à la mosquée ?

Sarki : Yau kun ƙare tsintuwa !

Le roi : Aujourd'hui c'est votre dernière trouvaille !

Fada ta hargitse. Ran sarki ya ɓaci matuƙa. Can shi ma Nagudu ya nemi ya yi magana.

L'ambiance est morose au palais car le roi est très fâché. De son coin, Nagoudou cherche aussi à faire des aveux

Nagoudou : Ranka ya daɗe !

Nagoudou : Votre majesté !

Turaki : Wai kai (Nagudu), mine ne ?

Touraki : Toi (Nagoudou) aussi ; qu'est-ce qu'il y a ?

Sarki : Kai ma (Nagudu), mine ne ? Kai ma son kakai ka ce da kai ciki ; ko ?

Le roi : Toi aussi (Nagoudou) c'est quoi ? Toi aussi tu veux dire que tu es impliqué ; n'est-ce pas ?

Turaki: Ka buɗa baki ka yi magana!

Touraki : Ouvre ta bouche et parle !

Nagudu: Wannan mutumen da ke cikin akwatin wannan, a gidana ya faro!

Nagoudou : Cet homme-là qui est dans la cantine, il vient de chez moi !

Sarki : *(Rai ya ƙara ɓaci) :* Kai ma, Allah ya jiƙan ranka ! Sarkin dogarai, kama mini munafikin banza !

Le roi :(Plus furieux) : Paix à ton âme aussi ! Chef de gardes attrape cet hypocrite !

Turaki : Tashi ! Fudda mini su gaba ɗaya. Ku tafi !

Touraki : Lève-toi ! Emmène-les tous. Allez-y !

Mununugi ya ga abin yana fama ya wuce hankali. Ya kasa haƙuri, ya nemi a bar shi ya yi magana.

Voyant que situation va de mal en pis, Mounounougui demande la parole.

Mununugi : Ranka ya daɗe !

Mounounougui : Votre majesté !

Turaki : Wai kai, mine ne kaima ?

Touraki : Mais toi aussi, qu'y a-t-il ?

Mununugi: Wannan sha'anin fa… Bincike ya kamata, a diba shi.

Mounounougui : Cette affaire … mérite une véritable enquête.

Turaki : Nufin ka ?

Touraki : Qu'est-ce que tu insinue ?

Mununugi: Bincike ya kamata a yi! Mutuwar mutumen wannan ya kamata a bincike ta!

Mounounougui : On doit mener une investigation ! La mort de cet homme-là nécessite une investigation !

Turaki : Ina Mununugi ?

Touraki : Mounounougui ?

Mununugi : Ita shari'a sai da hankali, ranka ya daɗe !

Mounounougui : Le jugement nécessite beaucoup de prudence, Votre Majesté !

Sarki : Ɗan farka kai ; Ba mu ba muka sa ka karatun ?

Le roi : Fils de pute ; n'est-ce pas nous qui t'avions inscrit à l'école ?

Turaki : Sarki ya ce, ba shi ba ya sa ka karatun (da kake Tinƙaho) ?

Touraki : Le roi dit : est-ce que ce n'est pas lui qui t'a inscrit à l'école (dont tu te targues à présent) ?

Mununugi : Kwarai kuwa !

Mounounougui : Bien sûr que oui !

Sarki : Kai fa ɗan kanwata ne !

Le roi : Toi tu es mon neveu !

Mununugi : Kwarai kuwa !

Mounounougui : Bien sûr que si !

Sarki : Shekaranjiya shekaranjiya nan, muka kama ka nan muka sa ka karatun !

Le roi : Il n'y a pas longtemps que nous t'avions inscrit à l'école !

Turaki: To yanzu, me kake so?

Touraki : Bon maintenant, qu'est- ce que tu veux ?

Sarki: Tun ba a haife ka ba muke shari'a! To, mi kake so ?

Le roi : Je rends des jugements depuis avant ta naissance ! Alors qu'est-ce que tu veux ?

Mununugi : Ya kamata wannan haraka a diba ta sosai !

Mounounougui : Je pense que cette affaire doit être bien investiguer !

Turaki : Wace irin dibawa ? Banda sun taka dokar Sarki ?

Touraki : Quelle investigation ? Ils ont déjà enfreint la loi du roi.

Mununugi: A yi mini afuwa, in yi wannan shari'ar!

Mounounougui : Faites- moi une dérogation pour que je fasse ce jugement !

Turaki : Lailaha illallah ! Amma Mununugi, ka koyi lalata ! Yanzu ɗan karatun da ka je ka yi, har kake jin ka fi sarki ilimi ?

Touraki : Il n'y de dieu qu'Allah ! Mounounougui, tu es appris de mauvaises choses ! A cause de tes études insignifiantes tu penses être plus intelligent que le roi ?

Turaki : Da ilimi, da hankali da shari'a, ai sarki yake yi ! Tun ba a haife ka ba a nan gidan, ake shari'a!

Touraki : Le savoir, la sagesse et la justice sont l'apanage du roi ! Ici dans cette cour on fait les jugements depuis avant ta naissance !

Mununugi : Ranka ya daɗe yo, ai shari'a iri-iri ce !

Mounounougui : Votre majesté ! Il y a plusieurs manières de rendre justice

Turaki: To, wace iri ce irin taka?

Touraki : D'accord, quelle est ta manière ?

Sarki : Na ji abinda ka faɗa !

Le roi : J'ai entendu ce que tu as dit !

Turaki : Sarki ya ce ya ji abinda ka faɗa !

Touraki : Le roi dit qu'il t'a entendu !

Sarki: Za ni ba ka izini ka yi min shari'a.

Le roi : Je vais t'autoriser à faire le jugement.

Turaki : Sarki ya ce zai ba ka izini de ikon yin shari'a !

Touraki : Le roi dit qu'il va te donner l'autorisation de faire le jugement !

Sarki: A samo wanda ya kashe wannan mutum!

Le roi : Qu'on retrouve celui qui a tué cet homme !

Turaki: Sarki ya ce, a samo wanda ya kashe wannan mutum!

Touraki : Le roi te demande de retrouver l'assassin de cet homme !

Sarki: In kuwa ba ka samo shi ba…!

Le roi : Si tu n'arrives pas à le retrouver… !

Turaki: In kuwa ba ka samo shi ba…!

Touraki : Mais si tu n'arrives pas à le retrouver… !

Sarki: In sha Allahu, kai ma a gama da kai, ka sha wuƙa!

Le roi : Toi aussi, tu seras exécuté comme les autres !

Turaki : Sarki ya ce kai ma yanka ka za a yi kamar yadda za a yanka Liman !

Touraki : Le roi dit que tu seras exécuté comme l'Imam !

Sarki: In ma kana ɗan kanwata yanka ka zan yi! Tashi, ga ta ka yi !

Le roi : Meme si tu es mon neveu tu seras exécuté ! Va à toi de retrouver l'assassin !

Turaki : *(Ya ce ma su Liman)* ku zauna !

Touraki : Asseyez-vous ! (S'adressant à l'Imam et ses compagnons d'infortune)

Ladan : (Ya nuna wa Nagudu yatsa tare da cewa) : Amma kai, tsakanin mu da kai, Allah ya isa !

Le Muezzin : (Pointant Nagoudou du doigt) Toi là, nous nous remettons à Allah pour ce que tu nous fais subir !

Sarkin dogarai : Ku zauna ! Ku zauna, aka ce !

Chef des gardes : Asseyez –vous ! Asseyez-vous ! C'est un ordre !

Turaki : (Ya turi Nagudu tare da ce masa) : matsa can !

Touraki : (Il pousse Nagoudou en lui disant) : Pousse-toi là-bas !

Mununugi : Ina Liman ?

Mounounougui : Où est l'Imam ?

Liman : Ga ni Biyamaradi !

L'Imam : Me voici, mon Prince !

Mununugi : Ina ka samo akwati ?

Mounounougui : Où est-ce que tu as eu la cantine ?

Liman : Ni ko, Biyamaradi, ina zan samu akwati in ba masallaci ba ? Ina tsammani zakka ce ka san shekara tayi ; na ce wani maikuɗi ya kai, ya sa a masallaci, sadaka !

L'Imam : Mon Prince où est-ce que je pouvais trouver la cantine, si ce n'était pas à la mosquée ? Je pensais que c'était de la zakat que quelqu'un avait déposée à la mosquée pour aumône comme nous somme à la fin de l'année Islamique

Mununugi Hum! (Sannan ya nufi Ladan) To kai fa? Ka ce kai ma ya biyo ta wajanka akwatin wannan ?

Mounounougui : Hum ! (S'adressant à Ladan le muezzin) Et toi ? Tu dis que la cantine a passé par toi ?

Ladan : Ni ma kamar Liman ne. In ba a masallaci ba, ina ni, ina tsintuwa! Kai dai ɗan kwaɗayi ne, cewa muke dukiya ce! Laifi, ba mu kawo ba ne!

Le Muezzin : Moi-même c'est comme ce que l'Imam a dit. Si ce n'est pas à la mosquée, où pourrais-je trouver quelque chose ! En fait c'est de la cupidité ! Nous pensions que c'était un trésor. Notre faute c'est de n'avoir pas prévenu les autorités !

Sarki : Ku, malamai masu zalama ko ? Kwa faɗi gaskiya yau !

Le roi : Vous les marabouts cupides ; n'est-ce pas ? Vous allez dire la vérité, aujourd'hui !

Turaki : Sarki ya ce, kun faɗi gaskiya !

Touraki : Le roi dit que vous allez tout avouer aujourd'hui !

Mununugi:*(Ya juya kan Nagudu)* : Kai, yaya aka yi, ka ce mutumen wannan a gidanka ya rasu ?

Mounounougui : (S'adressant à Nagoudou) : Toi, dis-nous comment est- ce que cet homme est décédé chez toi ?

Nagudu : Biyamaradi, Allah yana gani, wannan mutumen a gidana ya mutu !

Nagoudou : Mon prince, Allah est témoin que cet homme est décédé chez moi !

Turaki : Nagudu, ka ci amanar sarki ! Kai, a nan, a gaban ka, aka aza wannan dokar!

Touraki : Nagoudou, tu as trahi la confiance du Roi ! Tu étais présent quand la décision avait été prise !

Mununugi : Gidanka ? Kenan…

Mounounougui : Chez toi ? Donc …

Turaki : Nagudu, kai, ka ci amanar Sarki, Wallahi !

Touraki : Nagoudou, tu as vraiment trahi la confiance du roi !

Mununugi : Ka sauke baƙo, ba ka ji abinda Sarki y ace ba, ko ?

Mounounougui : Tu as hébergé un étranger malgré l'interdiction du roi ?

Nagudu : Biya maradi… !

Nagoudou : Mon prince … !

Mununugi: Ka taka dokar Sarki kenan!

Mounounougui : Ainsi tu as délibérément violé la loi promulguée par le roi !

Turaki: Nagudu ka yi ɓanna!

Touraki : Nagoudou tu as vraiment commis un crime !

Ladan : Ƙwarai ko ! Ya kai a masallaci don ya cuce mu, da ni da Liman !

Le Muezzin : Effectivement ! Et il a amené le cadavre à la mosquée pour nous faire accuser !

Turaki : Ku ko, da zafin kwaɗayi, kuka ɗauka, ko ?

Touraki : Et vous les cupides, vous vous en êtes emparé du la cantine, n'est–ce pas ?

Mununugi: To mutumen da ya zo, yaya ka yida shi?

Mounounougui : Bien quand l'homme est arrivé chez toi, qu'as-tu fait de lui ?

Nagudu : Biya maradi, wannan mutumen da dare ƙwarai ya zo min a gida. Ya sallama, dare ya raba lokacin nan, ya tambaye ni alfarma in sauke shi… Ni ba shi makwani, nan ya kwanta. Washe gari ko, da ni tashi sai na iske ya mutu.

Nagoudou : Mon prince, cet homme était arrivé chez moi très tard dans la nuit. Il s'était annoncé vers minuit. Il avait demandé une faveur pour être hébergé. Ainsi je lui avais donné une place pour passer la nuit. Le lendemain, quand je m'étais réveillé, je l'avais trouvé mort.

Mununugi : To, da ya zo, bai ce ma ba bai da lafiya ?

Mounounougui : Bien quand il est arrivé, n'a-t-il pas dit qu'il était malade ?

Nagudu: Yana dai ɗan tarishi, ɗan kaɗan. Ba mai damun shi ba ne !

Nagoudou : Il toussait un peu mais ça ne semblait pas le déranger !

Turaki : Wane iri ne ? Yaya yake tarin ? Yi mu ji. Ee !

Touraki : Quel genre de toux ? Comment toussait-il ? Fais un peu comme lui pour qu'on entende !

Nagudu : To, Turaki !

Nagoudou : D'accord Touraki !

Turaki: Tara kaɗan; ji!

Touraki : Tousse un peu pour qu'on entende !

Nagudu ya ɗan tara.
Nagoudou tousse un peu.

Nagudu : To, da ya fara, sai na ce ya rage ; don kar a ji, ee !

Nagoudou : Bon, quand il a commencé à tousser, je lui avais dit de ne pas tousser fort, de peur qu'on ne l'entende.

Mununugi: Ba ka ba shi baa abinci? Ka san, baƙo in ya zo, ana bashi abinci kan ya kwanta, ko?

Mounounougui : Tu ne lui as rien donné à manger ? Tu sais comme c'est la tradition, un étranger on lui donne à manger avant qu'il se couche ?

Nagudu : I, Biyamaradi ! Ni lokacin da ya zo, bai iske tuwo ba gidana. Da na tambayi maiɗakina, saita ce, babu. Amma akwai hura. Sai na ce a dama hurar nan a bas hi, ya sha.

Nagoudou : Effectivement mon prince ! Quand il était arrivé il ne restait plus de T[8]ouwo. Quand j'en avais demandé à mon épouse, elle me l'avait confirmé, mais elle m'avait dit qu'il y avait du foura[9]. Alors je lui avais demandé de lui préparer ce foura ; et c'était ça qu'il avait bu avant de se coucher.

Mununugi : Sai aka sa nono, aka ba shi.

[8] Pâte traditionnelle à base de farine de céréales
[9] Aliment traditionnel à base du mil ou sorgho

Mounounougui : Vous ɣ aviez ajouté du lait caillé et vous lui aviez donné.

Nagudu : Babu nono. To, da yake ɣan magana sun ce baƙonka Allanka ; Allah ya sa akwai ɣar zumuwa da na sayo…

Nagoudou : Il n'ɣ avait pas de lait caillé. Mais comme on a coutume de dire ton étranger est ton Dieu, Dieu a fait qu'il ɣ avait du miel que j'avais acheté auprès de Leka- Kogo.

Sarki : Baƙonka, makashinka ! Kwananka ya ƙare, munafikin banza !

Le roi : Ton étranger, ton assassin ! Je te ferai tuer, espèce d'hɣpocrite !

Turaki : Ai Nagudu, na ce maka munafiki ne !

Touraki : Je t'avais déjà dit que Nagoudou était un hypocrite !

Sarki : Ban aje doka ba, na ce kar wanda ya aje mini baƙo ? Don shegantaka, ka aje shi har ya mutu a gidanka !

Le roi : N'ai-je pas interdit d'héberger tout étranger ? Mais tu en héberge un et il meurt chez toi !

Turaki : Shi ma ne ya sa na ce, ya je, ya yi wasan ƙira, ya wa ɣan garin su !

Touraki : C'est pourquoi je lui ai toujours suggéré de retourner chez lui faire le griot !

Sarki : *(Ya ce ma Mununugi)* ci gaba da shari'ar taka ! In ba ka samo wanda ya kashe wannan mutum ba, ku mutu tare!

Le roi : (Il s'adresse à Mounounougui) continue ton jugement ! Si tu ne trouves pas l'assassin, vous mourrez ensemble !

Mununugi : To, muna saurarenka.

Mounounougui : Bien, on t'écoute.

Nagudu : Zumuwan nan da na sayo ta, na ce ma maiɗakina a ɗiba a sa, a gurmaza aba shi ya sha. To, ka ji abin da ya sha gidana hurar nan da zumuwan nan aka gama aka dama ta.

Nagoudou : J'avais instruit ma femme de prélever dans le miel que j'avais acheté, et l'ajouter au foura avant de le lui donner. C'était ça que nous lui avions donné : le foura là, auquel nous y avions ajouté du miel.

Mununugi : Zummuwan ta daɗe da ka saye ta ?

Mounounougui : Ça fait longtemps, que tu as acheté ce miel ?

Nagudu: A'a, shekaranjiya tsal na sayo ta a kasuwa!

Nagoudou : Non, c'est avant-hier seulement que je l'ai acheté !

Mununugi: Ba ka ɗanɗana ba?

Mounounougui: L'as-tu goûté?

Nagudu: Kaita niyi a gidana…

Nagoudou : Non, je l'ai amané chez moi…

Mununugi : Ko kai, ko maiɗakinka, ko yara, duk ba wanda ya sha ta ?

Mounounougui : Ni toi, ni tes enfants, ni ton épouse personne n-y a goûté ?

Nagudu: A gidana dai ba wanda ya ɗanɗana.

Nagoudou : En tout cas chez moi personne n'y a goûté

Mununugi: Uhum; yo, ka san wanda ya saida zummuwar wannan?

Mounounougui : D'accord, te souviens-tu de celui qui t'a vendu ce miel ?

Nagudu : Kwarai kuwa ! Kwarai kuwa ! Wajen Leƙa kogo da idon wani na sayo ta.

Nagoudou : Bien sûr que oui ! Bien sûr que oui ! C'est auprès de Leka-kogo que je l'ai acheté.

Mununugi: Leƙa kogo da idon wani…!

Mounounougui : Leƙa kogo da idon wani (Un nom comique qui signifie « *regarder à l'intérieur du trou d'un arbre avec les yeux de quelqu'un* ») ?

Nagudu : E.

Nagoudou : Oui.

Mununugi : Allah ya ba ka nasara !

Mounounougui : Votre majesté !

Sarki : Na'am.

Le roi : Oui.

Mununugi : Ina so a je a kawo Leƙa-kogo-da-idon wani.

Mounounougui : Je voudrais qu'on amène Leka –kogo.

Sarki : Sarkin dogarai !

Le roi : Chef des gardes !

Sarkin dogarai : Ranka ya daɗe ! (Ya matso kusa da sarki)

Chef des gardes : Votre majesté ! (Il s'approche du roi)

Nagudu : Yana nan bakin kasuwa !

Nagoudou : Il est là à l'entrée du marché !

Sarki : (Cikin tsanani sarki ya yi mai magana) Ka je bakin … kasuwa !

Le roi : (Avec fureur) Vas au… marché !

Wani bafade : Tabbas !

Un notable : Il a dit la vérité !

Sarki : Anka ce akwai wani, ko Leƙa-kogo-da - idon wani yake, ko da idon duniya ya kawo mini shi.

Le roi : Il y a un certain leka-kogo avec je ne sais quoi, qui qu'il soit amène le moi !

Sarkin dogarai : An gama !

Chef des gardes : A vos ordres !

Sarki: A kan hanya ko tuntuɓe ya yi, cire mishi kai! Ko tari ya yi cire mishi kai ; ni na ce ! Ya yi magana a nan !

Le roi : S'il oppose la moindre résistance tranche-lui la tête ! C'est mon ordre ! Il va parler une fois ici !

Sarkin dogarai ya kama hanya zai tafiya, Mununugi ya ce ya tsaya.
Le chef des gardes sort pour aller chercher le vendeur du miel mais Mounounougui lui demande d'attendre un peu.

Mununugi : Dakata.

Mounounougui : Attend.

Sarkin dogarai ya dakata.
Le chef des gardes attend un peu.

Mununugi : Zuma wannan akwai ɗan sauran ta ?

Mounounougui : Y-a-t-il un peu de ce miel-là ?

Nagudu : I ; akwai sauranta biyamaradi

Nagoudou : Oui, il en reste mon prince.

Mununugi : To ku je tare, ka biyo mini da zummuwan nan in gani.

Mounounougui : Bon allez-y ensemble ; tu m'apportes le restant de ce miel

Turaki *: (Ya ce ma Nagudu)* Tashi ku tahi !

Touraki : (Il parle à Nagoudou) Allez-y !

Nagudu ya je don ya kawo zumuwar.
Nagoudou va chez lui pour prendre le reste du miel

Turaki : Sarkin dogarai, in tari ya yi ka ɗebe mishi kai !

Touraki : Chef des gardes, s'il oppose la moindre résistance, tranche-lui la tête sans hésiter

Sarkin dogarai : An gama !

Chef des gardes : A vos ordres !

Turaki ya fiddo sauran fadawa daga wajen da su Liman suke.

Touraki fait séparer les autres notables des inculpés

Turaki : Da kai, da kai, da kai ; ku taso ku komo nan. Wannan wurin ɣan mutuwa ne ; ku bar su can su jera sun kashe kansu.

Touraki : Toi, toi et toi, venez par ici. Là-bas c'est le couloir de la mort. Laissez-les s'entretuer.

Suka taso. Sai Malam Bala ya rage. Shi ma aka ce ya taso.
Tous s'exécutent sauf malam Bala. Touraki le fait aussi quitter les inculpés.

Turaki: Kai ma taso, bar musu wannan wurin. (Turaki ya koma kan su Ladan) Kai tsohon Liman da kai tsohon Ladan…

Touraki : Toi également reviens par ici (Touraki se tourne vers L'Imam et ses co-accusés)
Toi ex-Imam et toi ex- Muezzin…

Suka ɗan matsa kusan Sarki. Sai sarkin ya kore su.
Ils s'approchent un peu plus proche du roi. Celui-ci les repousse.

Sarki : Ku matsa can ! Munafukan banza !

Le roi : Dégagez ! Bande d'hypocrites !

Masu jiran shari'a *: (Suka ja baya suna*) : Allah ba ka nasara

Les inculpés :(Ils reculent en disant) : Gloire à votre majesté !

Sarki : Jakuɗa daga nan kusa na !

Le ro : Eloigne-toi de moi !

Ladan: Allah ya ba ka nasara! Allah ya ba ka nasara!

Le Muezzin : Gloire à toi ! Gloire à toi !

Anan nan sai ga sarkin dogarai, ya shigo da Leƙa kogo da Nagudu sun shigo.
En ce moment le chef des gardes fait son entrée ; il est accompagné de Leka-kogo et de Nagoudou.

Nagudu : Biyamaradi… (*Ya ce yayin da yake aje zummuwar)*

Nagoudou : Mon prince … ! (Il dit en déposant le miel)

Sarkin dogarai : Ranka ya daɗe ; ga leƙa kogo da idon wani.

Chef des gardes : Votre majesté, voici Leka – kogo !

Leƙa-kogo-da idon wani ya durƙusa ya gaida sarki.
Leka-kogo se prosterne pour saluer le roi.

Turaki : Kai ne Leƙa-kogo-da idon wani ?

Touraki : C'est toi Leka-kogo ?

Leƙa-kogo-da idon wani : E ni ne. (*Ya ɗan ja baya*)

Leƙa-kogo : *Oui, c'est moi.* (*Il recule un peu*)

Turaki : A'a, matsa nan inda zan riƙa ganin ka.

Touraki : Non approche-toi ici pour que je puisse bien te voir.

Leƙa-kogo-ya matsa kusa ga Turaki.
Leka-kogo s'approche de Touraki.

Turaki : Kai ne Leƙa-kogo-da - idon wani.

Touraki : C'est toi Leƙa –kogo ?

Leƙa-kogo : Ni ne Leƙa-kogo-da - idon wani.

Leƙa-kogo C'est bien moi Leka-kogo.

Turaki: To ba Leƙa-kogo-da idon wani kake ba…Kana ji na?

Touraki : Je me moque de comment tu t'appelles, tu m'entends ?

Wani bafade : Assha !

Un notable : Désolé !

Leƙa-kogo : Na'am.

Leƙa-kogo Oui

Turaki: To ko Leƙa-kogo-da idon kakarka kake; yau a fada kake gaban sarki.

Touraki : Ecoute-moi bien. Meme si tu regardes les trous dans les arbres avec les yeux de ta grand aujourd'hui tu es à la cour devant le roi !

Leƙa-kogo : Tuba nake !

Leƙa-kogo Je demande pardon !

Turaki : …Ka shurare abin da za a gaya ma.

Touraki : Ecoute bien ce qu'on va te dire.

Mununugi: (Ya nuna Nagudu) Leƙa-kogo-da - idon wani, ka san wancan?

Mounounougui : Leka kogo, est-ce qu tu reconnais cet homme ?

Sarki : Ka faɗi gaskiya !

Le roi : Dis la vérité !

Leƙa-kogo: I, na san shi!

Leƙa-kogo Oui, je le reconnais

Sarki : Tambayar ka nike ! Kai, munafukin banza, ka faɗi gaskiya ! Idan ka yi ƙarya, ina sa a cire maka kai! Duk abinda ya tambaye ka, ka gaya mishi. Da ka ɓoye mini wani abu… Munafuki, kwananka ya ƙare!

Le roi : Espèce d'hypocrite, dis la vérité. Si jamais tu mens je te ferai trancher la tête ! Réponds à toutes les questions posées. Dès que tu caches quelque chose ; espèce d'hypocrite, je te ferai tuer.

Leƙa-kogo : Tuba nike !

Leƙa-kogo Je présente mes excuses !

Mununugi : Mi ke tsakaninku ?

Mounounougui : Qu'est-ce qu'il y a entre vous ?

Leƙa-kogo : (*Yana nuna Nagudu*) Wanga ko ?

Leƙa-kogo : (Il pointe du doigt Nagoudou) Celui-là, n'et ce pas ?

Mununugi : E.

Mounounougui : oui

Leƙa-kogo : Saye da sayarwa.

Leƙa-kogo Le commerce.

Mununugi : Kamar tami ?

Mounounougui : De quelle sorte ?

Leƙa-kogo : Ta zumuwa !

Leƙa-kogo Commerce du miel !

Mununugi : Kai ka saida masa zumuwa ta shekaranjiya ?

Mounounougui : C'est donc toi qui lui as vendu du miel avant-hier ?

Leƙa-kogo : I, ni na saida mai ita. Ba ta isa saidawa ba ma ! Ya matsa min, ya ce in ɗauko mishi. Na ce mai wallahi, ba ta yi ba. To, don shina saye wajena kullum sai na ɗauko mishi ita haka nan, yar kaɗance ma.

Leƙa-kogo : Oui, c'est moi qui le lui ai vendu ! Le miel n'était même pas prêt pour la consommation. C'était parce qu'il avait insisté. Mais comme c'est mon client régulier, je le lui ai amené en état. C'était d'ailleurs une petite quantité.

Mununugi : Ita zumuwar nan da ka ɗebo, ka ɗanɗana ko ba ka ɗanɗana ba ?

Mounounougui : As-tu gouté au miel au moment du prélèvement ?

Leƙa-kogo : Kai ! Mu, wajenmu ba mu maida ta abinci ba ! Mu abun banza muka maida ta.

Leƙa-kogo Non nous ne considérons pas le miel comme aliment ! Pour nous ce n'est pas un produit de valeur !

Mununugi: To a ina ka ɗebo ta?

Mounounougui : Bien, oú est-ce que tu l'as extrait ?

Leƙa-kogo : Inda na saba ɗebo ta. Cikin wani kon icce.

Leƙa-kogo Là où j'ai l'habitude de l'extraire. Dans un trou de tronc d'arbre.

Mununugi : Cikin wani kogon icce… kogon icce ?

Mounounougui : Dans un trou de tronc d'arbre… trou de tronc d'arbre ?

Leƙa-kogo : E !

Leƙa-kogo Oui !

Mununugi : Ka san wurin ?

Mounounougui : Te souviens-tu de l'endroit ?

Leƙa-kogo: Sosai! Ita abin da mutun ka yi kullum!

Leƙa-kogo Bien sûr que oui ! C'est mon travail au quotidien !

Mununugi : Ranka ya daɗe, a gama Leƙa-kogo-da-idon wani, da Dogari. Su je wurin kogon iccen nan, su leƙa. Kai, su sa wuta ! Kuma su zo, su ba ni labari.

Mounounougui : Votre majesté, envoyez le chef des gardes avec Leka-kogo pour vérifier le trou oú le miel a été prélevé. Y mettre du feu si nécessaire et après qu'ils reviennent me rendre compte.

Turaki : (*Cikin mamaki*) Wuta ?

Touraki : (Etonné) Le feu ?

Sarki : Sarkin dogarai !

Le roi : Chef des gardes !

Sarkin dogarai : (*Ya matsa kusan sarki ya ce*) Allah ya ba ka nasara !

Chef des gardes : (Il s'approche du roi pour lui dire) Votre majesté !

Sarki : Sa shi gaba, ku tafi inda zai gwada ma. Ka sa wuta. Amma, in ya waiwaya baya, ka cire mishi kai! Ni na ce! Kuma, in ka sa wuta, duk abin da ya fito, ko aljani ne, ka kawo mini shi nan!

Le roi : Suis-le pour qu'il te conduise là où il a récolté le miel. Et tu y mets le feu. Mais s'il t'oppose la moindre résistance, tranches lui la tête. Telles sont mes instructions. Après y avoir mis le feu, tout ce qui y sort, même si c'est un esprit, amenez-le-moi ici !

Sarkin dogarai: An yi an gama! *(Ya fita tare da Leƙa-kogo da idon wani)*

Chef des gardes : A vos ordres ! (Il sort accompagné de Leka-kogo).

Turaki : Hum *! (Yana mamakin yadda kogo yake iya samu alakƙa da abin da ke ciki.)*

Touraki : Hum ! (Perplexe car ne voyant pas de relation entre la mort de l'étranger et la place où la récolte du miel a eu lieu)

Mununugi : Turaki !

Mounounougui : Touraki !

Turaki : Ina jin ka !

Touraki : Je t'écoute !

Mununugi : Gidan wannan, ba a rasa mage, ko ?

Mounounougui : Est- ce qu'on peut trouver un chant dans cette maison ?

Turaki: Kwarai ko! Ai mussoshin da suke gidan nan… Har ka mance? (*Ya ci gaba*) Ibili ! Ibili ! (Don Allah zo ka taimaka !)

Touraki : Bien sûr ! Les chats qu'il y a dans cette maison… Tu as déjà oublié ? Ibili ! Ibili ! (Au nom d'Allah viens nous aider)

Ibili : Na'am !

Ibili : Oui !

Mununugi : A ba shi zumar ya je ya ba mage !

Mounounougui : Donne-lui le miel pour qu'il le fasse boire à un chat !

Turaki: Ba shi, ga ya can!

Touraki : Donne-le-lui, c'est ça là-bas !

Ibili : An gama, Yanzu !

Ibili : Ça sera fait, tout de suite !

Turaki : Ka je, ka ba mage !

Touraki : Va donner ça à boire à un chat !

Sarki: Sai an samo min wanda ya kashe mutumen nan!

Le roi : Il faut qu'on trouve l'assassin de cet homme !

Turaki : Sarki ya ce, sai an samo mai wanda ya kashe mutumen nan !

Touraki : Le roi dit qu'il faut qu'on retrouve l'assassin de cet homme !

Sarki : (*Ya nuna Mununugi da malaman*) In ba a samo shi ba, da Ladan da Liman da kai …

Le roi : (Montrant du doigt Mounounougui et les marabouts) Et si jamais on ne le retrouve pas, toi le Muezzin toi l'Imam et toi Mounounougui vous serez tous tués…

Turak i: … da kai Nagudu!

Touraki : … Et toi aussi Nagoudou !

Liman : Muna neman alforma !

L'Imam : Nous sollicitons votre grâce !

Sarki: Ba wata alfarma! Yanka ku zan sa a yi! Da ma…

Le roi : Il n'y a aucune grâce ! Je vous ferais décapiter. D'ailleurs…

Turaki : Allah ya ba ka nasara, cikin ikonka, har Mununugi ma ! A kashe har Mununugi da ke iya zama Sarki.

Touraki : Votre Majesté, avec votre permission, faites tuer Mounounougui également ! Il doit être tué car il peut prétendre au trône dans le futur.

Sarki : Hal Mununugi, ba ni barin shi. Ni za a ma shegantaka ? In yi doka a tada don rishin kunya !

Le roi : Y compris Mounounougui, il ne sera pas épargné. Je n'accepte pas qu'on se moque de moi en ne respectant pas mes décisions !

Ibili ya dawo da bayani.
Ibili revient après avoir donné le miel au chat et voulait parler.

Ibili : Allah ya ba ka nasara !

Ibili : Votre Majesté !

Turaki : *(Ya dubi wajen waɗanda ake zargi)* Kuna cin amanar ƙasa, kuna cutar jama'a !

Touraki : (Il se tourne vers les accusés) Vous avez trahi le royaume ! Vous avez trahi la confiance du peuple !

Liman da Ladan da Nagudu sai makarkata suke yi.

L'Imam, le Muezzin et Nagoudou tremblent de peur.

Mununugi: Kowa hankalinku ya kwanta!

Mounounougui: Calmez vous tous!

Ibili: Allah ya ba ka nasara, da na ba mage wannan zumuwa, na zuba mata, ta sha sau ɗaya; ta ƙara, ga na uku, wallahi ko harbawa ba ta yi ba!

Ibili : Votre majesté, quand j'ai donné le miel au chat, il a bu une fois, une deuxième fois à la troisième fois, il est tombé raide mort !

Turaki : Azzalumin banza, munafuki, lalatacce ! Allah ya ba ka nasara wannan ai shegantaka ce ! Yaya za a ce mini zumuwa ta kasha mutum ? Alhali kuwa, zumuwa, a nan gidan a hura, kai har a tuwo sa zuma mukai!

Touraki : Traitre, hypocrite, voyou ! Votre Majesté, c'est de la foutaise. Sinon comment penser que le miel puisse tuer quelqu'un ? C'est la tradition de cette maison de mettre du miel dans le foura et même dans le touwo !

Ibili : Wallahi !

Ibili : En tout cas !

Turaki : Kai kanka Mununugi, tun kana ƙarami kake shan zumuwa a nan gidan. Zumuwa ta taɓa kasha mutum ; ranka ya daɗe ?

Touraki : Toi-même, Mounounougui, tu prenais du miel durant ton enfance dans cette maison. Le miel n'a jamais tué quelqu'un, votre Majesté !

Sarki : Na'am

Le roi : Effectivement !

Mununugi : Turaki, cikin zumuwa, ai akwai zumuwa !

Mounounougui : Touraki, la qualité du miel peut être affectée

Turaki : Don Allah, haƙura Mununugi ! Kar ka zi mini wannan zancen !

Touraki : S'il te plait Mounounougui laisse tomber ton insinuation

Mununugi : Ga Gaskiya nan ta fara hutowa !

Mounounougui : La lumière commence à jaillir !

Turaki : Zumuwa ta taɓa kashewa ?

Touraki : Le miel a-t-il tué une fois quelqu'un ?

Mununugi : Liman !

Mounounougui : L'Imam !

Liman : Mu dai, ba mu taɓa gani ba !

L'Imam En tout nous n'avons jamais vu cela !

Turaki: Zumuwa a nan gidan, wuni ake ana ta shan ta!

Touraki : Dans cette maison nous consommons le miel en longueur de journée !

Mununugi : Zumuwa, ai iri-iri ce !

Mounounougui : Il y a plusieurs types de miel !

Shigowar sarkin dogarai ɗauke da gawar baƙin maciji ta katse wannan mahawarar. L''entrée du chef des gardes avec le cadavre d'un grand serpent interrompt cette discussion.

Sarkin dogarai : Allah ya ba ka nasara. Ga abinda na iske !

Chef des gardes : Votre Majesté, voici ce que trouvé !

Turaki : Aje shi ! Aje shi ! Koma wurinka! Bar shi nan! Koma wurinka !

Touraki : Dépose-le ! Dépose-le ! Retourne à ta place ! Laisse-le-là ! Retourne à ta place !

Mununugi: To, ranka ya daɗe, ta ƙare!

Mounounougui : Bon Votre Majesté c'est fini !

Turaki : Yaya, ta ƙare ?

Touraki : Comment c'est fini ?

Sarkin dogarai : Da munka tafi…

Chef des gardes : Quand on est parti…

Turaki : Na'am !

Touraki : Oui !

Sarkin dogarai : … tare da Leƙa-kogo….

Chef des gardes : … avec Leka-kogo….

Turaki : Na'am !

Touraki : Oui !

Sarkin dogarai : munka tafi wajen kogo…

Chef des gardes : On est allé au niveau du trou dans le tronc de l'arbre…

Turaki : Na'am !

Touraki : Oui !

Sarkin dogarai : Na sa aka saka hakukuwa cikin kogo… aka kawo wuta aka ƙuga … hayaƙi ya turnuƙe…

Chef des gardes : J'ai fait mettre de la paille dans le trou… on ɣ a mis du feu… la fumée a rempli le trou …

Turaki : Na'am !

Touraki : Oui !

Sarkin dogarai : Can sai munka ga zul ! Muka ga zul ! Leƙa-kogo yana cewa sarkin dogarai gare ka ! Sai da na zan namiji !

Chef des gardes : Après quelque temps, quelque chose sort du trou. Leka kogo a crié pour me dire de faire attention. Mais j'ai pu garder mon sang froid.

Leƙa kogo : Namiji ne sosai ! Haka, aka yi !

Leƙa-kogo : Il est vraiment courageux ! Il a dit la vérité !

Sarkin dogarai : Da ƙyar, ranka ya daɗe ! Ya goce nan, in bi shi! Sa'annan na hidda babarbarata, na cire mishi kai.

Chef des gardes : Avec beaucoup de peine Votre Majesté ! Le serpent a couru mais je l'ai suivi avec mon sabre et je lui ai tranché la tête !

Leƙa kogo: Haka aka yi!

Leƙa kogo : C'est la vérité !

Sarkin dogarai : Ku diba ku ga rigata, duk jini ne ! Ranka ya daɗe, ga shi nan!

Chef des gardes : Regardez mon boubou taché de sang. Votre majesté, voici le serpent tué (Il montre le cadavre du serpent).

Leƙa kogo : Ranka ya daɗe, Sarkin dogarai, namiji ne ! Ya yi ƙoƙari !

Leƙa-kogo : Votre majesté, le chef des gardes est un brave homme ! Il a été à la hauteur !

Turaki : (Cikin rishi gamsuwa) Uhum ! Uhum ! Ba ƙiyawa na yi ba, Sarkin dogarai, ka yi mazakunta ! Amma, Allah ya ba ka nasara, maciji ai ƙwai yake sha ba zumuwa ba. Me ya kai maciji cikin zumuwa ? Mu, a sanin da muka ce maciji ƙwai yake sha ! Bai shan zumuwa !

Touraki : (Non convaincu) Uhum ! Uhum ! Je n'en disconviens pas, le chef des gardes tu as été brave ! Mais Votre Majesté, le serpent boit des œufs et non pas du miel ! Qu'est-ce qu'un serpent fait avec du miel ? A ma connaissance les serpents prennent des œufs mais ne boivent pas du miel !

Sarki : Kaƙa za a ce min wannan macijin da ke cikin rame, kuma a ce shi ya kashe shi ?

Le roi : Comment peut-on me dire que ce serpent, qui était dans le trou, est responsable de la mort cet homme ?

Mununugi : Ranka ya daɗe, ina zuwa !

Mounounougui : Votre Majesté, laissez-moi conclure !

Turaki : Lumfasawa !

Touraki : Que votre volonté soit faite !

Mununugi: Wannan ba wani abu da ya kasha shi in ba wannan maciji ba, Ranka ya daɗe! Na yarda maciji ƙwai yake sha !

Mounounougui : C'est bien ce serpent qui est responsable de sa mort, Votre Majesté ! Et je suis d'accord que le serpent mange des œufs !

Liman : Gaskiya ne !

L'Imam : C'est la vérité !

Turaki : Kwai yake sha !

Touraki : En effet le serpent mange des œufs et non pas du miel !

Mununugi : Amma macijin da ke cikin kogon ice inda ke da zumuwa, in ya yi tsartuwa ai ka san ko tsartuwar maciji dafi gare ta ko !

Mounounougui : Mais un serpent qui se trouve dans le trou d'un arbre où se trouve du miel peut cracher du venin dans le miel !

Liman : Gaskiya ne !

L'Imam : C'est la vérité.

Mununugi : Tsartuwar nan mai dafi, sai ta shiga cikin zumuwar !

Mounounougui : C'est le venin du serpent qui a contaminé le !

Liman : Gaskiya ne !

L'Imam : C'est la vérité !

Mununugi: To sai Allah ya sa shi wannan Leƙa kogo bai ɗanɗana ba.

Mounounougui : Par la grâce d'Allah, Leka Kogo n'a pas goûté au miel.

Fadawa : Na'am !

Les notables : C'est vraisemblable !

Mununugi: Wannan wanda ya saida bai ɗanɗana ba. Iyalanshi ma ba su sha. Sai Allah ya kawo wanda kwananshi ya ƙare, wannan baƙon shi ya sha zumuwa, sai ya mutu !

Mounounougui : Celui qui a vendu le miel ne l'a pas gouté. Sa famille non plus. Le destin a fait que l'étranger est le seul à avoir bu le miel et il en est mort !

Liman : Gaskiya ne !

L'Imam : Ça c'est vrai !

Mununugi: Ka ji abun da ya kashe mutumen wannan! Ba laifin Liman ba ne, ba na Ladan ba ne ba ko laifin…

Mounounougui : C'est ce qui a causé la mort de cet homme ! Ce n'est ni la faute Del 'Imam ni celle du Muezzin, ce n'est non plus la faute de …

Leƙa kogo : Ni ma ba laifina ba ne ! Ban sani ba, da ba na ɗauko ta ba !

Leƙa-kogo : Moi non plus, ce n'est pas ma faute ! Si je le savais, je ne l'aurais pas pris !

Mununugi : Inda lokacin nan Leƙa kogo ya ɗanɗana zumuwar nan, da tashi ta ƙare !

Mounounougui : Si Leka kogo avait goûté à ce miel il en serait mort !

Leƙa kogo : Wallahi, ba cikin na sani ba, na ɗauko !

Leƙa-kogo : Je vous le jure, c'est par ignorance que je l'ai pris.

Mununugi:(*Ya nuna gawar baƙo*) Ga mai ƙararen kwana ! Ta ƙare kanshi! To Ranka ya daɗe ka ji yanda aka yi!

Mounounougui : (Montrant le cadavre) Voici la victime du destin ! Votre Majesté, vous venez de connaitre la vérité !

Turaki : Uhum ! Uhum ! Uhum !

Touraki : Uhum ! Uhum Uhum !

Sarki : Mununugi, lalle ka yi ilimin shara'a !

Le roi : Mounounougui, tu as vraiment étudié le droit !

Fadawa : Ƙwarai ko !

Les notables : Sa Majesté dit la vérité !

Sarki: Kuma, Allah ya yi maka albarka!

Le roi : Qu'Allah te bénisse !

Fadawa : Amin ! Amin !

Les notables : Amen ! Amen!

Sarki: In ba don ka ba, da da Ladan da Liman da wannan mutumen, da duk kwanakansu sun ƙare!

Le roi : Sans toi l'Imam et le Muezzin ainsi que tous les autres auraient été exécutés.

Turaki: Har shikanshi! *(Koda yake bai samu yadda yake so ba, sai da ya nuna ɓacin ransa.)*

Touraki : Y compris lui-même ! (*Mécontent de la tournure des choses, il exprime son indignation.)*

Mununugi : (*Don ya gwada Turaki*) Ranka ya daɗe, amma dai na ga, Turaki bai yarda ba da wannan shari'ar. In bai yarda ba, ga sauran zumuwar, to sai ya lasa!

Mounounougui : (Pour tester Touraki qui semble non convaincu par le jugement) Sa Majesté, j'ai compris que Touraki n'est pas d'accord avec ce jugement. Dans ce cas, fait lui goûter le reste du miel !

Turaki : Uhum, Mununugi ni fa na san da ma, a gidan nan naku, ba so na ba kake ! Ka ga aikin nan da nake yi wa rafaninka ne ba ka so, wallahi sai in huta, in dangana !

Touraki : Uhum, Mounounougui je sais que tu ne m'aimes pas ! Ecoute si tu ne veux plus que je continue à travailler à côté de ton oncle je peux me résigner à quitter la cour !

Mununugi : (Cikin tsokana) Gani na yi ba ka amince ba da shari'ar !

Mounounougui : (Avec ironie) J'ai compris que tu n'es pas d'accord avec le jugement !

Turaki : (*Ya ɗauki sauran zumuwar yayin da yake magana*) Yaya za ka ɗauko mini zumuwa, abinda ta kashe mutum ? Ana faɗi kace in sha ta kasha ni! Ba ka ƙauna ta ko? To sai in bar gidanku. Ɗauki kayanka !

Touraki : Comment veux-tu que je boive le miel qui a tué un homme ? Tu veux me le faire boire pour me tuer aussi, n'est-ce pas ? Reprends ton miel sinon je quitte cette cour

Mununugi : Fadawa, ko akwai mai taɓawa ?

Mounounougui : Chers notables, est-ce qu'il y a quelqu'un qui désire le gouter ?

Fadawa : A'a ! A'a !

Les notables : Non ! Non !

Turaki : Liman !

Touraki : Imam !

Liman : Na'am.

L'Imam : Oui.

Turaki : Da kai Ladan…

Touraki : Et toi Ladan…

Ladan : Na'am.

Le Muezzin : Oui.

Turaki : Shari'ar yaron nan, gaskiya ne ! Ni ma na bi, na yarda !

Touraki : Le jugement du jeune homme est juste ! Je l'accepte comme tout le monde.

Liman: To, madalla!

L'Imam: D'accord, c'est bien!

Sarki: Abinda nake tambayar ku…

Le roi : Ce que je veux de vous …

Turaki: Sarki ya ce abinda yake tambayar ku…

Touraki : Le roi dit ce qu'il veut de vous…

Sarki : Daga yau …

Le roi : A partir d'aujourd'hui…

Turaki : Ya ce daga yau…

Touraki : Il dit qu'à partir d'aujourd'hui…

Sarki : Kowa ya sa ɗanshi makaranta !

Le roi : Que chacun inscrive son fils à l'école !

Turaki : Kowa ya sa ɗanshi makaranta !

Touraki : Que chacun inscrive son fils à l'école !

Fadawa : Gaskiya !

Les notables : C'est juste !

Sarki : Karatu, kowane iri ne ya na da amfani.

Le roi : Le savoir, quel qu'il soit, est utile.

Turaki : Kowane iri ne Sarki yace abin nema ne.

Touraki : Quel que soit le savoir, le roi dit qu'il faut le chercher.

Liman : Sosai !

L'Imam : C'est juste !

Sarki : Ko ya zamanto na nasara ne, ko ya zamanto na hammadiyya ne, in yaro bai yi ba wannan ya yi wannan. Ko kuma ya yi biyun.

Le roi : Envoyez vos enfants soit à l'école moderne du blanc ou à celle traditionnelle Coranique. Que l'enfant fasse l'un ou l'autre, ou toutes les deux à la fois.

Turaki: Ka ji ko Liman?

Touraki : As-tu entendu Imam ?

Liman : Na'am.

L'Imam : Oui.

Turaki : Sarki ya ce ya wakilta ka, duk yaron garin nan in sun je sun yi karatun lakkwal sun dawo…

Touraki : Le roi dit que tous les enfants de la cité, une fois revenus de l'école…

Liman : Na'am.

L'Imam : D'accord.

Turaki : Ka tattara su ka kai su makarantarka, ka koya musu karatun Allah kuma !

Touraki : Tu les rassembles et tu leur apprends le savoir islamique également !

Liman : Na'am.

L'Imam : D'accord.

Turaki : Su rinka yin duka biyun.

Touraki : Qu'ils fassent les deux en même temps.

Liman : Gaskiya ne !

L'Imam : C'est juste !

Sark i: Wanda bai yi haka ba, na gamu da shi! (*Ya nuna Mununugi*) In ba don shi ba, Ladan da yau kun ƙare!

Le roi : Celui qui ne le fait pas, me rencontrera sur son chemin ! (Il montre Mounounougui) Sans lui, aujourd'hui, Ladan et les autres auraient été tous tués !

Turaki : Mununugi.

Touraki : Mounounougui.

Mununugi : Na'am.

Mounounougui : Oui.

Nagudu : A maka adu'a.

Nagoudou : Faisons une invocation pour toi.

Turaki : Matsa can su yi maka fatiya.

Touraki : Approche-toi d'eux pour qu'ils te fassent une invocation

Nagudu: Allah shi yi maka Albarka. Mun gode ma !

Nagoudou : Qu'Allah te bénisse ! Nous te remercions !

Fadawa kowa na ta yin tashi addu'ar Allah ya yi albarka. Saura na cewa amin. Les notables se mettent à invoquer Allah pour qu'il bénisse le jeune intellectuel

.

Turaki : Wannan ai shi ne mai kyau !

Touraki : Ça, c'est vraiment bien !

Nagudu : Mun gode ma, Allah ya ja kwananka ! Ai, Mununugi ya yi aiki.

Nagoudou : Nous te remercions. Puisse Allah te donner une longue vie ! Vraiment Mounounougui a été efficace.

Turaki : Ka ji ko, Liman.

Touraki : As-tu bien entendu, Imam ?

Liman : Na'am.

L'Imam : Oui !

Turaki : Sarki ya ce, ko yanzu likafanin bayan Allah nan a kanka.

Touraki : Le roi dit que la charge du linceul du défunt t'incombe.

Liman : Na ɗauka.

L'Imam : Je m'en charge.

Sarki : Zuwa za mu yi gaba ɗaya, a yi mushi sutura.

Le roi : Nous irons tous ensemble à ses obsèques.

Liman : Na'am.

L'Imam : Oui.

Turaki : Sarki ya ce da kanshi, shi ma zuwa ya kai.

Touraki : Le roi dit que lui aussi sera à l'enterrement

Liman: Na'am, na'am; na ɗauka!

L'Imam : D'accord, d'accord, je m'en charge !

Turaki : A yi niyya a je a binne bawan Allah nan. Amma kada ku mance….

Touraki : Dépêchons-nous pour enterrer ce pauvre homme. Mais n'oubliez pas….

Nagudu : *(Ya nuna gawar maciji)* Wannan kin shi ma ai ba abin bari ba ne.

Nagoudou : (Il montre le cadavre du serpent) Même le cadavre du serpent doit être enterrer.

Turaki : Ah ! Yo maciji ai da ma maciji abin kashewa ne ! Kada a mance, a nemi ilimi. Ka ga yanzu ilimi ya hudda ka daga cikin wannan haraka ; da an sa Sarki ya yi kaɓɓa.

Touraki : Ah, oui ! Le destin du serpent c'est d'être tué ! N'oubliez pas de chercher le savoir. Comme vous venez de le voir, c'est la savoir qui nous a sauvé.

Fadawa : Na'am.

Les notables : C'est entendu.

Turaki: Da ya yi ɓanna.

Touraki : Il allait commettre l'irréparable !

Fadawa : Gaskiya ne !

Les notables : Ça, c'est vrai !

Turaki: Da mun yi ɓannar shari'a gaba ɗaya! A ƙarshe da kai, da kai Liman da kai Nagudu, a gama da ɗansa Mununugi da kai kanka, kai zumuwa da baka tsira ba!

Touraki : Nous étions sur le point de rendre un mauvais jugement qui aurait couté la vie à L'Imam, le Muezzin, Mounounougui, toi Nagoudou et meme le vendeur du miel.

Leƙa kogo: Tuba nake! Tuba nake!

Leƙa-kogo Je présente des excuses ! Je présente des excuses !

Sarki : (Ya nuna Leƙa kogo) Kai !

Le roi : (*Pointant du doigt Leka-kogo*) Kai !

Turaki : Sarki ya ce …

Touraki : Le roi dit…

Sarki: Ka ɗauki wannan macijin ka gina rame ka binne shi. Ita ma wagga zumuwa ka gin rame ka binne ta.

Le roi : Prends ce serpent et creuses un trou pour l'y enterrer. Le miel là également il faut le verser dans un trou à fermer.

Turaki : Kuma !

Touraki : Encore !

Leƙa kogo : Na'am

Leƙa kogo D'accord!

Turaki: Zan ja hankalinka bisa abu guda da sunan sarki.

Touraki : Je vais aussi, au nom du roi, attirer ton attention sur une chose.

Leƙa kogo : Na'am, na'am !

Leƙa-kogo D'accord ! D'accord !

Turaki : Ba zumuwa ba kake saidawa ; kai, duk mai talla, in ma ya je ya ɗauko ne ; kan ku je ku sai da wa yan uwa jama'a su ci, ku nemi wata dabba a gidanku, ku ba ta ta ci. In ta wuni ta kwan, in ka ga ba ta mutu ba, ke nan abin yana da lafiya. Ana iyi saidawa jama'a. wannan yana ɗaya daga cikin tsaron lafiyar kanku ne.

Touraki : Je ne m'adresse pas uniquement aux vendeurs du miel. Tous ceux qui vendent des produits de cueillette, avant d'aller les vendre à la population, cherchez un animal pour le lui donner à manger. S'il passe une journée et une nuit sans aucun mauvais signe, en ce moment vous pouvez commencer à vendre les produits. Cela fait partie de la prévention et de la préservation de la santé des populations.

Sarki: Kada in ƙara jin irin wannan kaɓɓa fa!

Le roi : Que plus jamais une telle gaffe ne se reproduise !

Leƙa-kogo : Na'am.

Leƙa-kogo D'accord.

Turaki : Ku tashi a yi niyya !

Touraki : Levons-nous et allons procéder à l'enterrement !

Suka tashi gaba ɗayan su. Sun ɗauki gawar, suna tahe, suna yin hailala.

Ils se lèvent tous ensemble. Ils prennent le cadavre en scandant le témoignage de la foi en Allah.

Fadawa : La'ilaha illallah ! La'ilaha illallah !

Les notables : Il n'y a de Dieu qu'Allah ! Il n'y a de Dieu qu'Allah !

Suka fita da gawar.
Ils sortent avec le cadavre.

Karshe/Fin.

Note biographique

Hamza Abdoul Aziz est né le 01 01 1980 à Tiguizéfen Rouafi/ Abala, Tillabéri (Niger). Doctorant en Linguistique et Science du Langage à l'Ecole Doctorale des Lettres, Arts et Sciences de l'Homme et de la Société à l'Université Abdou Moumouni de Niamey, il est professeur d'enseignement au Ministère des enseignements secondaires du Niger. Hamza Abdoul Aziz a pour centre d'intérêt la langue Hausa et y travaille pour la spécialisation.